[2/28, 6:40 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

In dedication to

Maimuna A A Rano

1 & 2

Karar kiran wayar da tajine yasa ta ajjiye yankan albasar da takeyi da sauri ta karasa kusa da telephone din cikin kitchen din hannunta Na rawa ta dauka husky voice dinsa taji asanyaye coffee ! Ya ajjiye wayar ta saki numfashi tana murmushi khaleel ta ambata a ciki ciki I like ur style ta girgixa kanta yana matukar birgeta tana son dabi'unsa da tsarinsa da sauri ta hada masa tai hanyar bangarensu daga nesa ta hango haisam yana daga karfen nan Na training ta yi tsaki ta kauda kai ta kwankwasa dakin shiru ta bude dakin kamshin air freshner ya daki hancinta ta karewa dakin kallo dayake a tsare kamar ba na namiji ba ta ajjiye coffee din akan center table din da ke kusa da ita tana niyyar juyawa taji motsin fitowarsa daga toilet da sauri ta waiwayo idonsu sukayi karo da juna gabanta ya fadi yana sanye da farin towel iya qugunsa jikinsa ruwane alamun daga wanka ya fito gashin kirjinsa ya kwanta hade da ruwan da bai gama tsanewa ba kyakykyawan matashi ne me hasken fata da jin dadi hade da kwanciyar hankali yana da saje me hada da gashin baki Wanda mafi akasari irinshi ustaxai suke bari a fuskokinsu yana da idanuwa dara dara masu haske da dogon hanci daya karawa fuskarsa Kyau da sauri ta kauda kanta daga kallon da take masa a kunyace ta juya tana kokarin fita daga dakin dim.... Ta bige da center table din da ta ajjiye coffee din achhhhhh !!! Ta fada hade da sunkuyawa ta dafe knee dinta ya dago dara daran idonsa ya kalleta ya kauda kai yana kokarin tube towel din daga kugunsa da sauri ta fice daga dakin shi kuma tashi matsalar kenan ta yarfe hannuwa duk da haka gwara shi akan wancen pepper din ta wuce tana jin dadin ganin Sa dan yau kwata kwata basu hadu ba da sauri ta karasa kitchen din ta hada dinner ta wuce dakinta tayi wanka ta janyo rigarka iya kasan gwiwa ash color tasa ribbon ta daure gashinta ta dauki karamar post ta fito daga dakin nata tayi bangaren momy tana xaune a kujera idonta dauke da glass tana danna computer tayi sallama duk da ba daidai tayi ta ba umma xan tafi sai Na dawo umma tadago kai hade da sakin fuska jenniper kin gama kenan eh umma Na gama ta fada kanta a duke OK to sai kin dawo ki gaishe min da mamanta ki xata ji umma ta mike tabar dakin. Da sauri ta fito daga harabar wajan ta nufo hanyar da xata fita daga gidan turus tayi da ta hango haisam xaune a kujera daga shi sai gajeran wando hannunsa rike da robar swan yana sha xuciyarta cikin tsoro ta nufo wajan tana addu,ar Allah yasa su wanye Ify jikinta Na rawa taxo gab da shi kallon arxiki bata samu daga gareshi ba ruwan daya kurba ya furxar dashi cikin huci har sai da ruwan ya dan taba kafarta sannu yaya haisam ! Ta fada muryarta ta Na rawa bai amsaba dama Sam bata Sa ran amsawar ta saba da sauri ta bude gate ta fice daga gidan kadan kenan daga cikin irin kiyayyar da yake nuna mata dan kawai addininsu ba daya ba tana matukar shan wahalarsa

da axabtarwa bata da yadda xatai xamanta a gidan tana yinshine kawai dan mahaifiyar ta amma axabar haisam ta isa tasa tabar musu gidansu tana tafe cikin nutsuwa karar hon taji gabanta ya fadi yauma rage mata hanya xaiyi ya wuce ta kadan ya tsaya da motar ta karaso nuni yai mata da idonsa khaleel ta ambata a xuciyarta ta bude motar ta shiga ya ja motar karatun qur'anin da yakeji ya cigaba take Jennifer ta tsinci kanta cikin wani irin yanayi tsoro da firgici hade da faduwar gaba sukai mata yawa gefe guda Na cikin xuciyarta Na jin dadin sautin fitar karatun duk da batasan me ake fada ba gumi ya rufeta ta ko ina ta dan jingina da kujerar motar hade da fadin oh my God ! Ta lumshe ido tana sauraran kira,ar cikin nutsuwa dai dai kofar gidansu inda mamanta take sai da abinci ya sauketa da sauri mamanta ta nufo su ya kashe mota yana murmushi oga khaleel Momy ta fada Ikcin data karaso Maman David ya fada oga ya gida yasu Hajiya suna nan kalau Maman David haka akeso mun gode sosai d dawainiya Allah ya saka tafa cikin gurbatacciyar hausar ta ta budewa Jennifer motar ta fito ngd yaya khaleel kai ya daga yaja motar daughter ta rungume Jennifer da hankalinta Na kan motar khaleel har sai da ya bace mata da gani tayi ajiyar xuciya mom ta fada tana shagwabe fuska ta dan xaro ido Ify Jennifer mom nayi missing dinki ta janyota jikinta nima haka yata tai mata kiss a goshi God bless u my daughter shiga cikin brothers dinki na jiranki tun daxu da sauri ta karasa oyoyo Jennifer wani kakkaura baki yana da hanci da katon baki ya fada yana murmushi oyoyo my bro Johnson ya rungumeta sannan ya saketa ta kallesa ina adebola da Joseph ?? Sun tafi church adduar Allah ya kawo mana son in law da wuri ta kai masa duka a shagwabe sai Na fadawa papa tayi hanyar dakin tana dire dire tana xuwa ta fada jikin shi papa kaga Johnson ko ?? Me yayi yafada yana dariya wai cewa yayi adebola da Joseph sun tafi yimin adduar kusami son in law murmushi yayi to sorry daughter zan hukunta shi tunda ya tabamin ke yawwa Daddy Na dai dai lokacin da mama ta shigo shagwabar me kikeyi ta xauna kusa da ita Jennifer ta Sa kanta a cinyar mama tana bata Ibr dariya tayi amin Allah ya kawoshi adduar dana keyi miki kullum duk Wanda xakiso kiyi soyayya da yarenmu Wanda yake addininmu daya xaki fi samun kwanciyar hankali da nutsuwa kada ki kula Wanda kikasan bamu da alaka dashi Na addini ko Na yare suka karasa maganar David da ya shigo dakin Jennifer da papa suka kwashewa da dariya mama sbd yawan wannan waaxin naki David ma ya haddace shi ya kalli Jennifer yana harararta dagamin cinyata ta tureshi oh ! Mama ta mike baxaku balla niba itama Jennifer ta mike nima zan tafi papa ta sunkuyo ya mata kiss God bless u my daughter emen ma dad suka jero da mama hannunta rike Dana David alleh miki albarka jannifer ina Johnson ya fita shagon askinsa ta fito ta tadda gurin sai da abincin mama a cike da mutane sardiq ta hango shida abokinsa hamza wayanda tsofaffin customers ne ta danyi murmushi sannunku da sauri da sauri hamza ya amsa da yawwa Jennifer kwana 2 kin buya shiru tai masa dan bata son yawan mgn ya dago kai hamza kenan akwai mgn da surutu hade da yawan tmby Maman David ina son Na tambayeki wani abu wai Jennifer kuwa Yar kice ?? Ranta bace ta dago kai me yasa kai min wannan tmbyr ?? Kwata kwata bakuyi kama da ita ba asalima Jennifer tafi kama da Hausa Fulani hamza !!! Cikin tsawa Maman David ta dakatar dashi Jennifer yata ce ta cikina kana son sawa yata wani tunani ne nadaban sorry Maman David ya fada hade da mikewa ya ajjiye kudin ya fice ta janyoni jikinta sorry daughter ke yata ce ta cikina kada hakan ya birkita miki tunani babu abinda Allah baya nuna ikonsa ciki kuwa harda banbanta kamanni murmushi Jennifer tayi inda sabo wannan mgnr ba sabuwa bace awajanta dan tun tana yarinya kawayenta suke fada mata da mutanen gari kada kidamu mama nasan ikon Allah akan komai tai mata kiss a goshi

hade da yimata adduar da tasaba yi mata kullum Na tafi mom ta wuce dai dai lokacin da ake kiran sallah magruba ta lumshe ido tana jin sautin fitar kiran salah tana jin dadinsa a kunnanta ta wuce ta masallacin tana kallon suna alwala abin yana bata shaawa tayi gaba xuciyarta asarke gab da xata shiga g.r.a gabanta ya fadi yau kuma wanne kalan rashin mutunci haisam xai mata ????

*BY UMMEEY*
[2/28, 6:40 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

In dedication to

Maimuna A A Rano

3 & 4

Jikinta a sanyaye ta shiga cikin unguwar tana tafe tana hardewa xuciyarta Na bugawa a hnkl har ta karaso gidan wayam taga kofar gidan ta kwankwasa garba me gadi ya bude mata ta shige tana kallon bangaren su yaya khaleel ajiyar xuciyata tayi yau Na tsalleke cin mutuncin yaya haisam kai tsaye dakinta ta nufa ta baje a gadonta tana maida numfashi tunani masu yawa sukai mata cunkus da sauri ta mike ta kunna glof din dakin haske ya kauraye ko ina ta je jikin mudubi ta kurawa kanta ido meyasa bata kama da danginta ? Ta saki ribbon din da ta daure gashinta ya sauka gadan bayanta ta karewa kanta kallo fara ce tasss doguwa bata da jiki tana heart face da dara dara idanu hade da dankaramin baki ta sunkuyar da kanta tabbas kalarta kalan Fulani koma larabawa ne tana da matukar Kyau Sam batayi kama da sauran yan uwanta su David ko mamanta da papanta ba tayi kama dasu koda kuwa ta kafafuwa ko hannaye da yatsu ikon Allah ! Ta girgixa kanta tabbas ikon shine ta danyi tsaki bata son irin wannan tunanin dan yana jefa xuciyar ta cikin rudu da tashin hnkl jikinta asanyaye ta mike ta fice daga dakin tai bangaren hajja kakarsu yaya khaleel kai tsaye ta shige falon ta sameta xaune tana karanta jaridar leadership tayi sallama duk da ba dai dai tayi ta ba hajja ta amsa mata cikin sakin fuska Jennifer naam hajja kin dawo daga wajan Maman taki ko ?? Kanta a sunkuye ta amsa da eh Na dawo hajja tana nan Ify ? Lafiyan ta lau mashaa Allah suka kurawa

t.v kallo sbd Ibrin da ya ja hankalinsu Na shaye shayen kayan maye da matasa sukeyi hajja taja tsaki Allah ka shirya mana xuri'a amin Jennifer ta fada hade da mikewa kina da wata matsala ne Jennifer ?? A a hajja Na xo Na dubaki ne in da akwai aiki a a babu aiki to zan wuce OK Jennifer gwara kije ki huta ai kina kokari ma sannu ta wuce hajja tabi bayanta da kallo cikin tausayawa yarinyar tana matukar bata tausayi girgixa kai tayi Allah ya shiryeki in dai xaki shiryu

Tana fitowa daga dakin kai tsaye bangaren Rubayya ta shiga ta tana kwance akan gado tana kallon Indian series ( qubul hai ) Rubayya ta dago kai cikin fara'a Jennifer ya akayi ?? Na dawo daga skul ban sameki ba Momy tace min kinje gaishe da Maman David eh cen naje ban dade da dawowa ba ayya ! Kayane gasu nan nayi kwalema nasan xasuyi miki tunda kusan size dinmu daya da murna ta kalli akwatunan data nuna mata wow ! Nagode Anty ruby taxaro ido Anty kuma Jennifer ?? Haba dai dan Allah karki kuma Sa'anni muke fa ngd sosai ruby bako mai kin cancanci fiye da hakan ma ta tashi ta kinkimi akwatin xuciyarta cike da jin dadin kayan ta fice tana mata gdy kai tsaye dakinta ta nufa Taiwa kayan daidaya atamfofine tsala tsala da shaddoji da lesa lesai manya dukkansu kusan sabbine dan babu alamar hudu ko uku ta dafe kai tana murmushi mutanen gidan nan suna da karamci da girmama dan adam duk da bata dade ba dan bata wuce wata 1 da satittika tana musu aiki ba mutun dayane yake masifar gallaxa mata haisam tayi ajiyar xuciya ya tsaneta sbd banbancin addini ta kwanta bacci me karfi ya sureta cike da mafarkai marasa kan gado

7:30 am

Ta tashi ta shiga kitchen ta hau shiryawa yan gidan break fast kasancewar ranar weekend ne har 9:00am bataji motsin kowa ba ta gama ta Jere musu a dinnig ta hau gyra falon ta kade kura ta share ko ina ta kunna turaren wuta ta wuce bangarenta tayi wanka ta dakko kayan da rubby ta bata atamfa brown me adon yellow orange ta saka tayi tayi ta daura Dan kwalin ta kasa haka ta dauko kana nan gyaluluwan da rubby ta hada mata dashi iya wuya tayi rolling din kanta dashi da sauri ta kalli mudubi taja baya a tsorace sak bafulatana ko balarabiya da sauri ta kauda kanta ta dauko break fast dinta ta fara ci hnklinta kwance ta gama ta hau gado ta mike 11:45am ta mike dan taje ta kwashe kayan da suka ci abinci ta kuma Dora lunch ta fito ba kowa a falon ta kwashe ta wanke kayan ta gyara dining area din ta koma kitchen ta hau Dora girki tanayi tana wakarta ta kiristoci tana gyada kai kee !! Cikin tsawa a tsorace ta kame dan tagane muryarsa baki da hnkl ?? Bakisan nan gidan masoya annabi bane kike mana wakar shashanci ?? Ta sunkuyar da kai tana nadamar manta a inda take har tayi wakar ?? Munafuka kafura yaja tsaki me karfi cike da tsana ki dafamin abu me ruwa ruwa yanxun nan sannan idan kika kikai min kazanta ko kisa min wani abun Na cutarwa Allah ya isa ! Wllh I hate u ta runtse idonta don dai bani da yadda xanyi soon xakibar gidan nan kije wajan makiya Allah irinku kiyi musu bautawa gunki fuuuu ya wuce ta tabe baki cike da Jin haushin kalamansa xata jure duk wani cin kashi har lokacin daxata cimma babban burinta da sauri da sauri ta hada masa daga nesa ta hangoshi yana training din daya saba yi kullum ta wuce dakinshi ta ajjiye ta fice da sauri ta

cigaba da aikinta ta gama ta shige dakinta tana tunanin bakaken maganganun da haisam ya kwaba mata ....wllh I hate u soon xakibar gidan nan kije wajan makiya Allah irinku ........ta furxar da huce itakam ba makiyiya Allah bace hawaye ya sauko mata har sai yaushe xata fara kyakykyawar rayuwa Mara tunani barkatai ?? Yaushene xuciyarta xata daina saka mata wasu muhimman abubuwa datake ganin sai ta cinma su xata samu sauki ?? Hayaniya taji me dan karfi na fitowa daga babban falon gidan anyi baki kenan da sauri ta mike dan ita ke kula da baki ta fice tana tafiya a nutse xuciyarta kuma ajagule hayaniyar su haisam da rubby da wasu muryoyi da ba ta sansu ba kai tsaye falon ta shiga hade da sallama suka amsa mata falon cike yake da duk mutanen gidan da ganinsu suna cikin jin dadi dan dukkansu dariya suke bakin fuska biyu ta gani mace budurwa da saurayi dukkansu kyawawa gefe guda ga trolley masu masifar Kyau da gani matafiya ne dan budurwar tayi kama da rubby sannunku da xuwa yauwa yanmata saurayin ya fada yana murmushi hade da kura mata manyan idanuwansa itakam budurwa ta kalleta sama da kasa ta kauda kanta Momy bakuwa mukayi ne ?? Hajja ta ce a a bayan tafiyarka anyi auren zainab wannan itace new maid dinmu ayya meye sunanki yanmata kanta a sunkuye tana murmushi ta amsa da Jennifer.. wat?? Ya fada hade da dan xare ido kina nufin ba bahaushiya bace ?? Eh uban tambaya inji hajja no hajja ba dake nakeba ki rufemin tsohon bakinki mom da mmk haisam yayi tsaki kafura suka kwaso mana dayar macen tace gsky ba tsari ya isa zahra inji rubby kowa yayi me fish sheshi saurayin ya dan girgixa kai sorry Jennifer nyc to meet u ya miko mata hannu ta miko hannu itama da sauri haisam ya bige hannun namijin haba mahboob meye haka ?? Jennifer ta sauke hannunta cike da jin kunya zahra ta kwashe da dariya Momy ta kalleta cikin tausaya wa jennifer jeki jera abinci a dining naga time yayi ga kuma su Zahara da mahboob sun dawo da sauri ta mike ta nufi bangaren kitchen din tana kallon khaleel ko kallon inda take baiyiba asalima danne dannen wayarsa kawai yakeyi tana jiyo hayaniyarsu suna hirarsu cike da annushuwa da jin dadi ta gama jerawa ta karaso Momy gashi cen nagama yawwa jennifer sannu kinji Allah ya saka amin haba mom inji haisam ya kike mata addua bayan kinsan wacece ita haisam .. Haisam.. Haisam mom ya fada tom jikin jennifer a sanyaye xata bar falon taji muryar mahboob Jennifer baxakiyi lunch din damu bane ?? Har abada indai da haisam ne no mahboob nayi nawa tun daxu OK toh shikenan mungode da dawainiya suka hada ido yakashe mata ido daya cikin gwaninta irin salon mayaudaran samari ta juya ta cigaba da tafiya kai kuma taka matsalar kenan itakam bakuwace yanxu take sanin yan gidan wayannan sababbin awajanta ko dame sukaxo ??

BY UMMEEY

[2/28, 6:40 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIPER✍✍✍

5&6

Daki tashige xuciyarta babu dadi tarasa kwakwkwaran dalili guda daya da haisam ya tsaneta sbd bambancin addini ?? Mutun dubu nawa yake mu'amala dasu Wanda ba addininsu daya ba ta lumshe ido abin nashi cin fuskane girgixa kai tayi shiya Sani baza ta bari bacin ranshi ya dinga mata tasiri aranta ba dan tana da babban buri akan yan gidan nan banda iyayenta su kadaine mutanen da tayi sabo dasu sosai har ta fara fahimtar abubuwa masu yawa akan abinda takeson Sani ta kishingida da filow din kan gadonta tana tuna farkon ganinta da yaya khaleel ta danyi murmushi ranta yayi tass mai mutunci da daraja dan Adam batare da kyama ko nuna kokon usili ba wannan dalilin ne yasa yake matukar birgeta hade da kyawawan halayensa kwankwasa kofa taji da sauri ta tashi daga kishingidar da tayi hade da bada umarnin a shigo ya shigo hannunsa daya a aljihu daya akansa yana shafawa fuskarshi dauke Da murmushi ya janyo stool ya xauna jenniper ta bishi da kallon mmk ya kalleta kina mmk ko ? Kai ta girgixa masa kada kiyi karya dan karya bata dace da kyakykyawar surarki ba mamakin ta ya karo duk da bayau aka saba ce mata me Kyau ba ya kalli gefen dakinta banyi karya ba tabbas mmk kike na gani na awajanki xakiyi tunanin me naxoyi me yakawoni ? Ya kalleta kina son jin amsar mmkin da kikeyi ko ? Kada ki damu danni mutun ne me damuwa da damuwar wasu musamman wayanda suke kusa dani wannan ta wadatar ki cire duk wani tunani da xai kawo miki xiyara naga kamar kina cikin damuwa ? Ta girgixa kai tana satar kallon gefan fuskarshi kinyi lunch ? Nayi ta bashi amsa kai tsaye anya kuwa ya fada yana kallon lips dinta fuskarshi dauke da murmushi wannan lips din beyi kama da Wanda yaci abinci ba tayi dariya tana mmkin xakewa irin tashi to shikenan nasan kyawawa basa karya sunana mahboob kamar yanda Momy ta fada kikaji kuma nima danta ne haisam shi yake bina ina so idan ba damuwa mu zama frnds ta xaro ido tana mishi wani kallo a tsorace ko ban miki bane ? Ya fada yana kallanta ranshi a dan bace ta girgixa kai tana ajiyar xuciya a a ta fada muryarta na sarkewa kin amince ?,ya kuma tambayrta kai ta daga masa yayi murmushi hade da mikewa daga kan stool din ngd kawata jenniper anjima zanxo muyi hira yanxu xanje na kwanta sbd na gaji ngd yaya mahboob mention not ya fada daidai lokacin daya bude kofar dakin ya fita tare da jifan ta da wani shu'umin kallo ta sauke numfashi tana mmkin hirarsu da shi yana magana atsare kamar wani marubucin novel yanayin maganarshi tmkr ta cikakkun mayaudara anya kuwa ? Koma mayaudarine tabbas yana da kirki ya kuma son darajar mutane duk da kasancewar ta Krista ya amince da alaka da ita me karfi mamanta tasha fada mata ana abota da mutane nagari mace ko namiji hade dasa kyakykyawan niyya sukam dabi'arsa kawance babban abune Wanda yake da matukar muhimmanci kafi karfina mahboob ta fada cikin kwarin gwiwa hade da Sa kanta akan filow dinta

4:00pm ta shiga kitchen dan ta Dora abincin dare telephone din kitchen tai kara ta karasa kusa da ita ta amsa muryar yaya khaleel taji ki kawomin tee da sauri ta amsa da toh ya ajjiye wayar

ta Dora masa tee din cikin mintuna kalilan ta gama ta nufi hanyar dakin nasa waya ta taddashi yanayi xuciyarta taji takusa bugawa dan ta fahimci da mace yake wayar oh sorry ki dinga fahimtar abu kafin ki yanke hukunci meyasa kikeson dagawa kanki hnkl ? Na fada miki babu wani abu uxiri xaki dinga min ayyuka sun min yawa plx plx plx share hawayanki zanxo kd kada kidamu kinsan bana son kuka ko ?? Ki daina waiwayo yayi yana kallonta da hnklinta Sam baya jikinta mmk ta bashi yanda yaga jikinta a matukar sanyaye murmushi yayi hade da cije lips dinshi na kasa jenniper ya dai shiru sai da ya bugi center table ta waiwayo da sauri Ify ya fada yana mata wani irin kallo da sauri tace Ify ta juyo xatabar dakin jenniper ya kira sunanta da muryarsa me dadin ji har cikin ranta taji dadin futar sunan ta daga bakinsa kina da wata damuwa ne yaxuba mata kyawawan manyan idanunsa fuskarsa adake bayabo ba fallasa ta kalleshi kwarjinin shi yasa ta saurin sunkuyar da kai tuni jikinta ya fara rawa babu komai yaya khaleel OK ya fada ya juya mata baya yana danne dannen wayarsa ta kwabe fuska tana kallon kyakykyawan bayansa ta juya ta fita tarasa me yasa takejin tsoron yaya khaleel meyasa yake mata kwarjini meyasa take matukar jin kunyarsa ?? Dawa yake waya ?? Mecece dinshi ? Kirjinta yai mata xafi ranta ya baci idonta ya cicciko da hawaye meyasa take jin haushi haka ?? Meya ke shirin faruwa da ita baxai yiyu ba ta fada afili mahboob ta gani agabanta kamar an jefoshi ya akayi ne my frnd ta kalleshi hade da saurin yin yake no no babu komai nafada miki kyawawa basa karya yaken takuma yi tana son barin wajan dan tana bukatar hutawa tayi tunanin magance matsalar da takeson xama damuwarta oh yanxuma tunanin kike yi ? Da sauri ta kalleshi batason lokacin da ta shagwabe fuska kamar xatayi kuka a a abokina ina son xuwa na karasa girkin Dana Dora ya kalleta yana kanne ido daya muje in taya kawata girki da sauri ta girgixa kai a a abokina wannan kyakykyawan jikin naka da yasaba da Hutu bana son ya kusanci wahala ta girki ya rike haba ina bazan bari kawata tayi girki ita kadai ba kada muyi jayayya oya kibiyo ni yayi gaba tabi bayanshi xuciyarta a cunkushe Sam bataso ya takura mata lokacin da takeson tunanin mafitar bakon al'amarin da yaxo mata binshi tayi xungui xungui har cikin kitchen din

BY UMMEEY

[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍ JENNIFER✍✍✍

7&8

Binshi tayi abaya ranta bai soba ya shige kitchen din ya waiwayo ya kalleta dame zan fara ya tmby ta ta kada kai da abinda ka iya tamayar masa da amsa asanyaye dan bata San mexata sashi ba ya wuce ciki yana bude buden food flas oh jennifer ya fada yana yarfe hannu kin gama

kenan kai ta girgixama Sa da saura dan yanxu zan dorawa Momy kunun gyada ya khaleel kuma zan mishi spinach nd egg stew ya kalleta yana murmushi ban iya ba dama wayace ka iya ta fada tana Dora tukunya akan gass hk ya koma gefe suna hira tana aikinta amsa masa hirar kawai take xuciyarta babu dadi a hk har tagama gaf da sallar mgrub ya kalli agogon hannunsa me Kyau da tsada lokacin sallah yayi dam!! .. taji kirjinta ya buga xan tafi amma ki tabbata yau dake xamuyi dinner ta kalleshi ya Matso kusa da ita kada kiyi tare xamuyi da family kai ta daga masa tana jinjina xakewa irin tasa ya wuce tai ajiyar xuciya ta shiga tunanin da takeson yi tun daxu yahanata me yake shirin faruwa da itane ?? Ya akayi takejin haushin wayar daya khaleel yayi ?? Tasa hannunta a kai hade da fadin oh! Meyasa zanjefa kaina cikin halin kaka nikayi ?? Wacce take kokarin Sa kanta yanxu ma takasa sbd tsoro da kuma firgicin halin daxata tsinci kanta jikinta a sanyaye ta debo abincin ta Jere a dining ta wuce daki tai wanka ta canza kaya ta kurawa wayarta kallo tana kallon number yaya khaleel kwankwasa kofa akayi ya shigo kamshin turarensa me sanyi tashaka ta kalli fuskarsa Wanda shima idonshi akanta Jennifer me ya sameki ? Da sauri ta saki fuska bakomai yaya mahboob OK ki taso muje ina?? ta fada wajan cin abinci ya fada hade da juya wa yana kokarin bude kofa itakam bata tabajin in da akai hakaba tayaya xata je taci abinci da iyayen gidanta ?? Bin bayashi tayi da kallo babu inda xata ta kwasowa kanta takaici da bacin rai tai kwanciyarta karar wayarta taji tana dubawa sunan Momy ta gani jikinta na rawa ta daga Jennifer jiranki mukeyi da mmk ta amsa da ina xuwa momy mikewa tayi da sauri ta nufi dining area ganinsu tayi xaune a falon dukansu babu yaya haisam ko yana ina ?? Oho mishi bakaramin dadi tajiba narashin ganinsa a kunyace ta karaso Momy gani ta dago kai momyn tana kallonta mahboob yace adinka cin abinci dake kuma ya fada miki amma mukaji ki shiru da mmk ta kalli mahboob takasa cewa komai dadi da farin ciki sosai ya kamata Momy ki kyaleta nayi fushi da ita mahboob yafada yana kallon agogon hannunsa 20 mints muna jiranta Momy tayi murmushi mahboob aboki yana fushi da kawarshi ne ? Momy fushin kadan ne ba dayawa ba yafada yana hararar Jennifer da mmk ya hana ta cewa uffan Rubayya ta kallesu da mmk itama ya mahboob wace kawarka ? To yarsa ido yacewa rubayyan Jennifer ce new frnd dina rubayyan tayi dariya ina tayaka murna kayi dacen kawa ina tayaki murna bakiyi dacen abokiba sukayi dariya mahboob ya harari ruby cikin daure fuska da kina kusa dani sai na mauje miki baki ta shagwabe fuska Momy ba gaskiya na fada ba ? Hajjo da tana gefe batayi mgn ba tasa baki gsky kika fada Rubayya inba Jennifer dinba waxaiyi kawance da mahboob Rubayya tasa hannu ta rufe baki tana dariya kasa kasa ba ruwana hajjo dama bakinku daya mahboob ya fada yana kallon hajjo da tafara xuba abinci kai kasani hajjo ta bashi amsa da sauri Jennifer ta amsa cokalin hajjo ta xuba mata abincin sannan ta xubawa kowa nashi tunda taxo wajan zahra bata kalle inda take ba shikuwa ya khaleel hnklinshi nakan waya yana danne danne babu wanda yasaran tofa nashi zancen sbd sanin hali ta xauna tana cin abincin suna taba hira jefi jefi idon mahboob akanta kunya duk ta kamata takasa sakewa xuciyarta tai mata dadi babu abinda bata sakawa axuciyarta ba itakadai tasan dalilin jin dadinta wayar zahara tai kara ta daga murmushi tab a fuskarta wlkslm Anty Jidda tayi wata irin dariya irin ta shakiyanci muna tare dashi ta kalli ya khaleel dayake juya cokali muna dinner nefa OK zan fada mishi ta ajjiye wayar ya khaleel Anty jiddanka tace ta kiraka bk daga waya ba ya kalleta sai kuma yayi murmushi nagani ina sone sai nagama cin abinci zan kirata kin San hirarmu bata karewa gaban Jennifer ya fadi dama yana mgn irin hk ? Kowa yayi mmkin mgnr shi mahboob yace wow ! Khaleel yakamata fa kayi mgn me Kyau akan aurenka da Jidda

yayi murmushi yana kallon mahboob tunanin dana keyi kenan Dana gma shiryawa zan yi kokari ya mike yana kallon wayarsa da sauri Jennifer ta bishi da kallo xuciyarta na mata zafi karaf ya kalleta hade da jifanta da wani kallo Wanda takasa fassarasa kamar na tuhuma ko kuma na ramuwa ya wuce suka bishi da kallon mmk hajjo ta tabe baki miskili kafi mahaukaci ban haushi Wanda yaron kamar aljani hk yake babu me shiga maganar sai in kai kakuma yinta zahra tace hajjo kin sawa ya khaleel ido fa baki na Sa masa ba idoba ja,ira kawai Rubayya tace kwantar da hnklinki hajjo menene na tada jijiyar wuya ko kishi kike ? Zan saba muku fa sukayi dariya dukansu banda Momy da hnklinta ya rabu sbd jin abinda khaleel ya fada mikewa Jennifer tayi cikin wani yanayi zan je na kwanta sai da safe OK Jennifer suka amsa mata dukansu banda zahra da tabita da harara yake Jennifer tayi cikin kwarin gwiwa baxaiyiyu kasami soyayyar kowa ba dolene kasamu masoya da kuma makiya koda bakai musu komai ba ta ta bude tadakinta ta xauna gefen gado hade da cire dankwalinta tana kallon agogo 8:25 ta gani kirr wayarta tayi kara ya khaleel taga sunan Sa kan screen din wayar gaban ta na faduwa ta daga asanyaye taji muryarsa coffee ! Ya kashe ajiya xuciyarta ta mike da sauri ta nufi kitchen ta hada masa ta nufi dakinsa tayi sallama waya yakeyi yana kyalkyalar dariya...... babyna kinsan abinda nakeso ya kuma dariya hade da fadin kada kiyi mmk komai yana canxawa zanzo kd kodan na saki farinciki nasan kinyi missing dina sosai nima nayi dan jiya bacci dake nayi araina.......ya dago kai yna kallon Jennifer da take a tsaye da cup din coffee tayi wuri wuri tana ajiyar numfashi murmushi yayi hade da cije lip dinshi na kasa ya dai Jennifer ?? Ya fada yana daure fuska da sauri ta sunkuyar da kai babu komai ta ajjiye cup din ta juya kinga " yafada ta tsaya hade da waiwayowa idonshi akan waya yana danne danne kina da damuwane yafada cikin ko in kula girgixa kai tayi a a ta wuce ta mmjin tambayar nan tashi

BY UMMEEY

[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

9&10

Daki ta shiga hnklinta atashe akasalance ta xauna akan gado tana mai da numfashi xuciyar ta arikice wannan irin yanayine wannan ?? Ranta tajishi abace hade da damuwa sosai muryar ya mahboob taji yana sallama ta amsa ya shigo idonshi akanta ta kalleshi tana kallon agogo 9:40 ya kalli agogon yana hararta nasani dare yayi sallama xamuyi ya janyo stool ya xauna yana fuskantarta kawata ta amsa da ya mahboob kin taba soyayya ? Da sauri ta kalleshi a a ta bashi amsa tana mmkin tmbyr meyasa ? Ya kuma tmbyr ta ta sunkuyar da kanta tana jujjuya xoben hannunta sbd ban shirya ba dariya yayi me sauti kadan Jennifer soyayya ba,a shirya mata tabe baki tayi dan tafara gjy da tmbyr kurillarsa da Kyau ya fada yana kallon lip din da ta tabe xan bige wannan karamin lip din daake tabemin shi dariya ya ba ta kalleshi bafa ....... Ya daga mata hannu bacci kikeji ko ? To karma ki fara hira xamuyi ta xaro ido tana kwabe fuska nagaji ya

mahboob ya katseta da fadin ki fadamin gsky kin taba soyayya ?? Zanyi ta nan gaba amma banta ba yinta ba tabashi amsa ya mike yana dariya naji amma......toh kyakykyawa kamarki da wuya ya bude kofa sai da safe nima baccin nakeji ya fice ta bi bayanshi da kallo hade da murguda baki ko ina ruwanshi da soyayyar ta ? Wata keso ? Sam bata Sani ba ! Batasan Wanda takeso ba tayaya xatayi soyayya yanxu bayan akwai muhimman abubuwan da sai ta gama cimmusu baxata Sa kanta a soyayyar kowa ba har sai babban burinta ya cika hnklinta ya kwanta mafarkinta ya xama gsk soyayya ta yan gata ce ba irinta wacce Nan gaba kadan batasan ya xata kasance mata ba

7:30 ta shiga kitchen ta shirya break fast ta Jere su a dining agajiye ta shiga dakinta tayi wanka kafin mutanen gidan su shirya ta kwanta bacci ya kwasheta sbd jiya batayi baccin kirki ba mahboob ya shigo dakin dan kiranta break fast ya ganta tana bacci ya kalli beautiful face dinta cikin tausaya wa yasa hannu ya shafa fuskar ya dade yana kallonta yana tunanin wani abu aransa ya fice daga dakin

12:23 ta farka agigice tana kallon agogo da sauri idonta ya sauka kan food flast din da cup da flast din shayi komai da komai na break fast dinta a ajjiye a sauke numfashi tana tunanin waye da wannan aikin ? Yaune rana ta afarko da ta taba wannan shirmen dolenta tacire duk abinda ke kokarin sata ka kasala da rashin bacci toilet tashiga ta shirya ta fito tayi break fast din agaggauce dan taje ta Dora lunch kafin time ya kure da sauri ta gama ta kwashe kayan ta nufi kitchen ta Dora abincin rana

Yau takama Saturday weekend da yamma ta na kitchen wajan shirya abincin dare ta hango su Rubayya da zahra wajan Malam Mahmud da yake xuwa duk weekend yana koya musu karatun kur,ani hnklinta na kansu sauri takeyi tagama taje wajan da tasaba buya taji karatun nasu dan yana Sa ta nutsuwa da shiga wani yanayi Wanda itaka dai tasan yanayin bayan ta gama ta sanda ta nufi bayan wajan tanajin karatukansu radau tana kuma lekensu jikinta asanyaye damka taji bata wasa ba andamki gashin kanta cikin mugunta muryar Yaya haisam taji munafuka ubanki kike sauraro ?? Wato munafurcine ya kawoki gidan nan ko ?? Koda yake kinajin axabar da Allah ya tanadarwa mushrikai irinku ?? Ke wacce iriyar jahila ce dakikiya arniya kaxamai yan wuta ta fashe da kuka me ciwo bayanxu xakiyi kuka ba har sai lokacin da Allah ya kamaki akan budulce masa da kikayi ya halicceki kiki bauta masa ki bautawa wani bayanshi ya hankadata ta bige da bango ta fadi wanwar akasa kalleni nan ya kwatsa mata tsawa da kyar ta kalli idonsa da ya kankantar dashi sbd masifa natsaneku dakuda addininku ya wullo mata key din dakinshi ki gyaramin daki kifito da kayan ciki masu datti ki wanke kaxama datti kaxanta yayi tsaki ya wuce da kyar ta mike hannunta tafe da wajan da ta bige sbd xogin

daya ke mata hango ya khaleel tayi xaune akan kujera hannunshi rike da waya yana danne danne akan idonshi komai ya faru hawaye ne masu xafi da daci suke subo mata hk ta mike hannunta rike da kanta ta wuce ta gabanshi bata samu kallon arxiki bare na tausayawa ta shiga dakin ya haisam da yai kaca kaca ta hau gyara taci wuya sbd kayan sawarsa barabaje atsakar dakin ta gyara tass ta wanke toilet ta fidda masu datti ta fito daga dakin tai wajan injin wanki hnklinta atashe ta gabanshi ta wuce yana waya hawaye ya sauko mata duk jarabar ka baxaka dau rayuwa ta ba tana wankin tanajin takaici sosai na cin mutuncin ya haisam

By UMMEEY
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

11&12

Ta gama wankin da sauri ta shanya ta koma daki xuciyarta tunkushe tana kuma mmkin bakin hali irin na haisam tana nan xaune aka kira sallar magrub da sauri ta tashi daga kwanciyar da tayi tana sauraron kiran sallar xuciyarta na kwadai ta mata abubuwa da dama karar wayarta taji jikinta asanyaye ta duba Maman David xuciyarta tayi sanyi kadan ta daga oyoyo mamana oyoyo Jennifer mama ta amsa kina Ify dai ko ? Lfy nake mama ya papana da su David suna nan kalau suntafi skul nayi missing dinku mama ta fada ashagwabe sorry Jennifer muma duk mun damu darashin ki kusa damu ranar Sunday kixo nan gida mutafi Church tare da brothers dinki damm ! Gaban Jennifer ya fadi rabon ta da xuwa Church har ta manta to mama zanxo yawwa kina dai aikin ki akan kari ko ? Eh tafada jikinta duk yai sanyi baki da wata damuwa ko ? Babu mama haka ake so sai xuwa anjima zan xubawa customers abinci Itr yata tayi mata addua takashe wayan wulli Jennifer tayi da wayan ta dafe kanta Sam ! Xuciyarta bata son xuwa Church kishingida tayi tana tuna abubuwa masu yawa da suke damunta takasa fadawa kowa kuma tana tsoron yankewa kanta hukunci asalima tarasa da inda xata fara warware matsalarta amincewarta aiki a gidan nan yana daya daga cikin warwarewar tunkushashshiyar matsalar ta takuma rasa ta ina xata fara mikewa tayi jikinta asanyaye ta fito daga dakinta tayi hanyar kitchen dan yau baxata ci abinci da mutanen gidan nan ba kicibus sukayi da zahra ta zabgawa Jennifer wani kallo na raini cikin isa da izza ta bude baki da kyar kamar bata son maganar kije ki gyaramin daki ta wuce tana rufe hanci Jennifer ta bita da kallo ta dawo baya tai hanyar dakin zahra ta bude kamshi me dadin shaka ya bigi hancinta wannan shine karon farko da ta taba shigowa dakin nata ko ina tsab haka dai ta karkade ta share da wanke toilet ta fesa air freshener ta sauko down stairs a falo ta gansu ita da ya haisam gabanta ya fadi taxo xata wuce atsorace hade da faduwar gaba kee! Taji muryar ya haisam jikinta na rawa ta xo maza da Allah ya fada cikin tsawa ubanwa ya baki ixinin cin abinci damu tayi shiru kanta akasa mgn nake miki ! Da sauri tace ya haisam zahra da take kallo tace na fuskanci ya mahboob yana da feelings

akan yarinyar nan tsaki haisam yaja cikin jin haushi shi ya Sani amma baxa a kara cin abinci da itaba inyaso yabita dakinta suci tare hmm zahra tayi mmkin dayake bani da baya iyajin warinta ta fada tana done hanci wari ?? Jennifer ta maimaita aranta zahran ta waiwayo ta kalli jennifer tun xuwanta gun sai yanxu ta kalleta hnklinta na kan tv da take kallo shishshigin naki yanaso yayi yawa kitsaya iya matsayinki tashi ki bawa mutane guri kazama kawai ya haisam yafada yana jefa mata mugun kallo na kiyayya da tsana da sauri ta mike tayi bangarenta ranta bace abincin daba taciba kenan ta kwana da yunwa da bacin rai

6:00am ta tashi ta gama komai da wuri dan batasan su dinka haduwa da mahboob taga ma tayi wanka ta bar daki ta yi can bayan gida inda babu Wanda xaiyi tunanin xuwanta wajan ta jinkina hade da sakanta jikin ginin wajan tasan tabbas mahboob ya ganta damunta xaiyi da tmbyoyi koma yace taxo suyi break fast itakam yanxu kome xai mata baxata kara xuwa wajan cin abincinsu koda kuwa xata yini da yunwa tana nan zauna har gyangyadi ya kamata abinka ga Wanda baisamu ishashshan bacci ba hk tayi baccin axauna

9:32am ta farka a gigice sbd rana ta daki fuskarta da sauri ta mike tayi dakinta tasa mukulli ta rufe tayi kwanciyarta tasan basu gama break fast dinba tayi baccinta me isarta dan safiya ne kadai time din hutunta duk inda 12:00pm ba ita ba sauran Hutu

Bugun kofar dataji ne yasa ta mike zumbur akuma tsorace ta bude kofar karaf suka hada ido yana murmushi sannu sarkin baccin safe ta daure fuska dan tana son yakiceshi ya shigo dakin daxu ina kika shiga naita nemanki da safe ? Tayi shiru kanta akasa sbd ya tsareta da idanuwa nayi wani aikine OK ya fada zanje unguwa sai yamma xan dawo me kikeso na taho miki dashi ?? Tayi shiru taji dadi sosai ta girgixa kai bana son komai ya bata rai baxaiyiyu ba zanyi fushi muddin kika ki fadamin shirun ta kumayi sbd batason me xatace tana so ba ya juya ya fice ranshi abace tabi bayanshi da kallo tana jin haushin kanta tayi rashin hnkl bai kamata tayiwa Wanda ya damu da ita haka ta shi taje dining ta kwashe kayan da sukaci abinci ta gyara wajan ta Dora na rana telephone tayi ring Momy ta gani ta amsa jennifer in kin gama kixo toh Momy ta amsa aladabce

Sauri tayi ta gama tana adduar Allah yasa ba laifi tayi ba a falo ta taddasu ita dasu Rubayya da zahra suna hira suna kuma kallo kin gama jennifer ? Momy ta tmbyeta tana kallonta eh Momy na gama OK yayi Kyau sannu da aiki Allah yasaka amin Jennifer tafada tana jin dadin adduar Momy xakuje kasuwa ne keda Rubayya yau dadyn su xai dawo xuwa yamma tayi murmushi Allah ya dawo dashi Ify amin Jennifer kije ki shirya to tamike da sauri tayi dakinta a gaggauce ta shirya doguwar riga tasa baka arabiyan gown wacce rubayya ta bata tayi rolling din kanta da gyalen rigar ta fito tsaye ta tadda rubayyan kusa da motarta tana waya gefe taja ta tsaya tana kallon bayanta Jennifer ta lumshe ido Rubayya tana matukar birgeta sbd tana bata darajta dan adam duk kaskancin Sa ta waiwayo tana kallon jennifer fuskarta dauke da murmushi muje ko jennifer ta bude mota tashiga suka fice

3:27pm dai dai suka dawo daga kasuwa gaba dayansu suka fada kitchen sbd 7 dady xai dawo girki sosai akayi kala kala basu gama ba sai wajan 5:00pm da wani abun alokacin hjy uwani me kawowa Momy yan aiki ta kawo yanmata su biyu wayanda xasu yi aiki tare da jennifer dukkansu hausawa ne daki jennifer ta shige tana adduar Allah yasa kada su dinka nuna mata wariyar launin fata wanka ta shiga toilet tayi ta fito tana shafa mai bayan tagama ta xo kitchen ta Debi abincinta ta koma daki ta ci ta xo mayar da plate din kitchen Momy ta kirata falo cikin fara a Jennifer ga mataimaka kin samu jennifer ta kallesu sannunku da xuwa suka bude hkr suna dariya yawwa sannun ina yini ? Suka gaishe ta ta amsa da Ify lau xuwa gobe Jennifer sai ki nuna musu kan aikin yau gidan namune duk muna busy inyaso na raba muku aikin da kowacce xatayi toh Momy ki kaisu dakin kusa dake nan xasu xauna ta mikawa jennifer mukullin dakin ta amsa sannan tace su taso su biyota da jakar kayansu ta kaisu dakin nasu ta nuna musu yadda xasuyi amfani da komai na dakin sannan ta koma kitchen ta gyarashi tsab takwaso girke girken ta Jere a dining ta gyara gidan tasss ko ina ya dau sheki ta kunna turaren wuta ta koma dakinta

7:35pm taji motoci na shigowa gabanta ya fadi dady ya dawo itakam bata sanshi ba sai photon shi kawai take gani taji hayaniya na tashi daga babban falo tasan farin ciki sukeyi da murnar dawowar dadyn nasu oh inama itama rayuwarta irin tasu ce? Da sauri ta kauda tunanin da yake tunxurota

Wajan goma taji tsit jikinta asanyaye ta shigo falon ba kowa yayi kaca kaca ta kwashe kayan wajan ta kai kitchen ta share ko ina nan da nan wajan yai Kyau ta koma kitchen ta gyarashi ring

taji na telephone da mmk ta daga muryar ya khaleel taji kixo ki gyaramin daki taxaro ido cikin Daren nan ina tuni ya kashe waya takalli agogan kitchen din 11 saura

BY *UMMEEEEY*

[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

15%16

Hon yayi me gadi ya bude musu get ya shige gidan sai yanxu ya samu nutsuwa tun haduwarsu da yan fashi shikam haisam xuciyarshi ta tafi kololuwar tunanin ya akayi Jennifer taxo Dubai sata ?? Wacece ita ? Me takeyi a gidansu Sam hankalinshi baya tare dashi bude kofa yusuf yayi ya fito daga motar yana yiwa haisam wani irin kallo kafito mana haisam koda yake kaika Sani inma anan xaka kwana cikin motar ya wuce cikin gida yana mitar halin da haisam ya sashi bin Yusuf din yai da ido yana girgixa kanshi baka San mmkin dana ke cikiba nafika tashin hnklin da kashiga baikai Wanda nashiga ba yanxun nan kwakwalwarshi ta rude yarasa wanne irin tunani xaiyi waya ya janyo daga aljihu ya kira zahra ba ta dade tana ringing ba ta daga muryarta adashe da alama bacci takeyi kiran wayar ya tasheta arikice yake tambayarta ........zahra ina jennifer da mmk ta amsa da bansani ba ya haisam me ya faru ??? No ! No ! Dubomin tana cikin gidan ta mike daga kwamciyar da tayi araxane menene wai ya haisam kafa dagamin hnkl da sauri ya canza voice dayin dariyar yake oh ! Zahra bakomai ina son sata wani aikine tayi ajiyar xuciya hade da yin dariya haba da katashi hankalina ta fito daga dakinta tai bangaren su jennifer a hanya ta ci karo da Sa,a ke xo ta kira ta a ladabce Sa,an taxo hade da sunkuyawa ina jennifer ? BATANAN TUN JIYA kaninta ne ba lfy ok ta katse Sa,an jeki kawai shima haisam din kashe wayar yayi dan yaji amsar da Sa,a ta bawa zahra batanan tun jiya baiji karashen zancen ba gumi me xafi ya rufeshi jikin shi ya fara rawa me ya ke shirin faruwa ?? Meyasa tahana akashe shi ?? Tabbas yasan ya kuntata mata dafe kai yayi arikice yarasa wani irin tunani xaiyi munafuka !! ya fada axuciye Allah ya Toni asirinki ya jingina jikin kujera xuciyarshi na ingaixashi Allah Allah ya keyi gobe tayi ya dawo 9ja yaji dalilin zamanta gidansu

Daren ranar baiyi baccin kirkiba gaba dayanshi arikice yake haka yaje meeting din batare da ya fahimci me aka tattauna ba da kyar ya saita nutsuwarshi ya fahimci kadan suna gama meeting din ya fito da gaggawa yai airport dan ya kagu yaxo gida ya tahumi munafukar yarinyar nan azzaluma macuciya barauniya

10:00pm ya iso 9jaa sai wajan 11 ya isa gida dare yayi haka yaita sintiri da ga bangarensu xuwa cikin gida da kyar bacci ya kwashe shi

Tunda wuri yadda ta saba ta fito dora musu break fast sbd kwananta 3 ba agidan ba tana wajan jinyar David suwaiba ta tarar a kitchen din suka yiwa juna murmushi suka gaisa suna girkin suna hira kwatsam suka ganshi akansu daga shi sai dan gajeran wando dama al,adar mazan kenan yawo da kana nan kaya kowanne irine da sauri ta kalleshi atsorace take gaishe shi ya kura mata ido yarasa tana ina xai fara tambayarta sbd xuciyrshi da take akufule miko min tee ya fada yana huci da sauri ta bude flask ta xubo masa a cup ta mika masa ya kalli tee din yana jujjuyashi ahannunsa ya watso mata shi cikin zafin nama ta goce duk da haka sai da ya samu gefen kafadarta ta kwalla kara sbd xafin da taji ya nuna ta da yatsa sai dai yakasa cewa komai sai girgiza kai kawai yake yakaiwa iska naushi da hannunsa yai tsaki me karfi ya bar wajan da sauri hade da ajjiye cup din hannunshi nesa da kitchen din su ya xauna yana tunanin hanyar da xai bullo mata abinda yabashi mmk dakiyar daya ga tayi cikin gwaninta da yaudara kamar basu hadu da ita a Dubai ba duk yadda akayi yarinyar nan bakar shedaniya ce bai kamata kai tsaye ya damketa ba kamun kazar kuku ya kamata yai mata xaibar wannan a cikinshi cikin lokaci kalilan zai mata mugun kamu binciken wacece ita xai farayi ya alkawarta sai yago dalilin zamanta cikin gidansu

Kuka takeyi sosai suwaiba na bata hkr kiyi hkr Jennifer wayeshi ? Cikin kuka take bata amsa dan gidan nan kanin ya mahboob ranar da aka kawoki ya tafi Dubai dama tuntuni baya kaunata suwaiba dan kawai addininmu ba daya ba ta kuma fashewa da kuka kiyi hkr Jennifer kin San kowanne kalan mutun da halinsa nikaina naga kiyayyarki sosai a kwayar idonsa kuma na fuskamci bashi da tausayi ko imani dan me imani baxaiyi abinda yayi ba bakomai suwaiba komai yana da lokaci addua suwaiba tacigaba dayiwa jennifer tana tofawa a inda ta kone inshaa Allah wajan bai tashiba kiyi hkr ki koma daki daki zan karasa girkin kai jennifer ta girgixa kibari mu karasa tunda kin min addua Allah ya saka miki suwaiba na fuskanci kina da adalci da daraja dan Adam in sha Allah xakiyi albarka arayuwarki dan mamana tana fadamin mutane

masu kyawawan hali da daraja muatane yanuwansu masu adalci da biyayya ga ubangijinsu suna albarka arayuwarsi kin dace dan wannan halin mamana ta fadamin baiwace Wanda sai mai rabo ubangiji yake bashi murmushi suwaiba tayi hade da kura mata ido cikin xuciyarta tana adduar Allah yasa kina da rabon musulunci Jennifer kalanki da nutsuwarki da kamanninki irin namune Allah mai iko tana mamakin kasancewarta cikin wannan halin Allah y shiryaki Jennifer shirin addinin musulunci bayan sun gama suka jeresu a dining sannan suka koma daki sukayi nasu break fast din suna hira jefi Jefi Jennifer na duba konewar da tayi abinda ya bata mmk kokadan koniyar bata tashi ba ta kalli suwaiba tana murmushi suwaiba kinga ikon Allah tafashash shan ruwan xafine fa amma kinga koniyar bata tashi ba suwaiba ta saki fuska baxata tashiba jennifer na miki adduar annabi Ibrahim alaihis salam lokacin da aka jefashi cikin wuta duk irin wutar da ta tabaki kowacce irice in kikai saurin yinta kika tofa ta tofa yanda bata illata annabi Ibrahim alaihis salam babu abinda xatai miki ko da yarone ya kone shiru Jennifer tayi tana tunanin wani abu Wanda babu Wanda yasan menene ciki kuwa har da ni ummee🤔

1:30pm suka gama lunch suka kai musu dining sannan suka dawo daki suwaiba ta wuce toilet tayo alwala ta tada sallah Jennifer na satar kallonta ta fuskanci suwaiba tana da ilmin addini daidai gwargwado sannan tana aiki dashi dan akwai son yin ibada akan lokaci tanayin komai nata anutsu sabanin sauran yan aikin su Sa a da hadiza da ko shiga harkarta basayi tunda suka San wacece ita novel ta janyo na Hausa tana dubawa na suwaiba ne tagane tana son karance karancen litattafan Hausa in dai sungama ayyukamsu ta idar da sallar ta dauko musu nasu abincin Jennifer ta sakko tasa hannu tana kallon suwaiba tai addua sannan ta fara cin nata bayan sun gama ma sai da tayi abin ya birge Jennifer sallamr hadiza sukaji sannunku yanmata masu hadin kai to kuxo masu gida suna nemanmu a babban falo da murmushi suwaiba ta mayar mata da to yanmata marasa hadin kai muna xuwa dariya Jennifer sukayi ita da hadizan sannan ta bar dakin tana mitar wai suwaiba ta fiya mai da kurji ciwo

Gaba dayansu ma aikatan gidan suka taro a babban falo dady da Momy ne a ciki kusa da shi ya khaleel ne hnklinshi akan waya yana danne dannenshi Jennifer tarasa me yake dannowa da kullum baya gajiya tun xuwansu wajan babu wacce ya dago kai ya kalla cen gefe zahra ce rike da Ipad itama tana game Rubayya hnklinta na kan tv sarkin kallon series films

Yayana sunnunku da xuwa daddy ya fada da sauri dukansu suka kalleshi cike da mmkin kiransu

da yayi da yayanshi ya aiki ? Ya tambayesu cikin hadin baki suka amsa da alhamdulillah babu wata damuwa dai ko ya kuma tmbyr su babu damuwa dady to masha Allah na tarakune sbd jibi dukanmu nida iyalina xamuje umara saudiyya kowacce xata koma gidansu ajibin sai mundawo dan 2 weeks kadai xamuyi ma aikatan mu maza su zasu kula da gidan banda Ku mata yaxaro kudi masu yawa yararraba musu sukayi godiya sosai sannan ya sallamesu kowacce acikinsu murna take banda jennifer da take cikin damuwar rabuwa da yan gidan suna fitowa sukai karo da mahboob ya harareta suwaiba tasaki hannunta tai gaba ita kuma ta tsaya tana kallanshi itama ..kinsan fushi nake dake ?? Ya tambayeta tayi dariya a a Yaya mahboob bansani ba shiyasa na fda miki dan na fuskanci bakisan ina fushin dakeba xo muje garden hira xamuyi ta xaro ido aikinfa ? Baxa kiyi ba ya bata amsa yana kallonta ta kwabe fuska kar nabar suwaiba shiittt ! Ya katse ta hade da Sa yatsansa daya abakinshi muje aikinta ne itama tabi bayanshi bata soba akan dadduma suka xauna cikin grass idon shi akanta Jennifer menene yake damunki kwana 2 dinnan naga kamar kina cikin damuwa ?? Shiru tayi tana tunanin amsar bashi dan tasansa da bin kokwkwafi hakane David ne bashi da Ify yana fama da sicler idan ta tayar masa hnklinmu na tashi duka sbd muna son yaron rashin Ifyr nasa yana takura masa Ayya! Ya fada cikin tausaya kuyi hkr kuyi masa addua Allah ya bashi Ify amin ta fada jibi xamu tafi umara naso ace tare muka tafi wani daliline me karfi yasa baxa mu tafi tareba amma next in shaa Allah tare xamu tafi murmushi tayi dan tasan dalilin shine kasancewarta Kristan ne hira sosai yai mata cike da tsari kasancewar Sa dan tsara zance ya dauko wayarsa sukayi photo tare kala kala dakyar ya bar ta tashiga gida yna fadin shi baigaji da hirar ba tana shiga cikin gidan taci karo da ya khaleel a tsaye hannuwansa cikin aljihu ya jefa da kallon da ya saba yimata Wanda takasa fassarashi

Saudiyya

Sun sauka Ify kwanansu 3 da xuwa haisam yana masallaci yna dawafi bayan an idar da sallar axahar ya fito dan yaci abinci yana sauka daga lifta karf idonshi ya sauka akanta tana sanye cikin dogowar riga Arabian gown suna tsaye da wata mata fara irin farin 9ja me kiba babbar mace mgn suke tana dariya ta riko hannun matar ta sumbata sukayi hugging din juna sannan tabar wajan da sauri yana tsaye ya kasa mgn mmk sosai da firgici ya kamashi da sauri yabi bayanta kafin ya cimmata tashige cikin mutane bat tabace masa da sauri ya dawo inda yabar daya matar batanan ya bige kanshi hade da fadin oshcc!! Meyake faruwa ne kasa ya dunkule hannunsa yana dukan tafin hannunshi da shi da gudu gudu ya bi wani wajen karaf yaci karo da wata ta hnkdashi hade da fadin baka da hnkl ? Cikin tsawa da sauri hnklinshi ya dawo kanta ya zaro ido yana mata wani irin kallo tayi tsaki tana masa kaskantaccen kallo mahaukaci ne kai ?? Irinkune sakarkaru da kuke tafiya bakwa kallon gabanku mahaukaci kawai tafada tana cigaba da tafiya ta dago yatsanta tana karkada masa nunin gargadi bai farga sai da takusa ficewa da ga masallacin sannan ya furta jennifer !! Akufule yabi bayanta da sauri

By

*UMMEEYY*
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

13&14

Cikin hukuncin Allah cikin kwanaki uku ta warware sbd yanda doctors din asibitin suke kula da ita lallai tasha gata awajan yan gidan tmkr yarsu haka suka maida ita komai na jin dadi sun ajjiye mata xahra ce kawai taxo hospital din sau 1 sukam kullum anan suke yini haka Momy ta kafa ta tsare akan bataso iyayenta suji zancen dan kada hnklinsu ya tashi su dauki matakin rabata da gidan ita kanta Jennifer batai karanbanin tunanin sanar dasu ba dan muddin suka

Sani to dukkan plan dinta ya rushe kulawar da suka nuna mata yasa takara sakankacewa ta kuma dauki damarar duk rintsi tana tare dasu har burinta ya cike suka daine mutanen da tai mu'amala dasu ta kuma yi sabo dasu sabanin iyayenta dan mamanta bata barinta mu'amala da musulmai dan tsoron karta musulunta tunda sunfuskanci Sam addininsu bai damu Jennifern ba

Yau aka salla mota suka dawo gida ta murmure sai rashin karbin jiki shima sai a hnkl xata koma nrml Momy canza mata daki tayi ta dawo da ita bangaren yanmatan gidan Jennifer taji dadin hakan sosai zahra kam taji haushi dan kiri kiri ta nuna bata so hakan ta faru ba da yamma suna babban falon gidan kamar yadda suka saba ya haisam ya shigo hira sukeyi banda Jennifer da tayi shiru tana tunanin wasu abubuwa da ita kadai tasansu ya xauna kusa da Momy ya dan kalli Jennifer yace ya jiki ? Kanta asunkuye cikin jin nauyi da kunya ta amsa da sauki Momy yaufa 12: jirginsu khaleel xai sauka Jidda cike da jin dadi ta mike tana rawa oyoyo my heart yau xai dawo dariya dukansu sukayi haisam yace ke kam kinfiya dauki ko irin Jan class din nan da kuma kunya tai far da ido wa zanjiwa kunya ?? Ya nuna Momy da ido tabbi momyn tawa ta taho da sauri ta rungume Momy momyn ta tallabota tana dariya wai fa kinji Momy ke xanji kunya Murmushi kawai momyn tayi ruby tace ai Anty Jidda bata hada kowa da ya khaleel dinta ba inkaga tana rawar kafa to tana kusa dashi far Jidda tayi da ido sbd shi na musamman ne shiyasa nake rawar jiki akansa kada wata ta kwace min shi haisam yace ba mmk a tafiyar nan tashi yasamu wata girlfriend a can zaro ido tayi hade da bata rai ya haisam xamu bata fa ta shagwabe fuska Momy 😫😫kina jin yaya haisam ko Momy ta jijjiga ta sorry shareshi kin San halinsa dan tsokana haisam yace to shagwabatu da anyi mgn kice Momy 😫 kamar ke kadaice me ita

mikewa Jennifer tayi dan tagaji da jin hirarsu mai bata haushi dakinta sabo ta koma ta kwanta ta rufe kanta da bargo hawaye ya sauko mata

*****************

Tun 11: sukaje airport tarar shi Jennifer ma ta bisu dan yanxu sun maida ita tamkar tasu janta sukeyi sosai ajiki sbd sunji tana muradin addinin musulunci itakam taji dadin wannan mugunta ta xahra tunda gashi ta dalilin haka tana samun kulawa da kuma tausayawa tana ganin ta haka ne babban burinta xai ciki 12:10 jirginsu ya khaleel ya sauka suna tsaye wajan masu jira suka hangoshi hannunsa dauke da jakar shi dayan hannun kuma rike da iphat cikin kasaita da isa yake jefa kafarsa Jennifer na hangoshi gabanta ya fadi yayi Kyau yayi haske ya danyi kiba yana karaso wa Jidda tasa kukan shagwaba ta fada jikinshi yayi murmushi ya dan ture ta kadan hade da rike mata hannu yan uwan ma rungumeshi sukayi suna fadin oyoyo 1 week kawai amma kowa yayi missing dinka bai kula da itaba sai da ya kusa shiga mota ya ganta arakube ya kura mata ido bai San lokacin da yace kinyi rashin Ify ne ?? Turus sukayi gaba dayansu cike da mmkin tambayar da yai mata ganin jikinsu yayi sanyi yasa yace kin koma gefe kin rakube kamar Mara Ify oya Ku shigo mota mutafi nagaji ina son hutawa suka shiga mota dukansu suka bar wajan

*******************

Bayan kwna 2 da dawowarsa daga Singapore suna xaune basu Dade da gama yin breakfast va duk da yaga sauye sauye akan Jennifer bai nuna ya lura da hakan ba sbd miskilanci Jidda sai shishshige masa takeyi duk inda ya xauna tana kusa da shi Jennifer tun tana damuwa har tafa ra hkr ta xuba musu ido yauma tana kusa dashi tace sweeter ina tsaraba oh ! Ya fada na manta ke ! Yacewa Jennifer ta kalleshi ya miko mata key din dakinsa kije ki daukomin wata karamar jaka ta amsa tafice haushin shi duk ya kamata ta dauko ta kawo masa ya ciro wayoyi masu Kyau da tsada iPhone last ta wannan year din ya raba musu suka hau murna dukansu abin mmk ya dauko irinta sak ya mikawa Jennifer sororo sukayi dukansu ita kanta Jennifer mmk abin ya bata ciki kuwa har da Momy Jidda kasa boye kishinta tayi ya xakayi hk khaleel ka hada bamu kyauta da Yar aiki zahra ma mugun kallo tabi Jennifer ta shi ita kanta Momy da Rubayya wani rikitaccen kallo sukewa Jennifer ta sunkuyar da kanta kamar ta fashe da kuka tsawa Jidda tayi masa ganin bashi da niyyar amsa mata tmbyrta me kake nufi !? Ya dago kai hnkl kwance ni kikewa tsawa ? Sbd kin maidani danki ko ? Abinda kikeso xanyi ? Xaki iya hidimta min kamar yadda takemin gyaren daki girkina duk itace kifada min kintaba min daya daga ciki?? cikin jin haushi tace ai biyanta akeyi afusace yace ke kike biyanta abinda naga dama shinakeyi bakuma Wanda ya isa yace min danme idan kina so mushirya kibi tsarina idan kuwa ba haka ba ki kuka da kanki ya mike yabar falon tasa kuka ta mike tana sane ta takwa Jennifer hannu harda murxawa tai sama tana kuka

By

*UMMEEYY*

[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

27&28

Tun xuwanshi saudiyya ya dage da addu'a sosai kullum yana masallaci yana adduar samun falala da kuma rahma awajan ubangiji xuciyar shi tafara haske damuwar dayake ji akan sanin wacece Jennifer ta taragu fiye da da dan da wani irin abu yakeji ya tsaya masa arai kansa ya kulle tunani ma rasa wanne iri xaiyi yanxu kam xuciyarshi tayi tass yasamu kwarin gwiwar da xaiyi binciken asalinta da kuma manufarta na munafuntarsu sai dai tunda yaje basu haduba daya idar da ibadarsa aikin nemanta yake tafiya haryanxu basu haduba

Kwanakin daya kesonyi sun kusa karewa xuciyarshi ta fara taradda din ko shareef al Hussain y samu nasarar kasheta ?? Dam gabanshi ya buga ya salam ! Dukkan mai rai mamacine amma baxaiji dadin mutuwar ta ba yaso ace ta musulunta ta tuba sannan yana son jin Ibrinta dafa kanshi yayi shikam baita ba cin karo da wannan al'amarin ba koda kuwa a films tashi yai ya koma masallaci yai addu'a sosai sai dare ya dawo gida ya shirya kayansa a jaka dan gobe yake son wucewa ranso bai soba  tunaninshi Jennifer bata raye ya kwanta ranshi abace

Washegari ya shirya ya fito ya hau motar daxata kaishi airport ya sauka daga motar ya shiga ciki

Bayan sungama masa komai ya xauna jiran time dan sai 1 jirginsu xai tashi wata mota ya hango mai Kyau sosai ta shigo tai parking ya kalli motar tai masa Kyau a ido ya kauda kansa ya cigaba da kallon shuke shuken da ke wajan dai dai lokacin daya ji sanarwar passengers wayanda suka da wo daga Egypt sun sauka ya sunkuyar da kansa kasa yana dagowa yaga wata mace mai kiba fara irin farin 9ja ya kuma kallonta yana son tunu inda ya santa wata ya hango sanye cikin riga da wando Pakistan ta yafa kyalen kayan akanta bayanta ya hango baiga fuskarba rungume juna sukayi suna dariya kana ganinsu kaga jin dadi da kwanciyar hnkl waiwayor daxatayi gabansa yai mummunan faduwa da sauri ya mike hade dayin Hamdala ya nufo su yana jin dadin sake ganinta kafin ya karaso har ta budewa babbar macen nan mota ta shiga itakuma ta xagayo tana kokarin budewa ta shiga Jennifer ! Ya kira sunanta ta waiwayo sbd yaxo gab da ita ta galla mishi harara tana mishi kallon raini fuskarta cike da tsiwa meyasa kike wasa da hankalina ? Dakata tace mishi baka da hnkl ya xaro ido yana mata kallon mmk ko kana da shi ?? Ta tambayeshi da rainin wayo shiru yayi yakasa bata amsa dan yasan da rainin wayo murmushi tayi ta bude mota kadan kaji ka kuma gani ta fada mota driver yaja ya wuce mmkinsa ya karo me yarinyar nan take nufi da kadan kaji kadan kuma ka gani ?? Tana nufin xata kuma cigaba da wahalar masa da tunani ?? Girgixa kai yayi zaiyi watsi da son sanin ko ita wacece koma metake son yi musu Allah ya fita hk time yayi ya hau jirgi ransa abace

Daki ta shiga ta xauna kusa da suwaiba tana kokarin kishingida suwaiba hnklinta nakan novel tana karantawa hannu Jennifer tasa ta warce buk din da sauri suwaiba ta kalleta tana murmushi dan Allah bani Jennifer in karasa haba a tsurawa buk ido ba'aji ba'a gani karatun novel kawai hmmm baxaki gane bane bakisan dadin da yake cikin karanta novel ba far Jennifer tayi da ido hade da tungura mata buk din gashi nan ki cigaba da aikin kurawa buk ido da sauri suwaiba ta dauka ta dago kai takalli Jennifer gobe Mr coffee xaiyi tafiya dariya Jennifer tayi hade da gyarama xama ya khaleel ba ina xaije xaibi dadi Singapore daxu ina babban falo zan kunna turaren wuta naji suna hirar Jidda tana ta zabga shagwaba Momy tana lallashinta kinsan abin

ban haushi ? Jennifer ta girgixa kai kanshi na kan waya yana danne danne baice cikanki ba abin ban haushi tsaki Jennifer taja su suka Sani suwaiba ta cigaba da mgn nafuskanci khaleel din nan miskiline na karshe ace budurwarka na kukan missing dinka sbd xakayi tafiya ka kasa ce mata komai hmmm tabbijam ina son miskilin namiji amma na Mr coffee yayi yawa ajiyar xuciya Jennifer tayi tana jinjina xancen wayar hannunta ta duba kinga lokaci yayi tashi muje mu fara aiki mikewa suwaiba tayi ta cigaba da mgn duk cikinsu mahboob yafi sauki amma kinga Mr pepper karshe kenan haisam tunda ya dawo dai naga kamar yarage wulakanci Jennifer tai dariya watakil inda yaje ne suka Konya masa daraja dan adam sukayi dariya dukansu suka shiga kitchen dan fara aikin abincin dare

Washegari bayan yan gidan sungama cin abincin rana Jennifer ta fito tana kwashe kayan tana kaisu kitchen dukansu yan gidan suna babban falo kamar ko yaushe suna hirarsu ke ! Taji muryar ya khaleel yana kiranta ta tsaya cak zonan da sauri tai cikin falon ba wanda ya kalleta sai Momy key ya mika mata shiga dakina ki dauko min jakar akwatina ta amshi key din ta fara tafiya taji Momy nace mishi time fa ya kusayi katashi mana tafice dakinsa ta nufa a hargitse ta tadda dakin ta sunkuya ta sunkuci jakar tafito ta taddasu atsaye jikin motocinsu ta ajjiye jakar tana miko masa key din nop ki koma ki daukomin dayar guda biyu juyawa tayi ta koma ta dauko dayar har ya shiga mota shida Jidda suna baya driver na gaba dayar motar kuma Rubayya ce zahra na kusa da ita Momy ta kalli Jennifer ko xaki bisu shiru tayi tana murmushi jeki ki dauko gyalenki kiyi musu rakiya jiknta asanyaye ta je daki ta dauko gyale ta shiga bayan motar da Rubayya take ja suka bi bayan motar su ya khaleel

Bayan sun je airport din Jidda na zuba masa shagwaba ta rike masa hannu har time din da akai kiransu tasa kuka ya tsaya yana kallon fuskarta yasa hannu ya goge hawayen da ke xarya a fuskarta kiyi hkr plx 1 week kawai zanyi zan dawo tarike masa hannu biyun duka zanyi missing dinka sosai a wannan week din sannan tasaki hannun kallon Jennifer yayi ke ! Xo ki dauki jakar nan kibiyo ni da ita turuss gaba dayansu sukayi suna mmk da sauri Jidda tace bari na daukar maka a a ajjiyeta tamiki nauyi ganin ba wasa a fuskarshi yasa ta ajjiye jakar da tai saurin dauka sbd yace na dauka  hannun Jennifer  na rawa ta dauka tabi bayanshi yayin da suka rakata da muguwar harara sunyi tafiya sai da suka xo dai dai wajan da ba dama Jennifer ta shiga ya tsaya yana kallonta murmushin mugunta ya watsa mata da sauri ta sunkuyar da idonta tana son gane fassarar murmushin ke ! Yace mata kina da abinda xakice ?? Tayi shiru tana juya tmbyrshi dan tarasa gane kanta kina da damuwa ne ? Ya kara tmvyrta muryrta na rawa tace bani da abinda xance bani kuma da wata damuwa murmushin mugunta ya kumayi hade da cije lebenshi na kasa ya sunkuya ya dauki jakar da ta ajjiye yai gba tana waiwayo taga duk sun xuba musu ido gabanta ya fadi Takara so kusa dasu dukkansu suka bita da kallon tuhuma mota suka shiga Rubayya na xaune wajan driver zahra na kusa da ita Jidda ta bude baya ta shiga Jennifer ma bayan ta shiga Rubayya taja motar Jennifer Jidda takira sunanta naam ta amsa tana jiran tuhumar daxatai mata menene tsakaninki da khaleel?  shiru tayi tana jinjina tmvyr Rubayya ce tai mgn muryarta asanyaye haba Anty Jidda menene kuwa a tsakaninsu ?? Kintaba ganin wani

abune sabanin yau ? Mgn ake miki kibamu amsa!  zahra ta kwasa mata tsawa Jidda ta kalli Rubayya datake tukin mota bantaba ganin wani abu kuma fatan ganin koma menene in dai akan ya khaleel ne me kuke cewa bayan kunbar kusa damu ? Shiru Jennifer tayi dan tarude tarasa amsar bata inbanda hawaye dake xubar mata a a va kuka nace kiyi ba amsa xakibani tsaki zahra tayi dama munafuki saurin kuka gareshi kin fiya shishshigi kitsaya matsayinki na Yar aiki kibar ganin kinxo gida da manyan matasa samari kyawawa dukkansu bavu sa'anki ke bari kiji gaba dayansu suna da yanmatan da xasu aura koya mahboob din da kike shishshige masa yana da wacca xai aura mufeeda Yar gidan ambassador na India in banda kwadayi ina ke ina xuri'armu ? Kibani amsata malama kar xuciyata ta fashe Jidda ta fada cikin tsawa da daga murya dabara ta fado mata cikin muryar kuka tace cemin yayi na dinka gyara masa daki ina karkadewa baya son ya dawo yaga yayi kura ko datti Hamdala Jidda tayi Rubayya tace shiyasa zargi bashi da amfani kunji ko ? Hankalinku sai ya kwanta dafa kafar Jennifer Jidda tayi kiyi hkr ina son ya khaleel fiye da tunaninki ban taba ganinshi da mace ba sbd yanda halinsa yake na rashin damuwa da mace ganinshi danayi dake naji takaicin da ban taba ji ba kiyi hkr tsaki zahra ta ja meye abin bada hkr ? Warning xaki yi mata ta fita sabgar mazan gidanmu dan masu ajine babu irinta bankiba ko mai gadi ko danjuma driver ya isa haka zahra Rubayya ta katseta mgn ta wuce tsaki zahra ta kumayi plx Anty Jidda mikomin air freshener na kusa dake warin rashin sarki ya dameni ta mika mata tafeshe motar dashi Rubayya ta kunna wakar India tana ji tana bin wakar hade da kyada kai alamun tana son wakar hawaye ya saukowa Jennifer ta runtse ido tana mmkin yan gidan wasunsu masu kirki wasu marasa kirki

By

*UMMEEYY*

[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

33&34

Cikin mutuwar jiki ta mike ta hau sama suka bita da mugun kallo musamman zahra daki ta koma ta jingina ajikin kofar dakin nata tana kallon wayar me shegen Kyau murmushi tayi najin dadi ta karaso kusa da gadon dakin ta xauna hade da kunna wayan abinda ya bata mmk layin da ta gani na mtn ta xaro ido dariyar farin ciki da kufce mata kwanciya ta yi hade da rungume wayar ajikin taji dadin wannan kyauta ta kuma yi mmkin ta yadda akayi yai mata kyauta iri daya da budurwarshi da kuma kannansa amatsayinta na Yar aiki danne danne ta farayi ta shiga nan ta shiga cen cikin matukar jin dadi ta duba account taga ful da kudi har 30k dariya ce ta kuma

kufce mata tayi far far da ido tana addu'ar Allah yasa ka mishi da alheri wayar tai mata duk abinda take bukata ta samu taji dadi sosai ta mike agado ta cigaba da danne dannen wayar xuciyar ta fal farin ciki

********************

Tun daga lokacin suka fara takun saka da Jidda ga yawan sata aiki da takeyi shima kamar ana turashi dan kullum cikin sata yi mishi aiki yake girki gyaran daki da coffee Sam bata gajiya tunda ta saba dashi tana kitchen dafawa yaya khaleel grilled chicken and Indian drink juice Momy ta shigo yawwa Jennifer kin gama ?? Eh Momy na kusa OK yanxu dadyn su zahra yai min waya yana nan dawowa ki gama kixo muyi aikin tare toh Momy agurguje ta gama ta kwashe ta kai masa sannan ta dawo suka hadu suna aikin girkin tarbar dady kamar yadda aka saba basu dade ba suka gama Jennifer ta gyara gidan ko ina ya dau kamshi da sheki

Some hours later

Motocin da sukaje tararsa suka dawo gida ya rude da murnar dawowar dady gaba dayanmu ma'aikatan gidan muka fito mukai mishi barka da xuwa duka yayansa suna jikinsa cikin farin ciki da murna tamkar xasu shiga cikin cikinsa suka mike suka nufi bangarensu Jennifer dakinta ta wuce ta xaune tayi tagumi tana tunanin yanda ta gansu cike da birgewa familyn nan nasu yana matukar birgeta wayar ta ta janyo tayi murmushi duk lokacin da kalleta sai taji farin ciki ta kuma tuna da yaya khaleel

***************

Bayan kwana 2 da dawowar Abba da daddre bayan ta kwashe kayan da suka ci abinci ta dawo xata wuce dakinta ta gansu xaune suna hira dukkan su a falo Jidda tana kusa da ya khaleel dady yana tsokanarsu tana shiga ta wuce toilet tai wanka ta kwanta bacci ya fara surarta daka mata duka taji anyi a firgice ta farka ta xaro ido tana kallansu xahra da Jidda suna karkade karkadan jiki na jin bala'i tashi malama ansamu waje anji sanyin a.c an narke a gado zahra ta fada tana mata yatsinan nan kallo Jidda tace mike ware ido albishirinki ?? Ta cewa Jennifer shiru tayi tarasa ce musu kala sbd mamakin da suka bata ranar juma'a jibi  Sa ranata da ya khaleel dai dai da birthday dinshi idan kinsa wani abu aranki game dashi sai ki cire sbd ya khaleel ba mijin karamar mace bane bagidajiya dangin su ojuku makiya Allah taja tsaki zahra ta cigaba da inda Jidda ta tsaya wannan shine warning na karshe tsakaninki dashi ke dama maxan gidanmu gaba daya ki fahimci wani avu mana taya xa'ai me tsarki ya hada iri da kaxanta

? Idan ma a nayi to banda gidanmu ke abubuwa sun hadu sun miki yawa ga tarin datti na kaxantar kafurci sannan ga talauci kina manta matsayinki na Yar aiki ?? Idan bakiyi wasa ba xaki tsinci kanki agaban iyayenki dan wllh sai mun hada miki bala'in da xaisa kibar gidan tai tsaki Anty Jidda muje suka fice ta bisu ta kallo hawaye na sauko mata baccin da batayi shiba kenan takwna tana juye juye

*****************

Washegari bayan sun gama yin breakfast sun kwashe kayan ita da suwai ba suka ga ma aikata na shigowa ana gyare gyaren gidan suwaiba tace ikon Allah ni banga abinda gidan nan yayi ba amma sbd kudin sunyi yawa sai wani gyare gyare akeyi Jennifer tai murmushin yake gyara yaxama dole gobe Sa ranar Mr coffee shida sahibarsa ta cije lebe Jidda hade kuma da birthday dinshi xaro ido suwaiba tayi wai ! Burin Jidda ya cika ana nan ana xuba rawar kai da farin ciki Allah ya kyauta Jennifer ta kalleta cewa xakiyi Allah yasanya alkairi hakane Jennifer Allah yaxaba abinda ya fi alkairi dariya adduar suwaiba ta bata ta kwashe da dariya suwaiba kenan itama dariyar tayi washe gari tana kwance jikinta amace ga bacin rai da takeji rabonta da bacci tun ranar da su Jidda suka tasheta ruby ce ta shigo dakin cikin fara'a Jennifer ta mike daga kwancen da take ta gaisheta ta amsa xo muje wajan makeup kinsan yau muna da shagali ta mike ta dauki gyale ta bi bayanta suka shiga mota Mon evee sukaje saloon akai musu sannan makeup sunyi tsananin Kyau anan Rubayya ta dakko gown ta material sky blue ta bata tai godiya suka canxa kaya ita kuma colour din ruby silver ne dukkansu dai sun saka skin colour dinsu ruby ta kalli Jennifer masha Allah kwalliya me gyara mutun gsky kin fini yin Kyau kin ganki kamar amarya da sauri me musu makeup din tace OK da ba itace amaryar ba dariya sukayi kanwar amaryarce dai dai lokacin data gama Nada mata head me shegen Kyau blue ya fi material din jikinta duhu suka hawo mota suka dawo gida ya cika dam da baki anata gaishe gaishe kallo ne ya dawo Kansu musamman Jennifer duk inda ta wuce sai ido wajan Momy suka karasa tana tare da kawayenta tayi kwalliya me Kyau ganin Jennifer yasa ta xaro ido tana murmushi y'ay'ana masha Allah kunyi Kyau Jennifer kece ? Kamar ba keba ta rungomata jikinta kinyi Kyau sosai wani dadine ya rufe Jennifer ta koma gefe tana hange hange can arakube ta hango su suwaiba ta mike tana tafiya ta karasa wajansu suka dago kai suna kallonta Sam basu gane taba tai murmushi tace suwaiba ta amsa tana kura mata ido Jennifer suwaiba ta fada tana xaro ido kece ?? Tsarki ya tabbata ga Allah dama haka kike ? Kin ganki kuwa yanda kikasan sarauniyar kyawawan duniya hannu tasa ta rufe ma suwaiba baki tabbijam suwaiba ta ambata ruby ce ta kira ta ta tafi tana tsokanar suwaiba ita da kawayenta su uku ta taddasu murmushi rubyn Taiwan Jennifer xaku gaisa da kawayena wannan ta nuna wata fara doguwa itace mufeedan ya mahboob ta mikowa Jennifer hannu suka gaisa wannan humaira ce kawata Yar gidan governor na bauchi itama gaisawa sukayi cikin fara'a sai hishma Yar gidan Alhaji Sani minister na man fetur suka gaisa hade da dan taba hira wajan ne ya dauki sowa sbd isowar ango da amaryarsa ta kallesu sunsha Kyau mahboob ne ya karaso ya kura mata ido Jennifer? Ya fada yana kalonta wow ! Wayarsa ya ciro ya hau daukan ta a photo kin cinye taro kawata kinfi kowa Kyau zahra ce takaraso inda suke ya mahboob ga kabeer cenfa yana jiranka ganin

Jennifer yasa tayi sororo jikinta amace fuskar ta da matukar mmk nan da nan ta bata rai hannu ya mahboob ta ruko plx muje hade da galla wa Jennifer harara Jennifer biyo mu yace mata tana sane dan ta kunta tawa xahara tabishi tana tafe cikin yanga sbd taji ance tayi Kyau yasata sauya taku hnklin mutanen da suke wajan yai kanta ciki kuwa harda ango da amarya kura mata ido ya khaleel yayi Jidda kuwa mmkine ya cika ta ganin Jennifer na kokarin fita Kyau wani kululun bakin ciki ya tokareta duk da kayan jikinta ya fi na Jennifer tsada nesa ba kusa ba takarsa inda ya mahboob ya tsaya shida zahra wajan wani black beauty tana kara sowa yace wow! Yanmata barka da xuwa anan gidan kike ? Ya akayi ban sanki ba ? Zahra ta budi baki xatai mgn da sauri Jennifer ta tareta da cewa ni Yar aikin gidance gwalo ido yayi cike da mmk ya haisam ya karaso wajan hannunshi rike da na wata zahra tace oyoyo Anty meena tasaki hannun haisam suka rungume juna haisam shima kallonta ya ke da mmk ta kalli ya mahboob ina xuwa tace tabarsu direct wajan ango da amarya tayi cikin murmushi tace pix zan mana da mmk Jidda ta kalleta haushi ya kamata shima khaleel din hararta yake hnklin mutanen wajan yai Kansu kafin suyi mgn ta ciro waya ta fara daukansu photuna sannan ta juya ta cigaba da rausaya wayarta taji tayi kara tana dubawa taga text ne ta bude number ya khaleel ta gni kije dakina ina son kimin wani aiki ajiyar xuciya tayi dan masifa ma yau din baxa a barta ta huta ba dakinshi ta nufa tana mita aranta ta bude key din dayake jikin kofar tashiga a gyare taga dakin ta xauna tana duba pix din da sukayi ta xaro ido gsky ta yadda tayi Kyau sosai batafi 5 mints ba ya shigo da sauri ta mike wani irin kallo ya bita dashi cikin fada yace waya baki ixinin yin wannan kwalliyar ki dinka rausaya agaban mutane duk kin dame kin fito da duk wata halitta ta jikinki kin San kanki kuwa ? Mmk ne ya hanata mgn ta xuba masa ido shin baiga kayan da kannansa da amaryarsa suka saba rike kugu tayi dan tagaji da wannan rainin wayon ni wannan bai shafeni ba aikin dana ke muku bamuyi daku xaku dinka bindiddigin rayuwata ba ta murguda baki matsa in wuce da mmk ya kalleta babu inda xaki akan me ? Ta tmbyeshi sbd bana bukatar ganin ki da wannan shigar cike da tsiwa tace sbd kana bakin cikin karna sami mijin aure eh hakane ya bata amsa ta xaro ido sbd me ? Sbd kina dashi arikice tace mijin ? Eh ya fada yana kallonta ta murguda baki bana sonsa koma waye dama baki da kunya ? Tai far da ido baka Sani ba ne to baki isa ba bari innu na miki tawa rashin kunyar fincikota yayi ya hada ta da bango numfashinsu na karo da juna kadan yarage tudun kirjinta ya hadu da nashi ranta ya baci akan me xaka takuramin ? Sbd na isa  cikin jin haushi tace to sai na fita ya Matso da fuskarsa har saida  karan hancinsa ya hadu da nata numfashinta ya fara fita da karfi kasakeni wannan ai mugunta........caraf taji bakinta cikin nashi yana tsotsarsu kamar ya samu alewa me shegen xaki

By
*UMMEEYY*
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

37&38

Yai mmk sosai ya kurawa wayan ido me yaka mata yayi shin xaibar bikin gidansu yaje ?? Ajiyar xuciya yayi jikinsa ya mutu kiran wayan ya kuma yi ga mmkinsa sai yaji switch off ranshi ya baci akira ace ana son ganinka sannna akashe waya ?? Yai tsaki shifa baxai kara karanbanin binckar wacece itaba har sai lokacin datagaji ta aiwatar da mummunan kudirinta da sauri ya koma cikin gida hannun shi rike da damin rafofi na liki

***** *****

Liki sosai A.k yake mata guri ya cika da mutane kowa na liki anata xuba kudade a hankali ta xame daga cikin filin rawar ta nufi cikin gida kai tsaye dakinta ta nufa tarushi GAM sannna ta xauna ta rushe da kuka kuka sosai take xuciyarta akuntace meyasa ya khaleel yake mata haka ?? Meyasa rayuwar ta take cikin rashin sa'a ?? Meyasa komai yake xuwan mata adabarbarce ? Kuka tasaka Wanda take matukar so yau ake Sa ranarsa da wata shikenan tayi asarar first love dinta ?? Meyasa shi baya sonta ?? Ta yi shiru ta tunani xuciyar ta ta tuna mata baya sonki xaiyi kissing dinki ?? Murmushin jin dadi ya kufce mata daxu daxu ya shanye miki lip tas hannu tasa tashafa lip dinta ta lumshe ido ta tuno lokacin daya ke kissing dinta tsikar jikinta ta tashi ta ajjiye ajiyar xuciya idonta ya kai kan wayar ta baya sonki xai sai miki waya iri daya da ta budurwarsa ?? Dariya me hade da kuka tayi ta janyo wayar hade da rungumeta akirjinta ta kunna wayan ta bude images din da tai musu ta tsaya kan Wanda sukayi ita da ita yayi masifar Kyau ferpect mach ta fada tana murmushi ina sonka Mr coffee kai kadace da tsarina da kai kawai xan iya rayuwar aure haka taita sambatu xuciyarta kamar madaci kidan data keji ya fara damunta haushi ya cikata sai yamma likis dan har anfara kiran sallah sanna taji hayaniya ta tsaya kidan ma antsaya taji dadi kwankwasa kofa akayi ta tashi ta bude gabanta ya fadi ba walwala afuskarsa ya shigo hade da rufe kofar yana kallonta dagani kasan na tuhuma ne ke bakyajin mgn ko ?? Me nace miki ?? Bana ce ban yadda ki koma ba ?? Shiru tayi kanta akasa tarasa amsar bashi zan dau babban mataki akanki me prince A.k garkuwa yace miki muryarta na rawa tace cewa yayi yana sona runtse ido yayi cikin jin haushi da jimami ke kuma me kikace masa ban bashi amsa ba dariyar me naga kunayi dashi tai shiru bakiji bane ! Am a a ban wllh Mr coffee bakomai what ? Mr me ? Da sauri tasa hannu ta rufe bakinta Sam batasan da sunan da takirashi ba murmushi yayi ganin ta tsorata ki fada masa kina da miji bana son na kuma ganinki da shi adake tace miji ? Nifa ya khaleel ba aimin miji ba matsowa yayi kusa da ita yasa hannu ya dago mata da fuska look dago kai ki kalleni ta dago kai atsorace ni nai miki miji bana son ki kula kowa ta sunkuyar da fuskarta ya dago da fuskar meyasa kike son wahalar da kanki ? Ta kalleshi shima kallonta yake suka kurawa junansu ido batare da sun fargaba muryarshi taji asanyaye Jennifer ya kira sunanta jikinta amace ta amsa da kyar hade da sauke fuskarta dago ta ya kuma yi ya matso gab da ita sunajin iskar numfashin su kin fisan kiyita wahalar da kanki ?? Meyasa baxaki ba xuciyarki abinda take soba ya fada yana kurawa lip dinta ido babu komai

axuciyata karya kike akwai kinfison ki barshi aranki sai dai kishigo daki kita rusa kuka da sauri ta kalleshi ki fada plx yafada cikin wani yanayi idonshi akan lebenta ahankali ta xame tai katsa ya bita da kallo dan jikinsa yai matukar sanyi ya juya xai fita tabi kyakyakyawan bayansa da kallo ki tabbata kin fada mishi abinda nace sannan kada ki kuskura ki bashi numb dinki ya fice daga dakin hawaye ya sauko mata tarasa gane inda yasa gaba  ta mike da kyar ta shiga toilet dan tayi wanka

****** ******

Tana fitowa daga wankan ta Sa doguwar rigar less ta shafa mai hade da yin kwalliya sosai duk tasan dare yayi ba kuma inda xata tana cikin shafa janbaki maroon ruby tashigo kina nan anacen anata nemanki ta xaro ido kadan waye yake nemana ?? A.k Garkuwa kin rikitamin bro fa kiyi sauri tai shiru sbd karar kiran wayar ta murmushi tayi special bro gata nan dariya to shikenan kafata kafarta xan kawo maka ita yanxun nan ta katse wayar kinga yadda ya daga min hnkl shi Jennifer Jennifer taso muje gaban Jennifer ya fadi da ta tuno gargadin mr coffee sannan tana matukar jin kunyar ruby baxata iya musu da itaba jikinta sanyaye ta mike tabi bayanta ruko mata hannu tayi sukai bangaren ya khaleel kai tsaye dakin suka shiga ita kam a tsorace ta shiga dakin xaune ta ganshi da farar singlet da yana ganinsu yasaki murmushi special sis ngd sosai dariya tayi nacika alkawari ta juya asha hira Ify ta fice ya harari Jennifer shine kika gudu kika barni ko ?? Kai dan rainin hnkl gata nan dakace baka sonta ba da sauri ta kalleshi dan batasan yana dakinba yana kwance kan 3 siter yana sanye cikin farar sheet da 3 quarter yana danne dannen wayrashi cikin hada rai yace meye haka Prince ? A gaban yarinya kake irin wannan zancen dariya yayi sorry manya Jennifer ya kira sunanta ta amsa ina son naji amsata ta saci kallon ya khaleel idonshi a kanta ya galla mata harara karar shigowar test taji ta duba ya khaleel ne ... Ki fada masa kina da miji kin amince min xaki aureni ? Da bara ta fado mata tace ina so kabani lokaci zanyi shawara wani kallo ya khaleel yai mata wane irin tunani malama ki bashi amsa yanxu khaleel plx kabita asannu a tsorace tace kayi hkr ammin miji ta kalli ya khaleel yai mata jinjina da hannu ta saki numfashi wannan ba damuwa bane Jennifer tunda ba ki aure ba zan cigaba da Neman aurenki har sai kinyi aure zan hkr Suka  kalli juna tai murmushi hade da cije lebenta na katsa wato ta rama abinda yake mata kwafa yayi ya mike ya shiga bed room dinshi yana barin wajan taji zaman ya gundireta ta mike wayar ta tafi A.k yasa hannu ya dauka yai dialing numb dinshi kiran ta shigo yaga numb din sannan ya mika mata wayar sukai sallama ta fice daga dakin jagwab ta fada kan gado tana tuna abinda ya faru tsakanin su banko kofa taji anyi gabanta yai mummunan faduwa ganin su zahra cikin tsawa zahra tace ubanwa ye yace kiyiwa Prince A.k mgn ke wacce irin mayyace ? Anty Jidda anya kuwa banza take barin maza shegiya duk inda taje sai ance ana sonta ? Ina fa banza agumi take musu irin Nasu na mugayen yare to wllh ahir dinki Jidda tace kina kallofa da kyar na rabata da ya khaleel irin bakin cikin dana kunsa akan wannan kafurar wai ma waya gayyace ki taronmu ?? Kin wani Sa banxan karamin  material dinki kina rausaya wai ke mai Kyau fadamin suwaye munana ?? Zahra tace warning na karshe dan ubanki ki fita har kar A.k dan yafi karfinki kije kisami dan jagaliya dangin ojuku ki aura ba ki dinka hange hangen wayanda suka fi karfinki ba

shasha sha ! Anty Jidda yarinyar nan sai mun mata Jan wuya na fuskanci Yar rainin hnkl ce cikakkiyar Yar iskaba xamuyi maganinki kin kusa barin gidan nan akoma cen acigaba da sai da garau garau sukai mata tass sannan suka fice ta share hawayen fuskarta da ya xubo tai tsaki ke kika damu da wani Prince A.k garkuwa

Basu dade da fita ba ya shigo awahalce ta kalli kofar yau kam taga ta kanta ya tsaya atsaya hannunshi cikin aljihu baxaki huta ba har sai kin fadi abinda ke cikin xuciyarki kada ki kuskura wata alaka ta hadaki dashi kiyi maza ke yanketa ki fada mishi kice mijinki baya bukatar ganinki da kowa ko dole ne yaja dan karamin tsaki ke ! Ta turo baki nifa ba sunana ke ba yai shiru yana kallonta ni kuma dashi nai niyyar kiranki mai yasa baxaki fadi maganar Da barinta xai iya janyo miki ciwo shikenan tunda kin xabi ki barta tai ta wahalar dake ya fice tabi kyakykyawan bayanshi da kallo tana mmkin maganganunsa a hnkl ta furta ina sonka mr coffee amma baxaka tafajin Kalmar nan abakina ba koda kuwa xata xame min illa araina kuka ya kufce mata ranar kam batai barci ba tunane tunane ta kwana yi

*****     *****

Washe gari ya haisam ya wuce office ya dauko wasu muhimman takaddu da ya manta su acen yana shiga ya gansu su uku biyu maza ita kadai mace ya kallesu ta waiwayo tana xabga masa shu'umin murmushi kana mmk ? Ta fada tana kallonsa meye abin mmk dan na ganki anan bayan nasan xaki iya aikat fiye da haka me ya kawo ki office dina ? Ko kin gama aiwatar da aikin daya kawoki gidanmu ? Wai shin Jennifer ke wacece ? Murmushin ta Kuma  yi nima shina ke so nasani ya wurga mata kallo wannan kuma ke kika sani dan bazan yadda da salon rainin hnklinki ba plx haisam ta katseshi wacece Jennifer ? Mikewa yayi yana kallonta dan gani yake ta gama raina masa hnkl wacece ke ? Ni kike tambaya matsayinki ? Ni bani bace Jennifer ta kalli mazan nan biyu Mara Sa Kyan gani suka fita so nake nasan wacece ita sunana hindatu .......

By
*GARKUWA*
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

39&40

Wani irin kallo yai mata me kike son cemin kwantar da kai tayi nafada mk bani bace Jennifer wacece ita ?? Yayi shiru hade da kallonta inajinki yafada yana gyra xama

Sunana hindatu ban San kaina ba ban kuma San wacece ni ba nataso a hannun marikina gawurtaccen dan fashi dan damfara dan safarar kayan maye yanxu haka yana hannun hukuma atsare kafin aka mashi yasha fadamin ba shi ya haifeni ba duk lokacin Dana girma xai bani wani Ibr me ban mmk akaina kwatsam ranar damukaje fashi a shopping mall na ganka har ka kirani da wani suna daya ban mmk dalilin dayasa na hana akashe ka dan abinda na da de ina nema kenan in San kaina shiyasa naita bin diddiginka har na gano inda kake

Shiru yayi yana kallonta dan shi Sam  bai yadda ba ita bace bace wayar shi ya ciro ya kira mahboob bata dade tana ring ba ya daga yace dan Allah mahboob hadani da Jennifer zan sata wani aiki gata ma muna tare a kitchen ya mika mata waya atsorace ta amsa ya rasa mai zaice da yaji muryarta tabbas itace ya kalli hindatu datake gabanshi ya kuma saurari muryar Jennifer da kyar ya saita kanshi yace ta dafa masa indomie yana nan tafe ya kashe wayar ya kalli Hindu tai murmushi kadan yasaki numfashi ikon Allah Allah mai halitta kin San wani abu ? Kai ta girgixa dai dai da maganar Ku iri dayace ba banbanci yanxu ya kikeso ayi ? Ina so duk yadda xa ai yanxu ka kirata taxo nan office dinka muga juna kamata yayi kitashi muje gidanmu kai ta girgixa masa koda zanje gidanku to ba yanxu ba kai tsaye numb din Jennifer ya kira ta daga atsorace yace taxo xata rakashi kasuwa akai kayan matan da yake son siya amma a office xata sameshi yanxu yanxu danjuma ya kawota ganin cewa a gaggauce yace yaxo yasa ta fito da sauri ta fada wa danjuma ya dauketa suka taho

****** *******

Basa bata lokaci ba suka iso yace danjuma ya juya ita kuma ya shigo da ita a tsorace take dan gani take kamar wata muguntar ya shirya mata ta ga mace axaune amma bata ga fuskar ta ba sai da taje gab da ita ta saci kallonta karaf suka hada ido a kidime suka mike lokaci daya suka mike hade da kurawa junansu ido Jennifer ta nuna ta da yatsa wacece ke ? Hawaye ya xubowa Hindu tace wa haisam kayi namijin kokari Dole ka kasa tantanceni da wannan halittar Alhamdllh lallai wahalata taxi karshe ki karemin kallo ni Yar uwarki ce rungumeta tayi ita dai Jennifer mmk da ta ujjubi ya hanata mgn ta xauna jikinta na karkarwa Hindu tace dole ki kasa mgn tashi muje ki nuna min iyayenmu abakinsu xamuji komai haisam ya mike gsky kam.dan al'amarin naku akwi son jin dalili gaba dayansu suka mike itakam Jennifer binsu kawai take har suka shiga mota dake haisam yasan hanya kai tsaye ya hau titi Hindu ta kalli Jennifer kinki mgn ta kawo wani gwauron numfashi sannan tace mmk ne ya kamani ban taba tunanin haka ba sai ga shi na ganki wllh babu wani abu daya banbantani dake axahiri sai dai ko abadini nayi mmkin wannan ikon Allah ni kaina banyi tunanin tsananin kamarmu dake takai haka ba dai dai da murya fa ko ba'a fada ba ai ansan mu yan uwan juna ne haisam ya tsaya dai dai kofar gidansu Jennifer kai tsaye cikin gidan suka shige a daki suka tadda Maman David ita da papa da David da yake kwance akan cinyarta da gudu Jennifer ta karasa hade da fadawa jikin Maman David da oyoyo my jenny su haisam suka karaso shida Hindu araxane Maman David take kallon Hindu

murmushi tayi hindun ta shigo Jennifer ya nunawa mama Hindu mama dama mu biyu kika Haifa ? Ya akayi baki taba fadamin ba fata rai tayi ke kadai na Haifa wannan ban Santa ba sam papane ya kalli Hindu da mmk yace wannan wanne irin kama ne ? Mikewa mama tayi me kuka xo yi ?, tacewa haisam kuna son sawa yata wani irin tunanine ? Dama sam hnklina bai kwanta da yin aiki a gidanku ba Ku tashi Ku fita ni yata ita kadai na Haifa bansanki ba ke ta nuna Hindu hawaye ya saukowa Hindu ko baki fada ba ni nasan ba ke bace uwarmu hannu tasa cikin riga ta xaro karamar bindiga ta nuna kan David ko ki fadamin gsky kona kashe ramammen dan nan naki kuka mama tasa plx karki harbeshi haisam ya mike Hindu kibi ahnkl kada ki harbeshi idan har bata fadi gsky ba kashe shi zanyi inkashe wancen mijin nata me kwala kwalan ido jin an ambaci papa yasa yace ko baki harbemu ba dole gsky tai halinta kuka Jennifer tasa kina da hnkl dan sunce ba iyayenki bane shine xaki kashesu ? Yimin shiru ! Hindu ta kwatsa mata tsawa ba iyayenki bane papa ya mike ina zaka hindu ta fada tana Nunashi da pistol din hannunta ya daga hannu sama zan dauko muku wata shedane yana ina ? Ta tmby shi yanuna wani tsohon akwatunshi haisam ya tashi da Kansa ya dauko papa ya bude jikinshi na rawa ganin anbude akwatin yasa mama rushewa da kuka wata leda ya dauko acikin akwatin ya xaxxageta kayan jarirai na sanyi da wani karamin dankunne da awrwaro na gwal suka fado sai envelope ya ciro wani karamin pix tabbas Jennifer Yar uwarki ce dan gashi nan a pix din da muka tsince ta ya mika mata pix din ta kalla hawaye ya sauko mata duk wayan nan kayan ina da irinsu ya akayi ka tsince ta ??,

Yana rubuce ranar talata a shekara ta 1995 watan July anan garin KANO a unguwar janbulo da safe muka tadda an ajjiye ta agefen bola dai dai kofar gidanmu nacen jikinta dauke da wannan kayan kunnanta da wqnnan barimar hannunta sanye da wannna awarwaron sai wanna envelope din aciki ansaka wannan pix din da kuma takaddanta na haihuwa wannan ranar ta nuna watan ta daya da kwana goma cif rushewa da kuka sukayi dukansu hindu da Jennifer ita hindu tana kukan bakin cikin wannan ramari cikin kuka tace rana daya aka wullar damu hannu tasa a aljihu ta ciro barima irin ta Jennifer da awarwaron sak iri daya sauran kayan suna cikin mota itakam Jennifer kukan tarasa gane kanshi babban bakin cikinta bata San wace rayuwa xata faraba da mmk papa yace kina nufin kema wullar da ke akayi ? Kai ta daga masa tabbas ina so kubani yar uwa ta muje mu binciki asalin iyayenmu papa mungode da taimako Jennifer ta tsaya da kukan ngd iyayena har gobe Ku iyayene kuna raina amma kuyi hkrin rashina na wani lokaci lokaci daya naji ina son ganin aslin iyayena dole zanbita baxan iya xama da wannna daukin ba takarsa da kuka mama kukan takeyi nabaki goyon baya jenny Allah yabaku Sa 'a hindu ta mike haisam ya mike xuciyarshi cike da tausayinsu Jennifer fa ma mikewa tayi tana kuka mama xan dawo nan da kwana 2 tafice da sauri tana kuka suka shiga mota gaba dayansu

****** *******

Haisam ya ce ina xamu hawaye na sauka a idon hindu tace gidana dayake cikin hotoro g.r.a ya ce ita kuma Jennifer fa ? Shine ban San ya xamuyi ba muje cen din ma yanke shawarar yadda xa ai basu bata lokaci ba suka iso kai tsaye falo suka xauna dukkansu jikinsu asnyaye Jennifer

tace ta ina xamu fara Neman iyayenmu haisam yace wai Hindu wacece wannan matar dana ganki da ita a saudiyya? Tai masa wani irin kallo saudiyya ??ta maimaita yes ya fada yana kallonta ko bake bace sulthaana ? Araxane ta mike cike da jin dadi bani bace Alhamdulillah bani bace shikenan wahalar mu ta yanke iyenmu nacen duk yadda akayi matar nan itace mahaifiyar mu ikon Allah haisam ya fada tabbas kuwa dan akwai sulthana ban da yanxu kince min ba ke bace baxan taba yadda ba dan yanda kuke tsananin kama da Jennifer haka take da Ku itama Jennifer dadi taji ya kamata yanxu ya xa ayi muje saudiyyan ni in kun yadda ma gobe muje kai haisam ya girgixa mata baxaiyiyu gobe ba nan da 1 week dai haisam plx hindu ta fada xuciyata tana cike da kwadayin son ganin iyayena ki kwantar da hnklinki dolene sai munyiwa Jennifer biza cikin satin nan dai ajiyar xuciya Jennifer tayi haisam ya kalleta yanxu wqcce shawara kuka yanke ?? Tame ? Suka tmby shi Jennifer mana anan zan barki a a ya haisam tare xamu koma gida dan bana son kowa yasan wannan zancen har sai mungama iyayenmu plx ka rufa min asiri murmushi yayi bakomai gobe gobe zansa a fara miki shirye shiryen tafiya ya mike yana kallon Hindu kefa kutafi Ku barni anan dan bani da wata matsala suka wuce a cikin mota Jennifer ta dake ya haisam ina son tmbyrka ? Wai shin ya akayi haka ta faru ya kwashe komai ya fada mata ta fashe da kuka yana rarrashinta har suka so gida

*******************

Suna shiga sukaci karo dashi yana kokarin shiga mota yai mmkin ganinsu tare nan da nan fuskrashi ta canxa gabanta ya fadi asanyaye ta fito daga mota yana harararta cikin gida ta shige tana jin tsoron abinda xai biyo baya awahalce ta xauna agefen gado hade da dafa kanta daya ke juyawa anya ma kuwa itace ? Jin kanta take kamar ba itaba wai mama da papa ba su suka haifeta ba jin abin take kamar amafarki ta fito daga daki xata gyara falon kasa a xaxxune tagansu dukansu dake har yanxu gidan acike yake da bakin da basu tafiba yawwa ummana taji muryar Jidda kinga mahukaciyar yarinyar da muke mgnr ta daxu ta nuna Jennifer gaba dayansu suka xuba mata ido wacce aka kira mama tace aw wannan ce ? Ai nazaji Yar wani kusa ce agarin nan yanda naga tana daukan knta jiya tana lika daloli ashe Yar su ujuku ce Yar gidan Malan shehu ke ! Jaraba kike kowa ? Gaba daya falon suka Sa dariya banda Momy da ruby zahra tace Jennifer OK koma wa kike xonan atsorace ta je kusa da ita hannu tasa da damki kunnanta meye matsayinki a wannan gidan tana xubda hawaye tace Yar aiki kinga wannan ta nuna zahra da Jidda daki taba minsu kwara ki tabani aknsu babu abinda baxan iyaba bani da Kyau in aka shiga gonta tun jiya aka kawomin kararki babu ke ba Ibrahim bare kuma Prince A.k Garkuwa sbd ba sa'anninki bane sun girmi ajikinki banda ma jaraba irinta namiji mai xaiyi da kaxanta? Dan Allah tashi tasakar mata kunne maxa akawomin hypo da kleen na wanke hannuna na taba kaznta fice kiba mutane waje sum sum ta wuce tana xubar da kwalla daki tana shiga daki ta fada gado hade da rushewa da kuka karar wayarta taji ta daga ba tare da ta duba suna ba muryar Momy taji kiyi hkr Jennifer bani da yadda zanyi sbd ianwar dadynsu zahra ceki kwantar da hnklinki komai zai wuce ba komai Momy ngd ta rarrsheta sosai sannan ta kashe waya

Da gamma tana xaune a daki ya shigo kamar ko yaushe fuskarshi ba walwala ya tsaya atsaye ina kikaje keda haisam ? Tayi shiru dan batai tsammanin tmbyr ba ke ! Bakayaji jine ? Cikin in ina a a a am mun munje kasuwa ne daga yau na hana ya fada cikin fada yai shiru sannan yace asanyaye kada na kara ganin kin fita da kowa kuma bana son nasake ganinki da mahboob ban yadda dakawacen Ku ba sannan daga yau karna kara ganinki da karamin gyale kina jina ?,kai ta daga masa kiyi mgn ina ji kuma zan kiyaye yayi Kyau yace sannan ya fice hawaye ya balle mata tana ganin abu iri iri

"**********************

Cikin sati daya haisam ya gama musu komai na tafiya taiwa Momy karyar xataje Edo state suka taho saudiyya

Saudiyya

Da yamma suka sauka Jennifer haushin hindu kawai takeji sbd tasa antaho da yaranta maza su biyu Mara Sa kyan gani ga gefe guda na xuciyar ta haushin hindun takeji batasan dalili ba haisam yai musu jagora dan suwa masaukinsu a hanya danja ta tsayadda su yana waiwayo fuskarsa yaganta acikin mota tana waya fuskarta cike da nishadi Hamdala dayayi da Saudi suka tmbyeshi yace ga wacce muke nema nan agabanmu baxasu iya ganinta ba dole suka hakura haisam yace drivensu yabi bayar mortar da ake janta basu Dade ba suka so wani tamfatse tsan gida mai gadi ya bude ta shiga suma suka bita ta fito daga mota tana yiwa motarsu kallon raini fitowa sukayi suna mmkin kamarsu da juna tana ganinsu ta kura musu ido ta kare musu kallo irin kallon sama da kasa sannan ta ya mutsa fuska suwaye Ku ta tambayesu araine ?
Dai dai lokacin da wata babbar mace ta karaso tana fadin oyoyo sulthana ganinsu yasa tai turus ta bata rai suwaye Ku a dake hindu tace mu yan uwan sulthana ne dan ko ba a fada ba ido ya tantance kuje kunemi inda yan uwan Ku suke yata itaka dai na Haifa tsaki hindu tayi nga alamar xaki raina mana hnkl mu kuma baxa mu jure ba xaro bindiga tayi ta nuna matar da ita ko ki fada mana gsky ko na daukeki da wannan sulthana ce ta shagaban matar dalla gafara malama ance ba sanku ba dolene ?,daga ka wai munyi kama ? Sai dai Ku harbeni tsawa hindu tai mata tsab zan harbeki dan naga baki da kunya fitsararriya matsa sulthana kada su cutar min dake cikin kuka matar take mgn tabbas sulthana ba yata bace tsintar ta nayi tafashe da kuka

By

*GARKUWA*
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

21&22

Kare mata kallo yayi kina Ify kuwa ?? Ya jefo mata tambaya ta kauda kai sbd tsura mata ido da yayi lafiya ya mahboob kawai kaina ne yake sarawa anya kuwa baxamu koma asibiti ba?? girgixa kai tayi basai mun koma ba zansha magani na daga kai yayi tasan kawai kyaleta yayi bai yadda da amsarta ba asanyaye ta wuce tana jin haushin Sa mata ido daya keyi musamman in tana cikin wannan yanayin data kasa gane mishi dakinta ta koma ranta amatukar bace babu abinda take tunawa irin yadda taga Jidda kwance gefen jikin ya khaleel tarasa dalilin dayasa take jin haushin haka anya kuwa taiwa kanta adalci ??

Tunda Jidda taxo gidan ta daina kai mishi coffee ko tee dan ta fuskanci kamar yana sane yake yimata haka indai yakira waya suwaiba take cewa ta daga ta kuma roketa da idan yace tana ina tace bata kusa jiddan ma kaucewa haduwa da ita take dan tana jin haushin ta tarasa dalilin dayasa hakan suna kitchen wajan Dora dinner hira suke jefi jefi wacce suwaiba ce karfin hirar ita hnklinta yatafi tunanin fitar da taga khaleel.sunyi da Jidda taji haushin ganinsu tare cikin farin ciki sunyi shiga mai Kyau da daukan hnkl da wuri suka gama ta fito kenan dan taje tai wanka ta ganshi tsaye kamar mai jiran fitowar ta alama yai mata da hannu cewar ta biyoshi garden ya wuce tabi bayanshi ba yadda ta iya tasan tsareta xaiyi da surutu da tsarin tsiya nuna mata guri yayi da hannu ta xauna shima ya xauna kusa da ita amincin Allah ya tabbata agareki maabociyar kyawu da kyautayi ina miki maraba da xuwa wajen nan ....dan karamin tsaki taja aranta haka ka iya tsarin mgn.....tare da kai ta amsa tana murmushin yake wow....murmushi yana yiwa kyawawa Kyau amma naki yafi dacewa da fuskarki idan kikayi murmushi fuskarki tana sauyawa ta koma asalin kirarata kyanki yana fitowa fiye da tunani tabe baki kawai tayi wannan abin dakikeyi Jennifer yana Sa kyanki ya haske duk wasu kyawawa dariya tayi dan yafara wuce gona da iri yasalam dariyarki tafito da kyawawan hakoranki Wanda haskensu ya haske taurarin da suka Dade da dushashewa ....girgixa kai tayi itafa wayan nan kalaman haushi suke bata ......ngd ya mahboob nine zan gode miki dan nasan kyawawan mata irinki suna da tsari da tunani akan Wanda yadace da suyi rayuwa dasu kowacce iri jennifer ya ambaci sunanta yana kallon kwayar ya idonta ta kalleshi ya kashe mata ido daya yana mata shu'umin murmushi ina son na tambayeki kanta akasa ta amsa da Allah yasa nasani ina son insan wacece ke ????
Araxane ta matsa da ga kusa dashi tana mishi wani irin kallo bangane ba ya mahboob?? nan da nan hnklinta yatashi sosai ta mike jikinta na rawa ya dago kai yana mmkin rikicewarta lokaci daya
Ina son nasan wacece ke ?? Maana tarihinki atakaice me kakeson Sani ?? Batasan lokacin da ta jefishi da tmbyr ba cigaba da kallonta yayi yana mmkin maganarta ban fahimceki ba Jennifer ? Laifine dan natambayeki asalinki ? Da sauri ta kwantar da hnklinta hade da komawa ta xauna

tana kallonshi  sunana Jennifer Solomon sunan mamata Sera amfi kiranta da Maman David gidanmu na cen bakin sabuwar kasuwa inda mamana take siyar da abinci mu yan asalin garin Edo state ne jim yayi yana jinta har tagama yayi murmushi hade da mikewa ngd ya kalli agogon hannunsa ankira magrub xanje nayi sallah gabanta ya fadi ta mike tanajin haushin rikicewar da ta nuna daxu tana addu'ar Allah yasa kada yayi tunanin wani abu ya wuce tabi bayansa da kallo itama tabi bangarensu cikin yanayi narashin jin dadi tafiya take batasan ina take Sa kafarta ba taci karo da katuwar mesar gidan daake bawa shukoki ruwa ta hardeta ta tafi luuu xata fadi caraf ya rukota hakan ya bata damar fadawa jikinshi sosai ta shaki kamshin turarensa me dadi ta lumshe ido tasan ya khaleel ne wani shock taji hade da bude idanunwanta data lumshe karaf suka sauka kanshi yana mata wani irin kallo kafin tagama tantancewa ya hanketa ta araxane ta kalleshi tuni tsoro da firgici ya ratsata hannu yasa ya tushe hanci yana kallonta a kynkymce kayi hkr ya haisam mummunan tsaki yaji kaxama yawuce hannunshi akan hancinsa yana toshewa ta juyo ta kalli ya khaleel da ya dauke kansa daga kallonsu ta wuce ta gabanshi tana mmkin wannan hadin me ban tsoro

Kansa ya dafe yana jin haushin taimakonta da yayi lokacin daxata fadi daya Sani kyaleta yayi ta fadi yaja tsaki kaxama datti munafuka mayaudariya yana nan xaune yana sake saken yanda xai bullo mata har yanxu yarasa ta ina xai fara a haka har akayi isha'i ya wuce masallaci yai sallah ya dawo gida kallo yafara yaji duk ya fita kanshi ya kashe ya kwanta yana tunanin wannan tunkushash shiyar matsalar ta Jennifer a haka bacci ya kwashe shi

Ganin shi yayi cikin wani daki mai duhu sosai yanda ba ya iya ganin komai can haske ya bayyana ya ganta tsaye da bakaken kaya da bindiga babba tana mishi murmushi meyasa kk son sanin ko ni wacece ?? Ya kalleta da mmk ina son insan mekikeyi a gidanmu ?? Ta bata rai xuwa nayi in kasheku araxa ne ya kalleta wani laifi muka aikta miki da kikeson ganin bayanmu ?? Babban dalili ne ina son daukar fansan iyayena da kuka kashe min su yanxu xan kasheka suma inkashe su Ta nunashi da bindiga .......a firgice ya farka ya hada gumi sosai yana ajiyar xuciya sai yanxu ya fahimci mafarki yayi me ba tsoro tashi yayi yana tunanin mafarkin yarasa me xaiyi laptop ya janyo yana duba abinda ya dace yayi istargram ya bude yana dubawa ya ga mahboob ya dora pix dinshi da Jennifer mutane da yawa sunyi liking suna xuxuta Kyan hoton ya duba yaga pix din yau kwana 3 da dorashi comments yake bi yana jin haushin xuxuta kyan Jennifer da sukeyi idonshi ya sauka kan wani comment da yagani ....kai menene hadinka da SULTHANA??? ya xare ido yana kallon comment din sulthana ?? Kanshi ya daure da sauri ya duba profile na mutumin daya ga sunashi Elmustafha ya duba yaga abinda yake son gani sauka yayi saga IG din yana jin dadin abinda ya gani dan xai tai maka masa sosai  dabara ta fado masa yayi murmushi ya kwanta yasan Sam shida bacci kuma sai ya gano wacece jennifer ??

Washegari da safe bayan sunyi break fast sun fito shida mahboob haisam ya kalli mahboob am mahboob ina son kabani laptop dinka da kake chat oh ! Tana daki na wullar da ita kasan kwana

2 dinnan dady ya bani aiki na kula da sababbin ginaginan shi ban sami lokaci na duba social network ba hamdala haisam yayi yanxuma cen xan wuce jiyma fa sai 6 na adawo yau ban San ma lokacin da xan dawo ba ya wuce sai na dwo OK Allah ya dawo da kai lafiya kai tsaye dakinshi ya wuce ya dauko laptop din bai sha wahala ba dan yasan code dinshi ya bude istargram yana jin fargaba dan baisan mai xai tarar ba test ya gani masu yawa da notification Test din ya bude wani test ya fisgeshi na Ammar ibn Muhammad ..hi guy meya hdaka da Hindu ?? Kasan wacece ita kai gaggawar goge pix din nan idan kuwa ba haka ba xakayi nadama kuma xaka Sa kanka cikin tashin hnkl

By

*UMMEEY*

[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

43&44

Kallon shi sukeyi xuciyoyinsu cike da mmkin ganin su haka da sauri Jidda ta juya tabar wajan zahra ta bita murmushi yayi hannunsa rike dana jenny yai wajan Momy cikin farin ciki yace Momy jenny taxama Yar ki ya ruko hannun Momy ya mika mata hannun Jennifer Jennifer taxama tamu ta fada min tana son ta musulunta fuska Momy ta saki hade da fadin alhmdllh nagode wa Allah rungume jenny tayi ruby ma takara so ta rungume ta naji dadi sosai ta ruko hannunta sukai cikin gidan xuciyar Jennifer tass da ita duk da tana cikin kunci Momy tace zan kira dadynku na fada mishi zansa khaleel yanxu yaje ya taho da Malan Dr Ahmad Sani ningi yaxo ya baki Kalmar shahada da duk abinda ya kamata dai toh Momy ngd a a karkiji komai Jennifer kin zama tawa ina jinki kamar yata Momy ta mike bari na hau sama ruby ta taso kusa da ita ina cikin farin ciki jenny yau xaki karbi Kalmar shahada murmushi tayi itama nima haka ruby xuwa anjima kinxama mu mun xama ke ta mike itama bari naje nayi wanka nagaji itama mikewa Jennifer tayi ta shiga dakinta aciki ta samesu kowacce fuskarta a daure zahra ce ta rufe kofar Jidda cikin kuka nan gidan kune ? Shiru tayi dan bata da amsar bata ke wacc e irin munafukan yarinya ne ? Zahra da take a tsaye ta janyo akwatin kayan jenny tace yanda kikaxo haka xaki koma yau yau din nan kibar gidan nan tunda bana ubanki bane cikin kuluwa jenny tace dole na bar muku gidanku dan nima nagaji da cin mutunci barina gidan baxai xama karshen rayuwata ba duk da ina talaka to xuciyata ba talaka bace ta janyo akwatinta ta fito ba kowa a falo gab da xata fita ta hango suwaiba da sauri ta karaso jenny me ya faru hawaye ya sauko mata suwaiba masu gida sun koreni su wa ?,zahra da Jidda salati suwaiba tayi jenny ta

juya ta bar gidan

******* **********

Gidan hindu ta sauka tana ta ruko jakarta hawaye na xuba a falo ta tadda sulthana tana kallo ta wullar da jakar kayanta ta shiga daki tana kuka sosai ta fada kan gado ta rushe da kuka sulthana ta biyo bayanta ta tsaya bakin kofa tana kallonta tana kuka karaso wa kusa da ita tayi ta rike mata hannu xatayi mgn itama kukan ya kufce mata kiyi hkr jenny haka Allah ya kaddara mana dole mu dauki wannan kaddarar jarabawa ce daga ubangiji Allah muyi hakuri mu cinye akwai kyakkyawar rayuwa nan gaba Allah baya jarabtar mutanen banxa hindu ta fito daga wanka ganin suna kuka yasa itama ta karaso kusa dasu ta rungumesu duka dolene muyi kuka dan munga rayuwa kuyi hkr yan uwana addu'ace mafitar mu dai dai lokacin haisam ya shigo sunyi matukar bashi tausayi ya tsaya yana kallonsu xuciyar shi a raunane jenny ta kallesu baku San me nake jiba ni kadai nasan irin feelings din dana keji yanda kikeji hk kowa yakeji hindu tace tana share kwalla a xuciye jenny tace kuma sai kin min fada ? Sulthana ta hararesu hade da yin tsaki ta nuna Jennifer jenny kike ko jinnu sunanki ya dace dake jinni cike da jin haushi jenny tace ke kuma ifrituwa what ? Ifrituwa ? Dariya hindu tayi kun radawa kanku sunan da ya dace daku ifritu ta kumayin dariya yadace da ke ta nuna sulthana akufule tace ke kuma kwankwamai mikewa hindu tayi ta nuna sulthana da yatsa wacece kwankwamai ? Itama mikewa tayi kece kwankwamai wani abun xakiyi ? Haisam ne yace dasu ya isa haka kuna bani mmk yanxu yanxu fa kuka gama kukan halin da kuke ciki baxa Ku taba zama Ify waje daya ba oh ya rabbi ya rike kai sulthana ta Matso kusa da shi sorry ya haisam bai amsa ba jenny naga akwatin ki a falo me ya faru ? Masu gidan ne suka koreni xaro ido yayi bangane ba ? Zahra da Jidda ya salam ! Sbd me ? Suna zargin muna soyayya da ya khaleel janyo stool yayi ya xauna al'amarin ya khaleel dinne da daure kai kinsan haka ya taramu nida mahboob yai mana warning mu fita harkanki ban gane ba ya haisam ya girgixa kai eh shiyasa kika ga mahboob ya dan canza miki ni kaina banda nasan Jidda xai aura zanyi tunanin ko sanki yake lumshe ido tayi ina addu'a Allah yasa kada zargina ya tabbata jenny jikin Jennifer a sanyaye ta tashi inaga ba Ku fahimce shi bane murmushi yayi ki tashi mu koma gida kiyi hkr ni kaina wani Sa in inna kalleki inajin kunya da kuma nadamar abinda nai miki a baya ya haisam kabar tuna baya komai ya wuce ni kai ne kaxame min fitila wacce tasa nasan wacece ni abu daya nake so kai min kanuna Sam baka son inda nakeba koda zakaji suna cigiya ta ta yai shiru plx ya haisam shikenan xanyi yadda kikso ya mike xanje gida dan Allah ki kula da kanki kada kuyita fadace fadace murmushi tayi baxanyi ba yana kokarin fita sulthana tace ya haisam ba sallma OK hindu zan tafi sai na dawo kwafa tayi ba hindu bace sulthana ce cikin ko inkula yace OK ya fice

****** *********

Momy ta fito daga daki tai dakin jenny taga wayan ta sauko kasa ta duba falo bata ganta ba tai kitchen nan ma bata nan hnklinta ya tashi taxa gaye gidan kaf babu jenny kai tsaye dakin

khaleel ta nunfa tana kwala masa kira ya fito ina Jennifer ? Momy Jennifer kuma ? Cikin tashin hnkl Momy tace ban ganta ba da sauri ya fito daga dakinsa yai cikin gida ba inda bai duba bai sameta ba yasalam ! Momy meyasa Jennifer zata bar gidan nan ? Abinda ban saniba kenan khaleel da sauri yai dakin su suwaiba ya tadda ita ta hada kai da gwiwa tana kuka ina Jennifer ? Ya tambayeta cikin tsawa sun koreta ta bashi amsa tana kuka suwaye ya fada cikin karaji zahra da Jidda ya juyo cikin bacin rai a babban falo ya gansu me yasa kuka koreta ? Yana fadan ne kamar xai dake su a tsorace zahra ta gudu bayan Momy tmbyr Ku nake ! Ya xaro belt Jidda ta tsure kayi hkr tasa kuka ina jin kishin ganinka da ita baxan iya jurewa ba OK ya fada kinyi mgn sbd ansa ranata dake ko ? To NAFASA ! Baxan aureki baki San darajar mutun ba baxan iya rayuwa da mutumin da baya daraja kanshi bare ya daraja na wasu khaleel ! Inji Momy meyasa ka rude hk ? Dole na rude Momy !! yanda ya fadi mgnr yasa kowa ya tsorata dan baita ba irin wannan fishin ba ya fice ranshi a bace daki ya shiga hade da rike kirjinshi sbd zafin daya ke masa yana fidda numfashi a hnkl yace jenny ina sonki ! Meyasa kika gujeni ? Kin San irin halin da zan fada na rashinki kusa dani ? Azabtar dani da kikeyi da soyayyanki bai isheki ba har sai kin nesanta kanki dani meyasa ? Kece rayuwata farin cikina kece mace ta farko Dana fara so yana mgn kamar tana kusa dashi nasani kina sona gardamar ki ta hana ki fadamin muyi rayuwa ingantacciya ? Ban taba cewa ina son wata ya mace ba ban saba ba yan mata sun sabar min da cewa su suke sona why ke baxaki fadamin ba ya dauki ruwa ya sha yai hmdl tayaya da girma na in ce ina son karamar yarinya irin jenny? Baxan iya ba meyasa xuciyata taso ta ? Kin xama memin tauraruwa me matukar haske plx plx plx kixo ki fadamin kina sona jenny starshine oh ya rabbi ! Soyayyar ki xata xauta ni laptop dinsa ya janyo ya bude pix dinta ne akai Wanda sukayi ranar Sa ranarsa da zahra murmushi yayi gardamarki starshine xata Sa na auri wata bake ba alhali ke ce xabina dole na takura miki ki furtamin da kanki kina sona ya kurwa lip dinta ido ya lumshe ido ya tuno lokacin da yai kissing dinsu tsikar jikin Sa ta tashi ya rungume hannayensa starshine rashinki kusa dani baraxana ce ga rayuwata kwankwasa kofa akayi dakyar ya amsa suka shigo zahra da Jidda xubewa sukayi kusa dashi kayi hkr ya khaleel xamuje mu dawo da ita shiru yai yana kallon pix din jenny yana sauraron su OK naji zahra ta mike Jidda ta matso kusa dashi ya dakatar da ita no no ! Tashi ki bita bana son hayaniya ta mike sweet heart kayi hkr kada ka fasa aurena naji naji jeki ta juya jikinta asnyaye ka janye mgnr ?, plx kitafi nace plx ya khaleel na janye shikenan ngd ta fada sannan ta fice ya saki numfashi I love u starshine

*************

Bayan kwna biyu

Tana kwance akan 3 siter tana kallon pix dinsu dashi nayi missing dinka Mr coffee ina sonka yanda kake so nayi ne baxan taba yi ba tana mmkin irin abubuwan daya ke nunawa takasa gane me yake nufi shin shima ba Santa yakeba ? Meyasa yake hana maxa su kulata xuciyarta ce ta tunasar da ita Mr coffee yana sonki kamar yanda kike sonsa yana kishinki ba a kishin mutun batare da soyayya ba yayi kissing dinki dariya ta kufce mata ta shafa lip din da yatsunta hkn yana sona kara taji na kida sosai da sauri ta mike hindu ce ta karo volume na wakar film din

fan tana rawa a kufule jenny ta dauki remote din ta rage da sauri hindu tace meye hakan ? Dalla bani bazan bayar ba tunda ba gidan shedanu bane sulthana ta fito daga kitchen hannunta rike da plate da acinci a ciki tace xaku fara ? Jarababbu kin San inda jarababbiya take mikewa tayi kada a kuskura a fada min a binda zai tunxirani dan zan iya aika aika hindu tace wanne sakaren ne xai xauna kiyi masa wani abun ? Tsaki jenny tayi ba mmk dan ke Yar masara mutunci ce OK naji amma ai ba arniya bace ni ko ? Hindu tace amma ke tabbatacciyar fitsararriya ce sulthana ta harari hindu harda au kaxa a cin danko Yar daba kawai hindu ta dauketa da mari dai dai lokacin da ya haisam ya shigo duka sulthana ta kaiwa hindu tsawa ya kwatsa musu haba kullum abu daya Ku xauna Ku sasanta kanku hawaye ya xubowa hindu al'amarin mu bana sasanci bane haisam kawai kai mana addu'a ta wuce daki sulthana ya haisam sannu da xuwa bari na kawo mk ruwa a a ki barshi ya fada hade da xama kusa da jenny jenny akwai matsala fa ? Ta kalleshi tame ? Har yanxu hnklin kowa atashe yake sbd batanki kiyi hkr ki dawo office zan wuce naga yakamata na karaso na fada miki kiyi hkr ki koma gida ya khaleel ko fitowa bayayi daga daki plx jenny kiyi tunanin abinda ya dace anjima zan dawo na mayar dake sukai sallama ya tafi

Jin ya ambaci khaleel yasa ta kasa jurewa ta kira suwaiba da murna ta daga oyoyo Jennifer kin barmu cikin wani hali ki dawo dan Allah hnklin kowa ya tashi Mr coffee ma duk sonshi da coffee sai da ya daina sha sosai abinci ma inna kai mishi baya ci kullum cikin fada kinga kuwa yanda hnklinshi ya tashi dadi sosai ya kama Jennifer ta kashe wayan xuciyarta na axalxalar ta akan ta koma gidan da sauri ta shiga daki ta janyo akwatinta dama tagaji da fadace fadacen su itada yan uwanta zata fice daga gidan sulthana tace ke kam baki da aiki sai yawo da jaka ba kyanan bakya cen ? Ke kuma baki da aikinyi sai gulma da shiga abinda bai shafeki ba nabar muku gidan jarababbu Ku cinye kanku hindu tace ala raka taki gona waxai damu tsaki jenny tayi ta fice cike dajin haushin su zama dasu yasa tazama masifaffiya

Bata bata lokaci ba ta iso gidan a cen garden ta hango shi xaune yana sanye da wando 3 quarter da riga blue gefenshi ruwan cway ne tunda ta shigo ya xuba mata ido taji dadin ganinshi kai tsaye falo ta shiga dukkansu suna xaune sunyi jigum ganinta yasa Momy ta mike cike da murna da farin ciki Jennifer ta fada hade da rungumeta ina kikaje ? Kika daga mana hnkl tunda kin dawo alhmdllh ruby ta dauki jakar kayanta muje daki kiyi wanka ki huta kanta akasa ta mike har daki ta kaita ruby idan kin gama hutawa muna falo ta fice ta kalli dakin yana nan yanda ta barshi bude kofar akayi ya shigo gabanta ya fadi ya rufe kofar hade da rungume hannayensa ya xuba mata kyawawan idanunsa masu Kyau da haske fuskarshi a murtuke

By
*Ummee Garkuwa*
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

45&46

Ya xuba mata ido yana kallonta ranshi abace cikin muryar tsawa kadan yace daga ina kike ? Shiru tayi kanta akasa , ya matso kusa da ita dago kai ki ban amsa , ina kika je ? Asanyaye ta abshi amsa gidanmu . girgixa kai yayi , naje gidanku Maman David tace bakije ba, gabanta ya fadi , tarasa ydda xatayi gashi ya tsareta da manyan idanuwansa,

Naje gidan yayata ne. Tabashi amsa tana addu'ar Allah yasa ya amince, ina kenan ?? Ya kuma tambyrta muryarta na rawa ta amsa

Hotoro, Ok dago kanki ki kalleni

A kunyace ta dago fuskarta kwarjinin fuskarshi yasa takasa jurewa tai kasa da kanta, hannu yasa ya dago da fuskar ta ta xubawa kyakkyawar fuskarshi ido, shima idonshi akanta yana kallonta , kin San irin yaran da suke barin gida batre da wani dalili kwakkwara ba ?? Kai ta girgixa masa, nop kiyi magana, Asanyaye tace bansani ba,

Kwafa yayi yaran dabasu da tarbiyya,

Xaro ido tayi atsorace

Daga yau in ba dady ko Momy ne sukai miki mgn kada ki kuma varin gidannan jina jina? Kai ta daga hade da fadin naji zan kiyaye, Yayi Kyau, ya saki fuskarta sannan ya xuba hannayensa a aljihu, ki kiyaye.

Inshaa Allah zan kiyaye,

Ya fice daga dakin tabi bayanshi da kallo tana murmushi hade da jin dadin ganinshi ta fuskanci ya rame kadan,

************

Dakinsa ya koma ranshi yai mishi dadi na ganin ta dawo gida ya ga abubuwa da yawa afuskarta, tayi missing dinshi, murmushi yayi kadan, kofar aka bude hade dayin sallama mmk ya kamashi ganin Wanda ya shigo hannu suka bawa juna, sagir ? Yaushe ka dawo ? Ba sanarwa? Dariya sagir din yayi, jiya na dawo,

Hamdala khaleel yayi kaxo a time din Dana ke bukatarka, xama yayi ya kalli khaleel man naga ka rame kadan me ya sameka, kallon sagir din yayi da mmk, rama ? Ya maimaita, kana mmk ne sagir ya tmbyshi hade da janyo laptop din khaleel ya bude pix din jenny akai, sagir yace wow, wannan wacece? Ina kasamo kyakkyawa haka ? Karka cemin komai akanta nasan da Jidda aka saka maka rana, plx khaleel ina kamun wannan,

Bata rai khaleel yayi bai bashi amsaba, ta hadu matsalar kawai karama ce, amma nayi mmkin ganin pix din nan sbd nasan wannan ba tai kama da danginku ba, aslima yanda nasanka banajin xaka iya son karamar yarinya, shiru yayi khaleel bai amsa masa ba sbd ya kulu, dago kai yayi ya kalli khaleel yaga yayi kutukutu, shekewa da dariya sagir din yayi lallai fuskarka ta tabbatar min da son yarinyar nan kake, ya kuma kallon pix din wow ! Kyakkyawar fuska manyan ido, karamin baki, ya isah haka sagir, bana son maza su dinka yaba min ita, bana so da mmk

sagir yake kallonshi, menene dan na yabi mai Kyau, ranshi bace yace ban hanaka ba itace kawai bana so ka yaba, rufe laptop din yayi, abokina me ya sameka ?? Jingina yayi da jikin kujera sagir ina son Jennifer,

Jennifer? Sagir ya maimaita, Kristen ce ita ? Suka hada ido khaleel ya daga mishi kai, haba khaleel duk matan Hausa Fulani ? No ! Sagir, ya daga mishi hannu, kasan hakan ba haramun bane, dan tana Kristen bazan ki aurenta ba addinina bai haramtamin ba, idan na aureta kamar nayi jihadine, ajiyar xuciya sagir yayi hakane khaleel, kwafa khaleel din yayi ba wannan bace matsalar,

Taurin kai gareta taki ta sanar min tana sona, da sauri sagir ya kalleshi khaleel wai har yanxu kana nan da wannan tunanin naka? Wani kallo khaleel ya wurgawa sagir, kana ganin zan canzane? Naja ra'ayin yarinyar sosai kuma tana sona taurin kanta ya hana ta fadamin, dariyar shakiyanci sagir yayi, khaleel wato kai na daban ne mgn daya kake baka canxawa, tayaya karamar yarinya xata yi maka abinda manyan big gals irinsu nabila, amatullahi, jidda, suka kasa ? Murmushi yayi ina son Jennifer sosai ban San yadda akayi hakan ta faru ba, bakayi mmkin fada maka hakaba? Wata irin dariya yayi sagir mmkin ne yasa nabawa zancen serious, wai shin ya akayi kake sonta ? Kai da kace sai dai mace ta soka ? Bazan iya tunawa ba kawai na tsinci kaina cikin tsananin sonta, itama tana sona bazan iya gane waye yafi son wani tsakanin mu ba,

Khaleel mafita kawai kacewa yarinyar nan kana sonta,

What ? Sagir ni din ?? Ina bazan iya ba banta ba yi ba bakuma zan fara akan karamar yarinya ba, kasani sagir ban taba cewa budurwa ina sonta ba su suke sona, ban yadda da wannan tsarin ba xuwa wajan mace kace kana sonta sagir babban raini ne, ka ja ra'ayin yarinya da dabaru taxo da kanta sbd takasa jurewa tace tana sonka shikenan, lol khaleel kana nan da halinka kai din na manyan yara ne irinsu Jidda, Nabila, wai ina Nabila ne ? Tsaki khaleel din yayi ina ga ko tana Singapore ne ? Meyasa baka son yarinyar nan,

Iska ya fitar daga bakinshi bazaka ganeba Nabila bata da kamun kai dalilin dayasa nake son jenny yarinya ce karama akansu bata kaisu ilmiba har yanxu a 0 label take wannan year din tagama secondary fa amma tafisu aji da kamun kai babu jan ra'ayin da man mata ba amma har yanxu takasa ce min tana sona yai tsaki bana son mace ta dinka hauka akaina koda tana masifar sona nafison ta dinka Jan aji haka nakeso, hakane khaleel wasu matan soyayya tana Sa su manta kansu, yanxu ya xakayi da auren Jidda ka Jennifer ? Gyara xama khaleel yayi yace jenny is too young kona aureta yanxu renonta zanyi, dariya sagir yayi ko kuma ita tare neka ba, dariya shima yayi kasan dai zahra itace autar mu ko ? To nesa ba kusaba ta girmi jenny, kaga dole sai reno, sagir ya buce da dariyar keta ina jiye mk abu daya ranar da yarinyar nan xata rikita ka, wani kallo ya jefa wa sagir anfada maka ni mayen matane irinka kajira kaga abin mmk nan da wata daya zata furtamin tana sona da kanta, wata dariyar sagir ya kumayi, ko kuma kai ka fada mata kana sonta ba, sagir bana son iskanci kaifa shege ne tayaya da girma na da ajina zancewa yarinya karama ina sonta ? Kana ganin xan sauya ne yadda nake ? Kaxuba ido xaka sha mmkina,

Sorry abokina yanuna idonsa wannan shine nawa, amma fa kasani soyayya ba'a yi mata alwashi,

Tsaki khaleel din yayi ya janyo musu wata hirar

***********

Bayan ta fito da ga wanka ta sauya kaya Momy tashigo dakin jenny kin shirya ? Eh Momy, OK in shaa Allah anjima malan Dr Ahmad Sani ningi xai xo kamar yadda muka tsara xai baki Kalmar shahada,

Wani dadi ya kama Jennifer, toh Momy ina jiranshi, tare suka jero suka sauko kasa babbn parlourn gidan suka xauna, Jidda da zahra suna aika mata harara, ta lumshe ido bata damu da kiyayyrsu ba sam dan tasan rayuwa baxta yiyu kowa ya sokaba dole akwai makiya, suna nan a falon suna hira jefi jefi ya khaleel yai sallama shida wani babban mutun gaba daya falon suka mike suka gaishe shi cikin farin ciki da fara'a ya amsa ya xauna yai sallama suka amsa masa,

Wacece acikin ? Suka nuna ta kanta akasa, baiwar Allah meyasa xaki musulunta ? Hawaye ya taru a idonta cikin rawar murya tace sbd nayi imanin shine addinin gaskiya sbd adalcinsu da mutuncinsu da taimakokon juna tun ina yarinya karama nayi imani da Allah na kuma yadda addinin musulunci shine addinin gaskiya,

Alhamdulillah, mungodewa Allah yanxu xan baki Kalmar shahada kafin nan zan fada miki rkunnan musulunci da kuma ahikanshi imani, addinin musulunci addinine na amince da salama da taimakon juna da kaunar junanmu, rukunann musulinci ya kasu kashi biyar Wanda dolene sai ka amince dasu xaka shiga addinin Allah

1 shahadatu an LA ilaha illalha wa'anna Muhammadan rasulullah

2 tsaida sallah

3 bada zakka

4 yin axumin watan Ramadan

5 da xiyartar dakin Allah .

A keeda ta muslunci tushenta shine imani da Allah, da mala'ikonsa, da littattafansa, da manxanninsa, da kuma ranar lahira, da yadda da akddara me Kyau ko mummuna

Lallai wannan magana da kika fadamin ta cewa tun kina yarinya kikai imani da cewar addinin Allah shine addinin gaskiya sai kika tunamin da hadisin manxon Allah (s.a.w)  daya ke cewa, maa min mauludin illa yuladu alal fidrah, babu wani abin haihuwa face an haifeshi da imani ga Allah, fa abawahu, har sai iyayensa yuhawwidani au yunassiranihi aw yumajjisanihi, sun kasnce yahudawa ko banasare ko majusawa,
Wannan ba abin mmk bane dan dan malaman tauhidi sun kawo wannan, fa inna kulla maklukin kad fudira alal imani bi kalikihi min gairi sabqi tafkeer au ta'alim, Allahu akhbar, haka Allah ya ke halittar kowa da imani dashi batre da wani tunani ko koyarda shi ba, Alhamdulillah, Alhamdulillah Alhamdulillah. Ikon Allah ya wuce komai dan shiyake shiryarwa kuma shi yake fidda haske daga cikin duhu, baiwar Allah duk kin amince da hakan ? Cikin gwarin gwiwa tace

eh Malan na amince, yai murmushi yace to Alhamdulillah, zan fada miki Kalmar shahada kamar yanda nai miki bayani afarko, duk abinda na fada sai ki maimaita Ash'hadu an la ila ha illallah ta bude baki da murna hade da imani harshen ta ya karye taji wani irin abu ya rufe mata ido da kyar tayi kokarin juya harshenta ta kasa bata San lokacin data mike tana kakari tana son maimaita wa gaba daayansu sukayo kanta luuuu tai kasa kafin ta karasa kasa ya khaleel ya riketa yana jijjigata dif yaga idonta ya rufe numfashinta ya tsaya cak cikin tashin hnkli suke jijjigata

By
  *Ummee Garkuwa*
For comments
08037251895
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

47&48

A matukar raxane ya khaleel yake jijjigata da karfi yana kiran sunanta Malan ya mike yana mmkin al'amarin ya kalli idonta yaga yana motsi yayi ajiyar xuciya naya dan yagane inda matsalar take dukkamsu hnklinsu na kanta musamman Momy da ruby, Malan ya kalli ruby yace taje ta debo masa ruwa acikin cuf, da sauri ta tafi, bata dabe ba ta dawo ya amsa ya yayyafa mata bayan yai mata addu'a har yanxu bata bude ido ba, numfashinta ya kawo da karfi idonta arufe yana motsi, Malan yace nayi mmk sosai Ku xauna, Ku kwantar da hnklinku xata tashi babu abinda yafi karfin addu'a xama sukayi xuciyoyinsu cikin dimuwa, har yanxu tana hannun khaleel yakasa sauketa gani yake yana sauketa wani abun xai kara faruwa da ita,
    Malan yace, dama tana da wata matsala ne ? Jikin Momy asanyaye tace gaskiya ban Santa da matsala ba Ify lau take, yayi Jim yana juya xancen yace to xata tashi inshaa Allah xuwa kuyi hkr idan ta tashi ta samu nutsuwa xamuji daga bakinta, kuma akwai wasu tambayoyi da xammata in shaa Allah xamuyi wa tubkar hanci, kada Ku damu, ya mike tsaye ya mikowa Ruby sauran ruwan addu'ar yace sukara shafa mata duk yadda ake ciki suyi waya kafin ya tafi sai da ya kuma yi mata addu'a ya khaleel ya dauketa, so Momy suka bi bayanshi ya sauketa a dakinta jigum sukayi hade da xuba mata ido ransu ajagule

Some hours letter

Har dare bata bude ido ba gaba dayansu suna dakinta kowanne ranshi ajagule haisam da

mahbobb duk sunyi cirko cirko kowanne da abinda yake sakawa uban gayyar kuwa ya rasa kalar tunanin da xaiyi addua'a yake xabgawa ubangiji Allah ya tashi kafadun jennynsa, Malan Dr Ahmad Sani ningi ya dawo, har dakinta sukaje, cikin mmk yace wannan abu da muni yake nayi mmkin rashin bude idonta, Momy tace wllh Malan babu me kwanciyar hnkl acikinmu, mun rasa wane kalan tunani xamuyi kan mu ya daure tamau kwata kwata jenny bata tabayin irin haka ba, wani irin tari Jennifer ta fara yi da atishawa me karfin gaske idonta a rufe take yinsu, hnklinsu yadada tashi addua malan yai mata sannan ta daina sai kuma hamma, girgixa kai haisam yayi Momy kuyi hkr akwai abinda muke boye muku nida Jennifer amma yanxu dolene kusani jenny plx ki gafarceni yaxama dole su mom su Sani sbd awarware matsalar jikin khaleel ya fara rawa wani kishi mai karfin gaske ya taso masa ya cikumi wuyan haisam cikin fada da tsawa yace me ye atsakanin Ku Wanda kuke boyewa ? Menene ? Araxane Momy ta mike cike da mmkin khaleel din, kana lafiya kuwa khaleel ? Kasa keshi, cikin fada da jin haushi yace mom plx ki kyaleni, tayaya xasu munafunce mu su kintsa wani abun batare da sanin mu? Kasa keshi nace ! Da karfi yasakeshi har sai da haisam yai baya, ran khaleel ajagule gani yake ko soyayya suke shida ita, to me sukeyi ? Wani irin yanayi Mara fisaltuwa yaji shi aciki,
Momy tace muna jinka haisam girgixa kai haisam yayi cike da jin haushin dan'uwansa ya kwashe Ibrin komai ya fada musu jinjina kai Malan yayi hade da fadin ikon Allah, kunga inda babbar matsalar take, lallai sihiri mai karfi na bata da kauce hanya hade da babaken jinnu ajikin yarinyar nan dole anemo sauran yan uwanta ayi musu magani gaba dayansu, wani irin shock khaleel yaji hade da danasanin cukumar haisam da yayi yana son jenny shi bakone asoyayya ya kasa controlling kishi mai xafi daya ta so masa, Momy tace amma haisam kunyi yarinta sannan kunyi kuskure, kuyi abu Ku kadai batare da sanin babba ba gobe dadynku xai dawo yanxu xan kirashi a waya na sanar dashi komai, ubangiji Allah ya kawo mana dauki wannan lamari da sarkakiya yake idan kana duniya xakaga abu kaji shi kuma kala kala,

Malan yace mutane ne iri iri marasa tsoran Allah da sai kaunar duniya basa taba tunanin xaman kabarinsu basa tunanin yaumul hisaab duniya kawai sukeso cikakken me imani ne yake tuna Allah adukkan lamarinsa Ku ga ikon Allah kuji wani xalunci, araba yaya har guda uku da mahaifiyarsu da mahaifinsu da danginsu a watsasu a duniya sbd bakin xalunci ba abarsu haka ba sai da aka jefesu da mugun sihiri na kiyayyen junansu ta tambadewa, innalillahi wa inna ilaihi rajiuun, an raba musu kawuna waccen a Dubai an hadata da bakin asirin daxata lalata rayuwarta waccen a saudiyya itama an hda ta sihirin rashin kunya wannan a 9ja an hada ta da kafuri, subhanallah, amma sbd kudura da kuma iko na Allah subhanahu wata'ala sai ya hada kawunan su duk da mugun sihirin da akai musu na har abada baxasu hadu ba, Allah kenan mai yadda yaso, ya girgixa kai fuskarsa cike da tausayin jenny ya kalli fuskarta, Allah kadai yasan halin da iyayensu suke ciki, musammn mahifiyarsu, Yaya uku ris ! Ita wannan yan biyu aka kwana arba'in aka rabasu da nonon mahaifiyarsu, bata gama ficewa daga radadin batansu ba ta kuma haihuwa still aka kuma sace yar, na tausaya musu duka daga su har iyayensu, ya mike xuwa gobe duk yadda ake cike na dawo kafin nan nasan Dr bashir ya dawo Allah ya bata lafiya, ya fice yana jinjina al'amarin suma haka suka tashi jikinsu asanyaye suka fita khaleel yana xaune awajan ya kura mata ido tausayin halin da take ciki da kuma soyayyar ta mai karfin gaske yake ji tana xagaye ilahirin sassan jikinshi da kyar yatashi ya barta hade da tofe ta da addu'a

**********

Karfe uku da rafi na dare yana xaune yakasa runtsawa alwala ya dauro ya fara jera na filfili zumbur ya mike hnklin nakan yaje ya duba ta ya kalli agogo ya girgixa kai ina dare yayi, tun yana iya jurewa har sai da yaji ya kasa ya fito daga dakinsa ya nufi cikin gidan bangaren inda take ya bude kofar dakinta xaune ya sameta tayi tagumi ya xuba mata ido, atsorace ta dago kai ta kalleshi wani irin sonshi taji yana ratsata ta sunkyar da kanta cikin sassanyar muryarshi taji yace ke! Dago kanki ta dago kai tana kallon kwayar idonsa da take fur babu alamun jin bacci atare da ita, akwai abinda yake miki ciwo?, sanin halinshi da tayi na bai son mgn da alama yasa ta budi baki da kyar tace ah ah

Sanyin dadi ya xiyarce shi baisan lokacin daya lumshe idanunsa ba, da sauri ya bude ya danci mur wai shi bai son raini, karta gane yana mugun sonta, kin tabbata? ya jefeta da tambaya, na tabbata ta mayar masa da amsa, asanyaye yace masha Allah, yakamata ki kwanta ki huta dare yayi sosai cikin wani yanayi na musamman tace tohh! Ya matso kusa da ita ya janyo bargon lullubarta ya kalli fuskarta, oya kwanta, ta kwanta ya lullubeta da bargo sannan ya fice ta murgudawa bayanshi kallo sannan ta runtse ido plx ya kahaleel kana son hauka tani da wannan salon naka, da kyar ta samu tai bacci

Tun kafin yakarasa dakinsa yake jin dadyn jennyn Sa ta farka yanayin daya ganta ciki tayi kyau duk da tana cikin damuwa oh ! Jenny ta musamman ce ! Komai nata na musamman ne ina sonki jenny plx kema kina sona ki daina wahalar damu kice kawai kina sona, baxan iya yadda kike so ba Sam ! Aa shiga daki nutsuwa ta musammna yasamu kansa aciki bai San lokacin da yai murmushi yasa hannu ya shfa sajensa a hnkl ya furta, nine mallakin ki ni zan mallake ki nafi kowa dacewa da in xama naki ina sonki jenny yana nan xaune har akai kiran sallar farko yatashi yai raka'atainil fijr sannan ya tafi masallaci

************

Washe gari gidan tsit babu annuahuwa kowa ka kalla a damuwa yake da kuma tausayin rayuwar Jennifer tana kwance adaki wayar ta tai kara bata son numb din ba ta daga muryar sulthana taji, oyoyo Anty jenny munyi missing dinki,

Cikin farin ciki tace nima haka, kuna Ify ? Hmm Anty jenny ba sauki,

Dariya jenny tayi sulthana kinsan me kikace kuwa ?

Tsaki sulthanan tayi cikin fada tace me nace ?

Murmushi Jennifer tayi naji kince Anty shiyasa nayi mmk,

Hello jenny Hindu ce

Oh ! Hindu kin amshi wayar ne ?

Da fada tace ko bakaya bukatar jin muryarta kinji nace nice sai kin wani maimaita taja tsaki,

Daga cen gefe taji sulthana tana cewa dallah Malama bani wayata idan kin matsu ki kirata da taki mana,

Hindu tace baxan kiraba da taki nai niyyar yi fitsararriya nan danan suka fara fada kashe

wayar Jennifer tayi hade da tagumi ita da yan'uwanta an maidasu makiyan juna koma waye yai musu wannan xaluncin bai kyauta musu ba, karara motoci taji da sauri ta tashi ta leka dady ya dawo ta fada hade da rike kirji komawa tayi ta xauna mutum adali mai tausayi da karamci

Bayan ya huta yasa aka kira masa Jennifer dan tun jiya yaji Ibrin komai yayi mmk hade da ta ujjibi kanta akasa ta sunkuya ta gaishe shi ya tambayeta ko tana jin wani ciwo a jikinta, tace ah ah, suna xaune haisam suka shigo shida su hindu da sulthana dady yace su hau sama kafin malan yaxo kaf gidan sunyi mmkin mugun kamar da sukayi da juna xuciyoyinsu cike da mmkin wannan lamari dakin Jennifer ta kaisu a ya tsine hindu take kallonta, kinji haushi jenny ki tare gidan mutane matsayin Yar aiki, kafin jenny ta bata amsa sulthana tace taxi Wanda yake yawon dabanci, akufule hindu tace, kema wata tarbiyya gareki ? Tarbiyyar da bakya ganin darajar kowa duk tsufan mutun yarone awajanki,

sulthana ta harareesu duka naji tunda ba dabanci da kwacen kayan mutane nake ba sannan ni ba arniya bace,

Kwankwasa kofa akayi khaleel ne ya shigo bai kallesu ba idonshi akan jenny, fuskarshi a daure yacewa jenny,

Kin shafa wannan ruwan addu'ar ? A a ta bashi amsa dauko ki shafa, toh tace masa batare da ta mike ba, nop ki tashi ki shafa yanxu ina kallo sbd yanxu malan zai dawo ta dauko ruwan tashafa a furkarta, yace yayi Kyau sannan ya fice, hindu ta tabe baki shi kuma wannan dan xafin kanfa ?

Sulthana tace sai wani hura hanci yake kamar barren soja amma fa ya hadu, hindu tace kirar jikinshi taimin kana ganinshi kasan yana ji da kansa ina son maxa irinshi cikin jin haushi jenny tace to malamai ya isa haka ! Murguda baki sulthana tayi wllh baxa a hanamu yaban me Kyau ba karar wayar jenny ce ta katse su Momy tace su sakko kasa dukansu suka sauko malan ma yaxo ga dady, malan yace sannunku bain Allah suka amsa da yauwa, Jennifer ya kira sunanta wanne irin mafarki kikayi jiya, a hnkl tace gani na nayi cikin wani katon rami, kina yin irinshi ko jiya kika fara ?

Tunda na mallaki hankalin kaina nake irin wannan mafarkin, da sauri hindu tace, wllh nima haka, irin shi nakeyi,

Sulthana ma tace nima haka irinshi na keyi, kafin ta karasa suka ga jenny ta dungura numfashinta ya dauke idonta arufe amma yana motsi da sauri sukayi kanta hnklinsu atashe daki suka kaita

***********

Malan suka kebe shida dady daya khaleel malan ya jinjina kai Dr bashir ! Yakira sunan dadi, akwai matsala gagaruma makarin sammun jikin yarinyar nan shine ta auri musulmi, gaban dady ya fadi shi kanshi khaleel wani mugun shock yaji girgixa kai malan yayi wani shedanin aljinine ajikin yarinyar nan baxai barta ta karfi shahada ba muddin ta auri musulmi xai kyaleta dan shi baya son aure asalima hana wa yake shiwa ? Dady ya tmby shi aljanin malan ya bashi amsa, dady yace toh malan yarinyar nan ba yata bace shari'ah bata amince da haka ba, a a Dr bashir malan ya katseshi a ina iyayenta suke ? Ba Wanda yasani, sannan lalura ce ta taso muhimmiya da kuma uxiri, xa ajira ne har sai anga iyayenta sannan xa a fiddata daga cikin duhu ?, in dai yarinya ta amince magana tayi sannan su marinka ba musulmai bane amma dole xa a fada

musu ajiyar xuciya dady yayi, yana jinjina lamarin khaleel kuwa tuni gumi ya jikeshi sharkaf, malan yace muddin kana da Wanda ka yadda dashi da kuma addiminsa da tarbiyyarsa a daura mata aure dashi, hakane malan ina dasu dan naga tasu taxo daya da mahboob Dana ba matsala na hadata dashi danna San baxata kiba hamdala malan yayi Allah yaska da alkairi Dr bashir kayi jihadi Allah ya biyaka murmushi dady yayi bakomai da na kowa ne shikam khaleel suman xaune yayi wani abu yaji me dafi da xafin gaske ya sokeshi da karfi jin an ambaci mahboob xa a. Bawa jennyn Sa 😭😭😭😭

By
*Ummee Garkuwa*
F[truncated by WhatsApp]
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

49&50

Girjin shi yaji yana xafin gaske tamkar ana babba ka masa wuta numfashinshi da kyar ya ke iya saita shi,

Malan ya cigaba da cewa, Dr bashir na jijina maka irinku mu keso Ku yawaita aduniya masu taimako dan Allah, masu jajircewa akan d'a koba nasu bane Allah ne kawai xai biyaka da mafificin alkairi bakomai malan shi d'a na kowane baxaka ki mutum ba koda yaka sance ba addininku daya ba, sbd bakasan gaba, malan ya mike xan wuce Dr duk yadda ake ciki muyi waya, amma maganar auren nan in son samune kada ya wuce satin nan, murmushi dady yayi cikin gwarin gwiwa bakomai malan ko gobene ashirye muke,
Shima malan murmushin yayi hakane Dr Allah yasanya alkairi, ka tamvy ta bakin yarinyar ko tana da abinda xatace, insha Allah xanyi haka nagd sosai, malan ya tafi yana zabgawa dady addu'a ta samun rahama,

Saukar da numfashi dady yayi ya kalli khaleel,

khaleel ? Yakira sunanshi, khaleel ya kuma maimaitawa a tsorace yata bashi hade da girgixashi khaleel ! Da kyar ya iya bude ido ya kalli dady, cikin raxana dady yace meya sameka ? Kirjina dady yana min xafi ina jin xuciyata kamar xata fito, subhanallah khaleel ! Sbd me ? Yanxu yanxu fa lfyr ka kalau, mikewa khaleel din yayi tamkar xai fadi dady natafi daki zansha mgn da kyar ya iya mgnr,
Dady binshi yayi da ido yana mmkin ciwon nashi yanxu yanxu ace ana tunanin xuciya kamar xata fito ya salam ! Meya sami yaron nan farat daya haka ?? Haka ya cigaba da tunane tunane ko xai danko dalilin cutar babban nasa daya keso tamkr namaa tsoka daya a miya

*************

Kai tsaye dakinshi ya wuce shi kadai yasan yadda ykeji aransa abude ya tadda dakin ya shiga

ciki a wahalce ya xauna kan 3 siter dinshi sai da ya xauna sosai sannan ya kula da sagir daye xaune yana kallonshi,
Sagir ! Yakira sunanshi, ya cije lebenshi xan rasa jenny ta,
Xaro ido sagir yayi, cike da mmk yace ban fahimta ba khaleel, da kyar khaleel ya bude baki cikin wani mugun yanayi na bakin ciki da bacin rai,
Dady xai bawa mahboob auren ta,
Subhanallah ! Sagir yace sbd me ? Ya tmby khaleel din daya runtse ido yanajin kansa kamar ana cakamasa kibiya, sbd yace tasu tafi xuwa daya,
Da mmk sagir yace to khaleel yanxu meye abinyi hnklina yatashi nikaina bana so karsa jenny, tsaki sagir yayi duk kai ka janyo wannan tashin hnklin taurin kanka ne yajamaka,
Kwfa khaleel yayi bana son fda plx kabarni naji da abinda nakeji shi kadai ya isheni, idan narasa jenny narasa dukkan farin ciki na rayuwata bana jin xanyi aure, dan konayi wacce na aura baxata taba jin dadin xama dani ba, kallonshi kawai sagir yakeyi dan ya kasa mgn, ina son jenny naso na aureta na reneta na bata ilimi ta goge da rayuwa har xuwa lokacin daxata mallaki hnklin kanta yanda xata iya rayuwar aure dani, da inaji ajikina jenny ta wace, yanxu tana so tafi karfina tayaya dady xai gane jenny itace mahadi na farin cikin rayuwata ? Dafe kansa yayi cikin mayuwancin hali har abada bazan daina son jenny ba,itace macen dana kalleta yanayi na sauya ita kadaice macen dana fara so har nake tunanin rayuwar aure da ita sagir kasan ya akayi jasan Jennifer?
Girgixa kai sagir din yayi,
Kwanciya khaleel yayi hade da tsirawa cillin din dakinsa ido

Ranar lahadi ne da yamma Momy ta ce ya kai wata abu Yar aikinsu kasuwa xatai mata siyayya bayan sunje yai parking dai dai bakin kasuwa wajan kofar gidansu inda mamansu take sai da abinci yana xaune cikin mota ya hango baban avokinsa da ya rasu xaune cikin rumfan murmushi khaleel yayi dan mutumin yana da matukar kirki tun suna yara abokin nasu ya rasu amma khaleel bai manta da shi ba dan yana xuwa gaishe ahi lokaci xuwa lokaci futawa yai daga cikin motar yana sanye da wando 3 quarter da riga maroon ta dan kamashi kadan hannun shi rike da mukullin mota yayo rumfar wajan Baban abokinsa ganinshi yasa mutumin yin dariya hade da fadin sunanshi, khaleel  d'ana kana duniya ? Dariya shima khaleel din yayi hade da sunkuyawa baba barka da yammaci,
Yawwa khaleel tashi ga benci nan xauna ya gida ya aiki ya iyayen naka? Mikewa yayi ya xaune hade da fadin suna nan lafiya baba,
Mashaa Allah khaleel har yanxu dai ba iyali ko ?
Kai khaleel ya sunkuyar hade da murmushi ankusa baba,
Af kullum amsar kenan ankusa ba, to ubangiji Allah yasa,
Khaleel ya amsa da amin
Shiru Baban yayi, duk lokacin Dana kalleka sai na tuna da khamis, Ubangiji Allah yaji kanshi da rahma,
Amin baba,
Karasowa tayi tai musu sallama suka amsa kan khaleel akasa bai kalleta ba ta mikawa baba plate na abincin daya siya ta juya xata tafi baba ya kirata, Jennifer xo ki tambayi khaleel me yakeso? Dago kansa khaleel yayi suka hada ido gabanshi yaji ya fadi da karfi wani abu yaji yam

tundaga kansa har dan yatsan kafansa da sauri ya sunkuyar da kanshi muryarta yaji me matukar dadi, me xa'a kawo maka ? Girgixa mata kai yayi hade da kara kallonta mmk sosai abin yabashi ganinta yayi adire kyakkyawa Sam batayi kala da sunanta ba aslima shi yafi ganin kamarta da Hausa fulani a hnkl a hnkl gaban nashi ya rage faduwa mmkin kansa yake baba na cin abinci yana mishi hira shi kam hnklinshi nakan sabon sauyin daya samu kansa ciki bai taba kallon mace duk kyanta da tsarinta yaji wannan yanayin yanayi wa mutane kwarjini yau shi akaiwa kwarjini yarinya karama hnkl ya kallo bangaren da take xaune akan benci cikin runfar nesa dasu kadan karantar yanayin da ta ke ciki yayi sbd ya karanci sanin yanayin halayyan dan adam tana da nutsuwa sannan tana cikin damuwa haka kawai yaji tausayinta ya kamashi, kwala kiran sallah akayi, araxane yaga ta kalli inda kiran sallar yake fitowa gaba daya ta bada nutsuwanta akan sauraren kiran sallar mmk sosai ya kama khaleel bai tsure da mmkinta ba sai da suka debi ruwa arumfar tasu shida baba suka fara alwala kura musu ido tayi tana kallon alwalar kana gani kasan alwalar birgeta tayi jinjina kai khaleel yayi ya mike Abu ya hango ta nufosu tagama siyayyar yace ta shiga mota ta jirasu xasuyi sallah xuciyar cike da mmkin yarinyar da kuma tunanin son taimakonta suka shiga masallaci

Bayan sun idar da sallah sun fito shida baba ya kira Jennifer xai biya kudin abincin daya ci da sauri khaleel ya xaro kudi ya tambayeta nawane kudin tace 500 ne ya bata 1k ta tafi kawo masa changy yace ta barshi baba yai gdy shikuma khaleel din ya shiga mota dai dai lokacin da Maman david takara so wajan baba Jennifer tace wai a bar changy? Gyda kai baba yayi bani na biya ba khaleel ne dan gidan Dr bashir na g.r.a xaro ido Maman David tayi, hee ! Baba meyasa baka kirani nayi gaisuwa ba ? A kamfanin babansu fa Baban David yake gadi kamfinsu na takalma ai mutanen kirkine baba, Allah ya saka angode ta wuce tana mmkin ganinshi ana sbd tasan dan manyan mutane ne

*****************

Wasa wasa kullum khaleel ya xauna bashi da aiki sai tunanin yarinyar nan ba yanda baiyi ba ya share ya kasa da kyar akai 1 week da kyar ya samu ya xakulo dabara sbd yaji daxu Momy tana anemo mata Wanda ya iya girki kafin bikin Abu yaxo da yamma ya shirya ya nufi unguwarsu kai tsaye rumfar Maman david yaje bai samu Jennifer anan ba sai Maman david din yatarar ga mamakinsa yana xuwa yaga Maman David da sauri taxo wajanshi dan ta ganeshi sannu da xuwa oga amsawa yayi sannan ya xauna ta gaishe shi da girmamawa ya amsa shima tace me xa a baka yayi Jim ya dago kai kenan ya hango almarai ya dan saki numfashi ya xaro Damin kudin ya mika mata abawa wayen cen almajiran da murna ta amsa bayan ta raba musu duka abinci ta kawo kudin wai sunyi yawa yace ta barshi da murna ta fara gdy ta xauna nesa dashi kadan ta hau surutu ai oga Allah yaska muku da alkairi irin taimakon da kukeyi megidana ma a companyn Ku na takalmi yake gadi ajiyar xuciya khaleel yayi dan yasamo mafita yayi murmushi kadan bakomai akwai mgnr dana keso muyi gyara xama tayi inaji,

Sunana khaleel Dr bashir,

Bude baki tayi da mmk Kaine khaleel ?

Daga mata kai yayi

Momyna tana son Yar aiki wacce xata dinka yi mata girki ko kina da wata hanya daxaki

mata naga kin iya girki sosai,
Washe baki tayi cike da murna sosai ma oga khaleel ina da hanya dan ina da y'a Jennifer itama ta iya girki sosai, Hamdala khaleel yayi cike da jin dadi, OK amma kafin nan naga cen gabanku kadan sun bude catering skul ko ? Inaso taje cen tayi training na 3 months kafin tafara aiki dan Momy kafin ta dau mutun tana kai shi catering yai training, jim Maman David tayi dan bata da kudin daxata iya biya mata hakan yakaranta a fuskarta yasa yaxaro damin kudi Wanda yasan yafi na catering din yawa ya mike hade da mika mata gashi aje ayi mata register, ta amsa tana xabga gdy

Wannan shine dalilin zaman Jennifer gidannan kuma tunda taxo na fuskanci tana sona tun ban yarda sonta nake ba har sai da na yaddarwa kaina ta tsunduma son jenny so kuma ba na wasa ba naso na aureta na maida ita cikakkiyar mace ya girgixa kai hade da cije lebenshi sagir kasan banta ba burin soyayya da karamar yarinya ba ? Babban burina shine auren mace wayayyiya wacce at least ace tagama degree dinta tasan rayuwa tasan menene aure, tana da cikakken hnklinta, bani da burin auren yarinyar da komai kai xaka koya mata ciki kuwa harda soyayya batasan yaxatayi ta farnta mk ba kana fishi da ita itama tana fushi da kai, dariya sagir yayi da sauri khaleel ya galla masa harara kaifa dan iskane dariya kakemin ?
Sorry abokina ina mmkin yanda akayi bakasan yaran yanxuba tarr suke ganinka abinda yaran xasuyi wata babbar baxatayi ba, tsaki khaleel yayi baxaka ganeba sagir !
Kayi hkr khaleel
Cije lebe yayi bakasan me nakeji ba Kalmar nan ta hkr da ka fadamin jinayi kamar ka Debi narkak ken ruwan dalma ka xubamin ajikina,
Wani irin xaro ido sagir yayi hade da fadin Allah ya kawo sauki

***************

Dady ya tarasu kaf mutanen gidan a babban falo harda su hindu sulthana da jenny yayi gyran murya yana kallonsu 1 by 1 shikadai yasan wanne irin yanayi yake jin kansa,
Alhamdulillah na tarakune anan dan mu tattauna gagarumar matsalar da muke ciki kan rashin lfyr Jennifer ya kalleta kallo na tausayawa Jennifer ! Yakira sunanta ta amsa kanta akasa mun yanke shawarar xamu auraar dake ga musulmi kan shawo matslarki kin amince ? Gabanta ne yai mummunan faduwa da sauri tace eh jikinta na rawa Hamdala dady yayi sannan ya kwshe yadda sukayi da malan yasanar dasu, kije kiyi tunani Jennifer idan kina da Wanda kikeso Wanda kika yadda da ingancin addininsa nan da xuwa gobe ki fadamin da kyar ta iya bude baki sbd nauyin d yai mata tace toh
Sulthana ce tace dady nima kaimin auren plx ! Da sauri hade da mmk dukansu suka kalleta murmushi dadi yayi sulthana ! Yakira sunanta kiyi hkr itama Jennifer kinji babban dalilin daxaisa ayi auren, dady nima myb in ammin auren matsalata ta yaye ka auramin ya haisam ! Dariya ta subcewa dady ! Ta shagwabe fuska plx dady ina sonshi, ki yi hkr akwai time in dai yana sonki lokaci kuma yayi tsab xan aura miki shi,
A a dady ko baya sona kai mishi auren dole dani, tsawa haisam yai mata baki da kunya ko ?

Wani kallo tai masa tunda kasani maimai cin me kk ? so kafasan bani da kunya name xaka tmby ni ita ? Kunya tayi yamma ni nayi kudu tafada hade da murguda masa baki girgixa kai dady yayi cike da tausayinta mace da akasani da kunya ita anxare mata ta ta da karfin sihiri, dady ta katse masa tunaninsa cikin fuskar tausayi ni nasan baxai soni ba ! Sbd bani da kunya ni fitsararriyace amma ina sonshi ni kaina bansan lokacin Dana ke futsara ba ta fashe da kuka me tsuma rai dady inaji dama babuni na tsani kaina kai da Momy ne kadai kukemin kwarjini amma koya kallo daya nake mishi da kaina, cikin matukar tausayawa Momy tace kiyi hkr sulthana kowanne mutun da irin kaddararsa in shaa Allah komai xai wuce kutashi kuje kuyi sallah ankira dukansu suka mike kowa da abinda yake sakawa aransa

***************

Suna kwance karfe 3 na dare sulthana ta tashi ta dauro alwala tana fitowa daga toilet ta kalli yan'uwanta su 2 da jenny da da hindu suna barci hnklinsu kwance wata kiyayyarsu taji me xafin gaske frige ta bude ta dauko ruwa me sanyi ta juye musu shi ajikinsu pirgit suka tashi ganin itace tai musu aikin yasa hindu ta mike a kule ubanwa yasaki ki xubamin ruwa ? Da kallon raini tace ubanwa yasaki ki mike kafa kina barci cikin kwanciyar hnkl kamar baki da wata matsala a rayuwa alhali kin fi ubanwa lowa matsla kitashi ki fada wa ubangiji bukatanku, da jin haushi hindu tace shine xaki tasheni da ruwan sanyi

Tsaki sulthana tayi ki godewa Allah daba tafashash she bane

Wanka mata mari hindu tayi

Wani kara sulthana tayi hade da kaiwa hindu duka da roban ruwan sanyin data tashesu, takaici ya kama jenny ta fashe da kuka hade da rufesu da duka dukansu suka kacamai da fadan gaske irin Wanda suka farayi daren ranar da suka dawo hotoro karar fadan nasuce ya tashi mutanen gidan dukansu sukayo dakin nasu hnklinsu atashe samun sukayi sun kacame da fada akai akai su rabu suka ki hnklin dady atashe ya kira ya khaleel yana xuwa ya kwatsa musu tsawa suka tsaya da fadan dady hnklinshi atashe yace meya hadaku cikin Daren nan ? Hindu tana haki tace dady wannan shegiyar futsararriyarce muna bacci ta xuba mana ruwan sanyi,

Cikin fada sulthana tace niba shegiya bace, kece dai shegiyar futsarariya,

Jenny ce wawuro center table din dakin kwara na kasheku na huta dan jaraba dadyna yana muku mgn baxaku daina ba,

Da sauri sulthana ta janyo lokar mirror din dakin wllh kina bugamin nima zan buga miki,

aguje hindu ta bude Jakarta ta xaro bindiga ta nunasu da ita wannan shine kuskuren da muka kara yi haduwa waje daya kun manta maganin da boka ya bamu muka xuba akofar wancen gidan bamu xuba anan ba wannnan magnin shiyake rage mana karfin kiyayyar juna nagaji ! Nagaji ! Kwara na kasheku na kashe kaina mu huta ta nuna su da bindiga

By
*Ummee Garkuwa*
[2/28, 6:41 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

51&52

A raxane dady yace hindu ! Menene haka ? Yan 'uwanki ne fa ? Ki ajjiye bindugar nan, ta kalli dady fuskar ta a daure tana xubda hawaye tace, dady baxamu gyaru ba, baxamu ga iyayenmu ba, ka barmu mu mutu mu huta, mutuwa itace kawai hutunmu, cikin fada khaleel yace, ki ajjiye wanann bindigar, kada ki kuskura ki harbesu, girgixa masa kai tayi yaxama dole kodan mu rabaku da wahala, jenny ta harareta ta rike kugu ki harba wayake tsoran baraxanarki ?? Dariya sulthana tayi hawaye na xubar mata amma kafin kiyi Harbin ki duba bulet din kiga xai isheki ?? Tayi tsaki kin San fanko ? To hk bindigar nan take, nida jenny mun kwashe bullet din mun watsa shi a toilet munyi flushing sbd shegiyar baraxanar da kikewa mutane da bindigar, sai ki harba mugani,

Sauke hannunta tayi, ta xauna gefen gado hade da ajjiye bindigar kusa da ita amma kun shammaceni banxaye barayi,

Jenny tace abinda kikeyi ne mukai miki, dan kece cikakkiyar barauniya,

Dady da sauran yan gidan kallonsu kawai suke suna mmkin wannan ikon Allah, sun fara cacar baki ya katsesu,

Tunda abin yxama haka zan raba muku wajan kwanciya xuwa gobe amma kafin nan ke hindu jeki dakin zahra ke kuma sulthana kije dakin rubayya,

Cikin shagwaba sulthana tace a dady ni dai dakin waccen me ji da kan xani ta nuna xahra naga tunda muka xo gidan nan take wani fusge fusge a dakin ki nakeso na kwana kikai min wani rashin kyautawa na miki dukan tsiya dan bani da mutunci, ta gallawa xahran harara, tsaki xahran tayi, tayi gaba kafin dady yayi mgn sulthana tabi bayanta, dady yace sulthana axauna lfy plx,

tace to dady karka damu,

Ajiyar xuciya dady yayi yabi bayansu da kallo Rubayya tace hindu, xo muje suka tafi aka watse akabar jenny ta rufe dakin ta rungume filow tana tausayawa rayuwarsu bata da buri arayuwarta yanxu irin ta musulunta taga iyayenta hawaye ya sauko mata ta runtse ido Allah ka kawo mana agaji Allah ka cikamin wannan burin nawa tasa kanta jikin filow yanda taga rana haka ta karashe daren bata runtsa ba

****************

Washe gari da safe misalin 11:00 malan ya kawo musu magunguna na karya sihiri kowanne iri Wanda shari'ah ta yadda dashi ya fada musu yanda xasu dinka amfani dashi dukansu amma banda jenny dake suma abin ya ishesu yana kawowa suka fara amfani dasu babban burinsu shine suga iyayensu

Da yamma suna xaune a falo bayan sun gama cin abinci hindu tace dady ina son mgn dakai ya kallete yana naxarin fuskarta ya fuskance ta tunda suka xo gidan nan Sam bata da nutsuwa ko da yaushe a cikin damuwa take, ina jinki hindu,

Dady narasa ta inda xan fara bin ciken inda iyayenmu suke,

Jinjina kai dady yayi ni kaina narasa ta ina xan fara, abinda yakamata muyi shine mu dogara da Allah mu mike tsaye mudage da ambatonsa da naiman daukinsa sbd Allah da kansa yace mu rokeshi xai amsa mana,

Jenny tace dady ko xamuje gidajen radio da jaridu,ko xa'a dace ?

Shiru yayi yana naxarin xancen,

Momy tace ganina wannan ba mafita bace, tayaya xa'a fara cigiyar ? Ace wacce ta yadda yayanta har 3 shekaru goma sha takwas? Ta ina xa'a sameta ? Hakan ma kamar jawo wata masifar ne sannan ga tonon asiri muddin yan jarida suka San da haka sun dinka yayata zancen kenan Ku xama abin nuni a gari kunya ma ta ishe ku,

Addu'a itace mafita ko ba'aga iyayen Ku ba ni Ku daukeni matsayin uwa dan ni tuntuni na maidaku yayana,

Sunthana ta fashe da kuka ta daga hannayenta sama dukansu suka kalleta da tausaya wa, ya Allah ya ubangijina gareka na dogara gareka na ke naiman taimako ya Allah kasa kafin na koma gareka Allah kahadani da fuskar mahaifiyata na ganta ta ganni, tana kuka sosai

hindu ta runtse ido hade da mikewa ta bar wajan,

Jenny ma kukan takeyi batason lokacin da ta fara fadin inaji ajikina xan hadu iyayena amma narasa ta ina ta wacce hanya ? Mikewa itama tayi ta bar sulthana anan tana kuka,

Kai tsaye dakinsa ta nufa tura kofar dakin tayi ba sallama ya dago ya daka mata tsawa, baki iya sallama ba ? Juya wa tai tayi sallama ya amsa ta shigo yana xaune kan 3 sitter yana kallon labaran BBC ta xauna akasa kusa da kafarshi tana murmushi ya khaleel naga baka ci abincinka ba shine na xuvo na kawo maka, idonshi akan tv yace ok, tashi tayi ta xauna kusa dashi sosai kanta tasa akafadarshi, matsa ! Yace mata da mmk ta dago kai taki matsawa ya waiwayo fuskarshi adaure kafin ya kuma mgn ta sauka ta koma inda take ajiyar xuciya tayi ranta ya baci sosai, ya khaleel nai maka laifine ? Meyasa baka kula dani ? Kodayaushe cikin gwasaleni, plx aure fa xamuyi kasani ina sonka banason narasa, idan nai mk laifi kayi hkr tunda nabar gidan nan nake cikin tunaninka kwatsam naji Ibrn aurenka da Jennifer, nasan ba tsarinka bace sbd bakason k'aramar yarinya sannan gata Mara asali duk da naji ance ta musulunta ko kadan bata dace da kai ba waya sanima ko shegiyace,  tsawa ya kwatsa mata ke ! Idan cin mutuncin matata xakiyi tashi kibar min daki, wani irin kallo tai masa da nanata mgnr shi "matarka ?

"Tana da asali kada ki kuma sheganta ta ki girmamata tunda ni take aure, kamar ta fashe da kuka Dan takaici haka ta daure ta janyo wata hirar ta daban

Kasa jurewa tayi
afusace ta fito daga dakinta tai b'angaren ya khaleel xuciyarta na tunxirata cak ta tsaya da sauri ta koma daki silent makeup taiwa fuskarta ta nufi kitchen ta hada mass coffee ta nufo b'angarenshi sallama tayi ya amsa tashigo jidda na kusa da kafarshi, taji dadin ganinsu a haka dan sun yi nesa da juna, ta ajjiye coffee din ta cire hijab dinta kai tsaye bed room dinshi ta wuce ya bita da kallo yana mmk dan baiyi tunanin xata kawo masa coffee ba, jidda xuciyar ta kamar tayi bindiga ganin ya khaleel yana kallon jannat yasa ta k'ara jin haushi fitowa tayi hannunta rik'e da rigarsa sbd farar singlet ce ajikinshi ta k'araso kusa dashi tana k'ok'arin saka masa yaji dadin kulawar ta shiyasa ya tayata Sa rigar taxauna kusa dashi ta xuba masa coffee din ta miko masa ya amsa yana sha, ta dauki remote, ta canza channel ta kaishi zee tv akwai series din da suke yi mai kyau, mmk ta bashi yanda yaga tasaki jiki sosai yau adakin shi sab'anin da datake a d'arare, wani mugun kallo jidda take binta dashi, tsam jannat ta mike dan tagaji da Harar da jidda take mata hawa kan kujerar tayi tasa kanta akan cinyarshi tana kallon tv lumshe ido yayi ya ajjiye coffee din hannunsa kamshin turaren mai dadi ya shaka yasa hannu yana shafa kashin kanta tayi matuk'ar birgesa yanda ta nuna msa kulawa, jidda kasa jure kallonsu tayi ahaka tayi mmkin yanda k'aramar yarinya ta d'auke hnklinsa da sauri ta mik'e xata fita, shi sam ya manta da ita futa tayi afusace, ya tabe baki

By
*Ummee Garkuwa*
[2/28, 6:42 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

59&60

Shiru sukayi kowacce da abinda take sak'awa aranta,
Abin ya matuk'ar d'aure musu kai,
Sulthana ce tak'atse shirun,
Y'an uwa menene abinyi ? Abin nan ya bani mmk ni sam ban yadda da maganar wannan mai k'asumbar ba,
Hindu ta kalleta nasan osasa abokin mariki nane na yadda da abinda yace sosai sbd nasan wanene shi,
Ajiyar xuciya, tayi kudin daya nema ne bamu dasu ko Rabin su ma ni banda shi,
Ni abin ya isheni wllh, takarasa maganar da hawaye,
Gyda kai sulthana tayi kiyi hkr sis hindu ko mai yayi xafi maganinshi Allah ni kaina narasa me yake min dadi nakuma rasa mafita,
Sukayi shiru dukansu xuciyar kowacce tana kuna hade da sakawa da warware wa basu da mafita basu da yadda xasuyi,
Jannat ce ta katse shirun da sukayi,
Mudage da addu,a mu cigaba da fadawa ubangiji Allah yana kallon kowa yana kallon xuciyar kowa Allah ya kawo mana dauki Allah ya baiyanar mana da iayayenmu, dukansu suka amsa da amin,
Hindu tace plx sulthana kada ki fadwa kowa xancen nan, koda kuwa dady ne ko Momy
Da sauri ta kalleta sbd me ?girgixa kai tayi muyi tunani plx, bayin Allah nan suna iya bakin kokarinsu wajan taimakon mu da kyautata mana kada mu k'uresu, kud'in da osasa yafada sunyi yawa, mubar abin iyakarmu tunda mu ya shafa,
Sulthana tace gaskiya sunyi mana taimako sosai sun maida mu yayansu sun d'auki damuwarmu sun maida ita tasu wannan kam dole mu b'oye,
Jannat tace hakane sis idan suka san zancen d'aga hnklinsu xasuyi, akan xasu bashi kud'in kuma sunyi yawa, addau itace mafita Allah yaka womana k'arshen wanann masifar,
Ku tashi mu shirya kada dare yai mana asanyaye suka mik'e kowacce tana jin d'aci aranta ta na kuma d'okin sanin suwaye iyayensu haka suka gama kwashe kayan babu wacce taiwa wata mgn acikinsu akan haryarsu ta komawa ma haka sukayi xugum babu hirar kirki sai sak'e sak'en xuciya,

Gab da magruba suka dawo gida jikinsu asanyaye alwala suka dauro sukayi sallah jannat ta dad'e tana xuba addu,a akan Allah ya kawo musu mafita, bayan ta idar da sallah tayi jigum ad'aki tana tune tunane har akayi isha'i ta mik'e ta yi sallah had'e da yin adduar data saba tana idarwa ta kishingida bacci ya fara daukanta k'arar wayanta ne ya tasheta, tana dubawa taga Mr coffee ne tasan abinci yake jira takai masa kafin ta daga wayar ta katse da ta tashi ta tashi kitchen ta d'eba masa abiincin Sa ta had'a masa coffee ta nufu b'angarensa,

Sallama tayi ta shiga yana kishingide jikin kujera yana sanye da 3quater jikinshi ba riga yana kallon labarai kallo daya tai mishi ta kauda kai,
Ajjiye kayan tayi tana kokarin xuba masa coffee,
Ke" ta kalleshi,
Ki cire hijabin,
tarasa meyasa kullum taxo sai ya ce ta cire hijab dinta, ba yadda taso haka ta cire hijab din kanta ba dankwali sai fakin din gashinta da tayi ta xauna, ta dauko cup ta xuba masa ya amsa yana sha tana xuba masa abinci karar wayarshi sukaji da take a bed room dinsa,
Ya kalleta kadan,
" tashi ki dauko min, a hnkl ta mike ta nufi bed room dinshi ya bi bayanta da kallo yana mmkin kyawun dire datake dashi,
Lumshe ido yayi a hnkl ya furta jannah kina da tsari da halitta me Kyau ngd wa Allah daya mallaka min ke,
Ta dawo hannunta rik'e da wayr ta mik'a masa ya xiro hannu xai amsa hannunsu sukayi karo da juna yaji hannun laushi kamar auduga ya amsa ya duba, Jidda ce d'an k'aramin tsaki yaja ya ajjiye wayar,
Mikewa tayi xata sa hijab, ya dago kai yana kallonta,
Muryarshi asanyaye,
"Ina xaki ?? Ta kalleshi suka hada ido,
" daki zan koma,
Xauna muyi mgn,
Xama tayi tana kallon kafet din dakin,
"Daxu ina kikaje ??
Da mmk ta kalleshi,
Hotoro mukaje ban ma je gidan Maman David ba,
" da ixinin wa ?
Xaro ido tayi tana mmk, da ixininka mana, na tambayeka kuma ka mince,
Girgixa kai yayi,
Bana son yawo tafiyar bata da amfani, ni ban San kin tmby niba,
Ranta ya baci ta bata rai, idonshi akan tv yana shan coffee yace baki fadamin xakije hotoro ba, daga yau ma babu inda xaki k'ara xuwa, kina ji ?
Turo baki tayi batare da ta amsa ba,
Waiwayowa yayi yana kallonta ta hada rai ta turo karamin lip dinta, ya tsurawa lip din ido yanda sukai Kyau,
Ajiye cup din yayi ya janyo ta kusa dashi,
"Bakiji abinda nace ba ?
Asanyaye tace,
Naji " sbd ya tsura ta da manyan idanuwansa sannan yana gab da ita hannunta cikin nashi yana murxasu a hankali, ta marairarice tana k'ok'arin fusge hannun, daya hannun nasa yasa yashafa karamin lip dinta,
Ta matsa tana kokarin tashi, ya kalleta,
Ina zaki ?
Turo baki ta kuma yi, daki xani bacci nakeji,

Da hannunshi ya dawo da ita kasa, kamar xatai kuka tace plx ya khaleel ka sakeni.....kafin takai karshe taji bakin ta cikin nashi yana shansu da sauri sauri kamar yana shan alewa, tayi tayi ta kwce kanta ta kasa sbd ya rike ta gam ajikinshi, ya Dade yana shan lip dinta sannan yasaketa hade da tsura mata idanuwa, yana mata kallon yarinya amma tsarin dirinta yana Sa yana jin feeling dinta, ganin ya saketa yasa ta mike da sauri xata fice sam ta manta hijab dinta,
Daukar hijab din yayi hade da mikewa yabita bakin kofa dashi dakyar
Yace, "karbi hijab dinki, ta miko hannu xata amsa ya rike hannun gam tana kokarin fisgewa ya janyo ta jikinshi da karfi kamar xai tura ta cikin cikinshi jinta ajikinshi yasa yai ajiyar xuciya yana jin tamkar ana kara masa soyayyr ta, ahnkl ya xamota daga jikinshi, itakam duk ta rude jikinta sai rawa yakeyi ya kalleta ta sunkuyar da kanta kasa ya dago da fuskar suka kalli juna,
Asanyaye yace mata,
" kifad'i abinda ke ranki?
Da mmk ta kalleshi ta kasa kauda idonta sai da tace masa "me kakeso nace?
Hannunshi biyu yasa ya tallbo fuskarta,
Abinda kike boyewa arnki, ya kalli kirjinta yanda yaga yana bugawa yai ajiyar xuciya baiyi tunanin ta kai haka ba,
Tureshi tayi, sbd jin haushin mgnrsa, da fada tace masa, wanne àbu nake boyewa ?
Cikin ko inkula yace yace, Wanda kikeso,
Runtse ido tayi mgnr ta mata zafi har yanxu yana nan da wannan tunanin ? Dole kam ta sauya Dan taga abin xai wuce gona da iri,
Rike kugu tayi tana kallonshi, ni babu Wanda nakeso babu kuma abinda nake b'oyewa,
Aurenka kuma bani na xab'a ba kusan dolenshi ma akaimin, ta juya ta bude kofa ta fice hade da yi masa Harar sama da k'asa
Wani mugun mmk ne ya kamashi ya xauna yana nanata xancen,
" kusan dole akai mata ?
Gaba daya yaji kanshi wani iri ta bashi mmk baiyi tunanin ta iya tsiwa hakaba,

Da matukar jin haushi ta nufi bangarenta ta kwanta tana mmkin halin khaleel haushin sa sosai ya kamata ta gaji da wannan rainin wayon, kallonta kawai yake bai sonta ba,
Tsaki taja xaka sha mmk na, ta kwanta ranta abace cike da jin haushin shi,

*****************

Washegari da rana suna dakinta inda suka saba zama suwaiba ta shigo sbd tana koyawa jannat karatu, bayan sun gaisa, sulthana ta kalli hannunta da mmk tace suwaiba ina son henna waye yai miki ?
Zama suwaiban tayi tana murmushi ni nayi sulthana, wow ina so kiyi mana nida Anty jannat banda waccen ta nuna hindu Dan ko kin mata ba Kyau zaiyi ba, kin ganta cen duk itace mummunar mu,
Dariya sukayi banda hindu datake hararar sulthana, da dariya suwaiba tace haba duk kamarku daya ni kaina da yanayin shigarku nake tantance ku, Baku da banbanci, bari naje na hado kayan kunshin in dawo,

Bata dade ba ta dawo tai wa sulthana me Kyau sannan ta fara yiwa jannat ana gama mata na hannu wayarta tai kara hindu ta dauka ganin Mr coffee yasa tace jannat waye kuma Mr coffee? lokaci daya sukayi dariya da suwaiba, kar ta katse fa " ajjiye kwai hindu tunda lalle ne a hannuna haka wayar tai ta kara har ta tsinke sai wajan 4:00 tagama musu lallan mai Kyau dake gwana ce suwaiban ta kware sosai yayi Kyau

Toilet tashiga tai wanka kafin ta fito suma sun tafi wankan ta dakko kayan daxata Sa ka English wears ne murmushi tayi da ta kalli kayan yayanta Emanuel ne dayaje jos ya siyo mata su atsaraba satin da xasu shiga wannan wahalar rayuwar bata taba Sa kayanba body hock ce pink me karamin hannu da siket dinta bai karasa sauka kasa ba sun mata Kyau sosai ta tsaya gaban mudubi tana taje kanta bude kofa akayi ta xaci su sulthana ne ganin shi tayi cikin madubin ta hade rai tai kamar bata ganshi ba ya xuba mata ido Hannunshi sanye cikin aljihu,
"Bakiga miscalled dina ba ?
Banxa tayi dashi kamar bata jiba,
Mmkinta yake, bakyaji ina mgn ? Ya fada da fad'a,
Ya b'una fuska tayi mgnr takace bata da amsa,
Kadan yarage yasaki baki sbd mmk,
Mikewa tayi tana gyara xaman siket dinta, ya karewa shigar ta kallo tai mata Kyau ya kalli kirjina gabanshi sai da ya fadi,
Adake yace meyasa baki daga ba ??
Far tayi da ido "sbd bani da abinda zance,
Ta gama kaishi karshe a mmk tambayar kansa ya fara yi dama haka ta iya tsiwa ?
Har ya juya xai fita sai kuma ya dawo hade da fincikota, jikinta na gogan nashi idonta kir akanshi, ki kawo min coffee dakina ina jiranki, fincike jikinta tayi ta kasa sbd bakaramin riko yai mata ba, shiru tayi tana kallonsa, da tsawa yace ko bakiji ba murguda baki tayi, da mmk ya saketa lallai yarinyar nan ta shammaceshi, ta koma nesa dashi, ya fice daga dakin, tayi dariya ta cigaba da taje gashinta, mutun sai kafiya da riqak'k'en ra'ayi taja karamin tsaki

******

Ya kalli agogan hannunsa 11:30 ya furxar da huci me yarinyar nan take nufi ? Kodan taga yana hada jikinshi da nata ? Tun kafin magrub yace ta kawo masa coffee har yanxu bai ganta ba ? Dalilin daya Sa baison yarinya kenan dafe kanshi yayi idanfa yayi sake rainashi xatai shi mutun ne da baya son raini shiyasa ko k'annan sa baya wasa dasu xabura yai ya mike ya fice daga dakinshi kai tsaye bangarensu yayi yashiga dakinta tana kwance ta na bacci ya kalli beauty face dinta tayi kyau da baccin, tsura mata idanuwansa yayi yana kallonta, a hnkl ya xame bargon jikinta ya kalli hannunta dayasha lallai mai kyau yashafa hannun sbd yana matukar son lalle motsi tayi ya cire hannunsa ta juya daga kwanciyar ya kalli gashin kanta cikin sha'awa yakai hannu ya shfa kan, xabura tayi ta mike idonta taf cike da bacci ta galla masa harara menene haka ? Hada rai yayi ban sani ba ya mike tsaye, daxu nace ki kawomin coffee meyasa baki kawo ba ? Ya b'una fuska tayi "mantawa nayi ta fada tana gyara kwanciya, jannah ! Ya kira

sunanta da tsawa har sai da ta tsorata,me kike nufi ne amarairaice tace kayi hkr plx bacci nakeji,
Mantawa nayi,
" kinga bana son musu ko gardama kina jina ya fada hade da xare ido, na kyaleki sbd yau kika fara kada ki kuskura ki kara maimaitawa, ya fice daga dakin ajiyar xuciya tayi hade da hararan bayansa, idan baxaka canxa ba ya khaleel nima yanxu na fara ta juya ta cigaba da baccinta,

Da safe bayan sunyi breakfast suna hira ga al'adarsu, muryar Jidda taji tayi sallama suka shigo ita da mamanta da gudu zahra ta rungumesu gaban jannat ya fadi tasan wannan xuwan ba alherine ya kawosu ba

By
*Ummee Garkuwa*
[2/28, 6:42 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

63&64

tabe baki yayi yana jin dadin fitar tata tana ganin ta fice ranta ab'ace taji dadi sosai dama tayi hakanne dan ta bata mata rai ta dago kai suka hda ido ita da shi ta b'ata rai ta sauke kanta a hnkl ta xame kanta daga cinyarsa ta mike ta dauki hijab dinta ta fice kallonta kawai yayi hade da lumshe ido yau kam tabashi mmk yanda ta nuna ta damu dashi

cikin jin dadi ta kai flast din kitcean ta nubo bangaren su afalo ta sameta, ganinta yasa jida ta mike taxo gaf da ita xata wuce ta fisgo hijab dinta, fisge hijab din jannat tayi tana kallonta, hararta tayi mara asali wacce aka watsar da ita a bola, kina gadarar cewa khaleel mijinki ne ? auren na kaddara har aurene baya sonki ba kuma xai taba sonki ba dan ya khaleel yafi karfin ki yar matsiyata mara
asali waya sanima ko shegiya ce, tafiyar ta tayi ta kyaleta tana jifan ta da maganganu na cin xarafi daki ta shige xama tayi akan gado xuciyar ta na kunan maganganun da jidda ta yaba mata hawaye masu daci suka xubo mata cikin kuka take magana, dan kawai Allah ya jarabcemu shine muka xama abin gori ,meyasa mutane basa gane kaddara? sun manta Allah shiyake tsarawa bawa rayuwa ba ba bawane yake tsarawa kansa ba ?? hannu ta daga ya Allah ya ubangiji ka kawo mana agaji Allah kanuna mana iyayenmu kuka sosai takeyi, nagaji da wannan cin mutuncin jidda dole na dau mataki baxan iya jurewa ba ko ada ina kyalekune saboda aiki nake muku yanxu kam yayanki nake aure bazan iya ba dole na dau mataki

*********
washegari da safe ta fito daga wanka hindu ta shigo da breakfast dinsu sulthana na biye a bayanta, ta kallesu anan zakuyi breakfast din ? kai sulthana ta daga mata waccen masifaffiyar matar ta hakimce a dining area tana ta muxurai shine momy ta kawo min tace muje sama muyi breakfast din,zama jannat tayi hade da tagumi,sulthana ta kwashe da dariya anty

jannat ki kwantar da hnklinki wllh duk da tana takamar ita kanwar dadyce gidan dan'uwanta ne idan ta kuskura tace zata kara takamu nima sai na takata dan bata da girma a idona bazan iya jure cin mutunci ba dan ma nayi sauki sai na nuna mata kuskurenta, hindu ta katseta, haba sulthana matar nan fa ba sa'arki bace kodan darajar dady ki kyaleta plx dan Allah muna xaune lfy kada kija mana tashin hnkl duk masifarta nasan ba dadewa xatai a gidan nan ba, hararar hindu tayi idan xaki iya jurewa ki jure nikan wllh bazan iya ba ita tasan ba sa'ata bace take janmu da masifa ta xubar da mutuncinta nasa kafa na take, jannat ta kalli sulthana any'a kuwa kina shan mgninki sulthana ? ina sha sosai naga canji bakuyi mmkin jiya ban rama abinda matar nan tai mana ba ?? plx anty jannat sauko miyi breakfast a hnkl ta sauko tana tausayawa kansu na rashin sanin iyayensu,
bayan sun gama breakfast hindu tace jannat dama jidda budurwa ya khaleel ce ? kai jannat ta daga mata,sulthana tace jiya ruby take bamu lbr wai har ansa musu rana,tsaki tayi hanji dadi ba ko kadan, anty jannat naso ace ke kadaice matar khaleel banso kiyi kishi da tsohuwar guxuma irin jidda, murmushi jannat tayi dole ne sulthana sbd an dade da sa musu rana,addu'a xaki mana Allah ya bamu zaman lfy,test ya shigo wayarta tana dubawa taga ya khaleel ne...... ki kawo min breakfast..... ajjiye wayar tayi ta kyaleshi

*********

karfe 3:00 na rana suna xaune a falo jannat tana cikin daki haisam ya shigo, sulthana ta bata rai tai kamar bata ganshi ba xama yayi yana kallon tv da suke kallo, ya kalli sulthana ya ga ta bata rai, ya fuskanci kwana biyun nan ta daina kulashi, sulthana ba gaisuwa ? bata kalleshi ba tace ya kk ? murmushi yayi lafiya lau nake naga kin canza ko wani abun akai miki, murguda baki tayi wai kai ya kk so nayi in yi mgn kace bani da kunya sannan nayi shiru kana tmbyr me akaimin ina ruwanka da shiruna ? murmushi yayi ya mik'e bai ce mata komai ba ya fice, ta harari bayansa hade da yin kwafa, yana fita ya khaleel ya shigo dai dai lokacin da jidda take saukowa da ga upstairs ganinshi yasa ta karaso da sauri, gab dashi taxo sannu da xuwa ya khaleel, yawwa sannu, rubayya ki kawo min lunch dina daki, da sauri jidda tace ta bash shi zan kawo maka, ok yace ya fita kitcean ta wuce, sulthana ta tabe baki ta hau sama ta tadda jannat na karatun kur'ani, ta ajjiye kur'anin ta mike tana kallon sulthana, wani kallo takewa jannat din wai meya sameki ? ga shi cen waccen muciyar ta tafi kaiwa mijinki abinci tana matsayin budurwar shi idan kika tsaya sanya xata fiki daraja ni banga amfaninki ba keda mijinki ki xauna wata cen budurwar shi ta dinka yi masa hidima ? ki nemi dabara dan wannan ba ta dace da ke ba, ta fice daga dakin jannat tabita ta kallo hade dayin ajiyar xuciya, sulthana bakisan halin ya khaleel bane canza kaya tayi tai makeup ta fesa turarenta mai kamshi ta nufi kitcean ta hada masa coffee tai bangarensa sallama tayi ya amsa hade da galla mata harara, yarasa gane ina yarinyar nan ta dosa kusa dashi ta anjiye coffee din ta cire hijab dinta kamshin turarenta dayake so ya shaka ta xauna kusa da shi jidda na cen gefen ranta amatukar bace, ta gaishe da ya khaleel ya amsa yana danne dannen wayarshi miko masa coffee din tayi duk da yana fushi da ita haka ya amsa  dan baya iya yin xuciya dashi, sannu ya khaleel ka gaji ko ? gama shan coffee din kaci abinci in maka tausa, araxane jidda ta kalleta shima mmk ne yasa ya kalleta yarinya sai kace mai aljanu kullum da salon daxata bullo dashi shi sam bai gane dan jidda takeyi ba,

ya harareta kadan dauko waccen ledar ya nuna mata leda nesa dasu da sauri ta mike tana tafiya a hnkl ya bi ta da kallo ya lumshe ido, jannat kina da tsari da xubi mai kyau hawaye ya saukowa jidda ganin irin kallon daya kewa jannat da sauri da goge hawayen, ledar ta dauko ta dawo kusa da shi ta ajjiye xama tayi ta bude ledar English wears ne masu kyau, da murna tace ngd sosai Allah yakara budi rufe mata baki yayi da hannunsa bana son gdy hannunta tasa ta riko hannunsa gam tana dariyar farin ciki Allah ya saka da alkairi ya tsareka da ga sharrin mutane da aljanuma, yaji dadin adduar ta hade da mmkin tulin yarintar ta, sakin hannunshi tayi, jidda ta mike tamkar xata fadi kasa da kyar ta fice daga dakin murmushin jin dadi jannat tayi aranta tace kadan kika gani idan baxaki daina shigowa dakin ya khaleel ba tana futa tafara tattare kayan ta xuba su a leda ta mike xata fita ya fisgota jikinshi, meyasa daxu baki kawo min breakfast ba ?hade rai tayi tace, sbd banyi niyya ba kara matseta yayi ajikinsa ni kike fadawa mgn son ranki matsar taji tayi yawa, a a ya hakuri plx dan Allah kasakeni, banza yai da ita yana jinta cikin jikinshi yana jin dadin kamshin turarenta dayake shak'a kuka tasaka sannan ya saketa ta dauki hijab dinta tasa dai dai bakin kofarshi ta tsaya bazan kara xuwa dakin kaba, yanayin yanda tai mgn cike da yarinta murmushi yayi har  hkrnsa suka fito yanxu kam yarintar ta birgeshi takeyi tana kokarin fita ya riko ta kwabe fuska, "me kikace ? shiru tayi tana kallon gefen shi kamar xata fashe da kuka, baxaki kara xuwa dakina ba ko ? to babu inda xaki nan xakiyi ta zama,  zaro ido tayi hade da kwabe fuska, kayi hkr ya khaleel, lip dinta ya kalla ganin yana kallonta yasa ta bata rai plx zan tafi daki ka cikani, kafin ta karasa taji bakin ta acikin nashi ya riketa gam yadda baxata iya motsawa daga rikon da yai mata ba sai da yagaji dan kansa ya saketa ta juya aguje ta fice ya bi bayanta dariya ta subuce masa cikin jin dadi ya xauna shi kam da baya son yarinta yamxu kam yarintar jannat birgesa take tana kuma sashi nishad'i

***********

da sauri ta nufo bangaren su jidda ta hango idonta sunyi jaa tana kara sowa hijab dinta ta kuma fincika, tsaki jannat tayi tana mata kallon sama da kasa, ganin irin kallon da jannat din take mata yasa tace iyye sannu yar matsiyata kinxo gidan arxiki kin bude kafa kina cin maiko har kin auri d'an masu gida, kinyi kuskure Jennifer sai kinyi danasani kina tak'ama da auren shi kike shiyasa kike min gadara to wllh sunan aurenki matacce, tab'e baki jannat tayi wannan ne kuma baki isaba sbd Allah shiyake da ikon komai ba wani ba,  sannan niba sunana jennifer ba sunana jannat kada ki kara kira na da wannan sunan rufemin baki kona wanka miki mari jidda ta katseta,ba'a canxawa tuwo suna agurina har gobe sunanki Jennifer dashi zan kiraki, jannat ta galla mata harara ba mmk dan daga ganinki baki san ciwon jikinki ba idan kin saba hada jiki da ballagaxaxxu irinki nidai ba ballagaza bace kije kiyi da wanda kika sabayi dasu ta wuce afusace jidda ta kuma janyo hijab dinta, ki kare min kallo kinga nayi kala da ballagaza ?? wannan kuma ke xaki ba kanki amsa dan baki isa na kalleki ba, sakin hijab dinta tayi wllh baxan iya kishi da yarinya karama irinki ba akan ya khaleel babu abinda baxan iya ba banza yar tsintuwa mara asali, har jannat ta juya xata tafi ta dawo baya, meyasa kika bari mara asali ta rabaki da wanda kikeso ? alhmdllh ina gdw Allah da yayine a haka bani da asali amma ina tsoranshi kuma ina alfahari da jarabawarsa agareni dan nasan mumini na kwarai ake jarabta keda kike yar asali ni da bnda asali bamu da banbanci tunda dukkaninmu yan adam ne kuma mata, ta wuce ta barta

anan tana mmkin ta batayi tunanin tana da baki haka ba da gudu ta karasa daki wajan ummanta tana xuwa ta fada jikinta ummana zan iya mutuwa,bakin ciki xai kasheni umma tunkina da ranki bakin ciki xai halakani araxane umma take jijjigata me ya faru jidda ? menene ? sai da ta gama kukanta hnklin umma atashe ta rarrasheta ta kwashe karya da gasky ta fadawa umman, ran umma ya baci sosai kwantar da hnklinki y'ata khaleel xai xama naki ki juyashi son ranki na miki alkawarin sai yadda kikayi dashi

by

*Ummee Garkuwa*

[2/28, 6:43 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

65&66

Ngd ummana ina son ya khaleel yaji ni kad'ai yakeso arnsa bana son kishiya ummana araba auren khaleel da Jennifer,

Share mata hawaye ummanta tayi cikin kwarin gwiwa kada ki damu da wannan jidda ni kaina ban xauna da kishiya ba balle ke guda daya tal koxan tafi tsirara sai na cika miki burinki bani da farin cikin da ya wuce naki ki kwantar da hnklinki zanje wajan malamina na nan kano ya iya aiki kamar yankan wuk'a duk xasu Sani dukansu dariya jidda tayi cike da farin ciki Dan tasan ummanta ta akwai bin yan tsibbu babu abinda baxata iya ba, idan xata sama mata farin ciki,

**********

Washegari da safe sulthana tana breakfast dinta ita kadai sbd bata tashi ta wuri ba tana cikin yi zahra taxo kanta tai k'erere tana mata kallon raini, Jennifer dama baki da kuny'a? Tunanin zahra ko jannat ce, tacigaba da cewa,

jiya Anty jidda ta fada min kin mata rashin kuny'a kina mata gadara da kina auren ya khaleel idan ma banda k'addara me ya khaleel xaiyi dake ? Mtswww banxaye marasa asali Anty jidda ba sa'arki bace sai dai ni kiyi dani banda ma jaraba da shishshigi ku xo gidan mutane Ku tare ba dangin iya ba na baba keda wasu banxayen yan uwan.......... Marin da sulthana ta wanka mata ne yasa ta yin shiru bata k'arasa ba dai dai lokacin da jidda da ummanta suka dawo daga unguwar da suka tafi tun duku dukun safiya, da sauri jidda sukayo wajan ita da ummanta, umma tai wa sultana wani katon xagi, Dan ubanki me ya Sa kika mareta shegiya dangin dangi ro kixo gidan mutane kina cin arxikinsu har ki daga hannu ki mareta ? Ke y'ar gidan uban waye ? Koda yake ke kanki ba kisan kanki ba balleki San ubanki,

wani mugun kallo sulthana tai mata, ke kika damu da wannan abinda nasani ke mutun ce ni ma mutunce kuma haihuwa ta akayi ba daga sama na fado ba rashin kunya tai min shiyasa na zabga mata mari saura waccen muciya da xanin, ta nuna jidda, sakin baki sukayi cike da mugun mmk, umma tace kan bala'i daga cin arxiki kixo gidansu kina cin arxikinsu kike wannan zak'ewar?

Rik'e k'ugu tayi su arxik'in ubanwa suke ci ?

Ke ina mgn kina mayar min ni sa'arkice
Fari tayi da ido kema ba girmama na sama dake kike ba, ta murgud'a baki, jidda cikin tsawa tace, ke Dan ubanki ummana kike fadawa wannan mgnr, kallon banxa sulthana tai mata ita ummantaki meyasa ta fada min mgn ?
Dalla rufemin baki kixo gidan ubanmu kike k'ok'arin takamu to ba ki isa ba,
A wulakance sulthana ta ya mutsa fuska ubanki ko uban wasu ? Me ya hana ki xauna gidan uvanki kiyi gadara dashi nan gidan uban wasu ne ba naki ubanwa,
Umma ta kwatsa mata tsawa wannan yarinyar baki da tarbiyya,
A ya tsine tace ga Mara tarbiyya cen kin Haifa data kebin saurayi daki tana shishshige masa yana wulak'anta ta,
Hannu umma tasa akai lallai bashir ka kwasowa kanka masifa,
Kiga masifa akanki shi da ganin masifa har abada
Baxata sab'uba dole yaya bashir ya kori yaran nan tunda basa girmama manya
Kema ba girmama su kike ba kuma xama gidan dady daram ba shegiyar da ta isa ta koremu,
Salati umma tasaki
Da karfi xuciyar ta kamar ta fashe Dan takaici batayi tunanin cin mutuncin daga gun yaran ba,
Daga kaina kin daina nuna mutane da yatsa xaki gane kuranki sai nayi kaca kaca dake,
Oho wannan kuma ke kika yadda dashi avinda na yadda dashi Allah shine mai komai ba bawansa ba,

Momy da dady suka sauko daga sama cikin tashin hnkl umma tana ta zage xage jidda tana rik'e da hannun zahra tana xubar da hawaye Dan marin ya shigeta, hindu ta sauko jannat na tsaye akan upstairs tana kallon rigimar
Hindu Hannun sulthana ta rik'o tana ja dady yace
Subhanallah sulthana me ya faru ?
A kufule tace dady Dan kawai bamu san iyayen mu ba sai a tsanemu ? Waccen banxan zahran tunda mukaxo gidan nan take mana kallon raini shine yanxu take xagin Anty jannat wai Mara asali shegiya wllh dady banda sulthana y'arka ce kaida Momy dana koya mata hnkl, girgixa kai dady yayi to shikenan muje sama ya sata agaba had'e da galla wa zahra harara, sakin baki umma tayi cikin d'aga murya tace yaya bashir ina son mgn dakai bai waiwayo ba yace anjima xamuyi mgnr yanxu zan rarrashi sulthana, salati umma ta saka
Momy ma hararar zahra tayi had'e da k'wafa tai sama
Nashiga uku ni hadiza xama tayi akan kujerar dining had'e da cire d'an kwalinta cikin tashin hnkl tabbi jam ! Wannan masifar har ina ga y'arka data sha mari katafi lallashin wata cen futsararriya, way'an nan yara basu bar yaya bashir haka ba dole akwai k'ullalliya, xonan zahra kiyi hkr na fuskanci yanxu dadynku ta way'ancen shegun y'ay'an yake kaf sun juyar masa da hnkl wllh munsa k'afar wando d'aya dasu baxan bar gidannan ba har sai na karya wannan asirin ina xama bai kamani ba,

Daki suka shiga dukansu, jannat tace sulthana meya Sa kika mari zahra ? Haba sulthana ana barin halak dan kunya kada ki manta tarin alkairan iyayenta akanmu,
Tsaki sulthana tayi Anty jannat baxan iya jure cin mutunci ba kawai ina xauna ina breakfast ta

hau xaginki tunaninta ko kece dama haka suke miki wannan cin mutuncin ?
To idanke kin jure kin San ni ba xan iya jurewa ba,
Hindu tace abinda yafi damuna sulthana ki xage kina fada da babbar mace bafa sa'arki bace ki k'yaleta ko Dan girmanta,
Baxan iya bane kun San halina kun San yanda nake idan ina cikin wannan halin bana iya tantance babba da k'arami hkr ne kawai banda shi amma bana Neman rigima muddin kuwa ka tab'ani sai kayi Dana sani, jannat tace Allah ya kyauta suka amsa da amin

***********

Da yamma suna xaune a falo dukansu bayan sungama dinner umma cikin ya tsina tace Ibrahim, yad'ago kai ya kalleta, meya had'aka da y'ar'uwarka ? Kana son nuna banbanci tsakaninta da Jennifer ? Kasani fa xaka iya rabuwa da Jennifer jidda kuwa har abada yar'uwarka ce, katseta yayi,
umma plx kidaina min fad'a agaban yara ? Ya kallesu fuskar shi a d'aure Ku tashi kuba mutane waje, kowacce tashi tayi tabar wajan,
Ya dawo da kansa wajan umma, ta cigaba da fad'anta haba Ibrahim kafin kasamu Jennifer wa ka fara samu kashe wayarshi yayi daya ke dannata, umma ya kira sunanta, jannah matata ce jidda kuma k'anwatace baxaiyi yu nak'i kowaccensu ba sbd d'aya sannan abaya na fad'a miki kuma kin Sani yanxu ba Jennifer bace sunan Momy gareta ta musuluntа, ya mik'e tsaye ni bana son mgn akan abu d'aya me jiddan tace na mata ? Ko ma menene bai kamata kina min fad'a agabansu ba ya fice ta bishi da kallo cike da mmki, innalillahi wa inna ilaihi raji'un ta kalli momy, Firdausi ki biya malaminki, momy murmushi tayi ta mik'e ta bar mata falon gaba daya hnklinta yai mummunan b'aci kai ta dafe dole tai musu gagarimin aiki Dan idan tayi sake wataran khaleel xai iya mata cin mutuncin da batayi tsammani ba

2days ago

***********

Da rana sulthana tana gardin dayake bayan babban kitchen tana xaune tana tuna rayuwar ta mai dad'i wanda ayanxu komai ya cab'e ta koma kamar ba ita ba tagumi tayi, duk irin gatan da umminta ta nuna mata ba ita ta haifeta ba hawaye ya sauko mata ta samu gata duk da kasancewar ta cikakkiyar Mara kunya umminta bata taba nuna mata wata alama ba, motsi taji a kitchen ta tashi ta lek'a ta jikin k'ofar baya ta hango jidda ta d'auko flast din abinci ta xuba sulthana na hangenta ta jikin wata Yar mitsitsiyar k'ofa da akayita dan lek'e, gani tayi ta fito da leda a hannunta ta xaxxge magani akan abincin, xaro ido sulthana tayi tana mmk ta rufe flast din ta bude loka ta ajjiye ta fito daga kitchen din tai b'angarenta da sauri sulthana tabi bayanta da niyyar ta nuna mata ta ga abinda tayi kafin ta k'arasa ta shige d'aki ta fad'a toilet
Cije yatsa sulthana tayi, dabara ta xo mata da sauri ta koma ta juye abincin acikin wani plate na daban ta ta wanke flast din ta xuba wani abinci ta mayar lokar da ta ajjiye ta fito tana mmk jikinta har rawa yake direct dakin momy ta wuce ta sameta xaune tana laxumi kusa da ita taje ta xauna tayi ta gumi,
Momy ta kalleta cike da kulawa, sulthana meyasa meki? Hawaye ya sauko mata, cikin kuka tace momy halin da muke ciki na masifa ma ya ishemu way'an cen mutane suna k'okarin kara

jefamu cikin wata sabuwar masifar,

Atsorace momy tace wacce masifa sulthana ta share hawayenta ta kwashe abinda taga jidda tayi da yanda ta sauya abincin, tagumi momy tayi jikinta asanyaye,

Momy irin wad'an nan abubuwan sai dai nagani a novel ko a film yau na gani da idona, ina tsoran kada wani abu ya samu Anty jannat ita da ya khaleel kiyi wani abu momy,

Kwantar da hnklinki sulthana Allah ya fisu babu abinda xai faru bi'ixnillah zan kuma d'au gagarumin mataki abinda nakeso dake kada kifad'awa kowa sbd xaki d'aga musu hnkl zan Sa musu ido sosai daga ita har mahaifiyar tata kedai abinda nakeso dake ki cigaba da shan maganinki akan kari ki dage da addu'a kinji ko ? Ta mik'e naji Momyna inshaa Allah xan kiyaye asanyaye ta fice tana mmkin abinda ta gani ita kanta xata sawa jidda ido sosai tunda ta fuskanci inda suka sa gaba

**********

da safe bayan sungama breakfast jidda ta kalli momy,
mom banga ya khaleel yaxo yin breakfast dinshi ba,

da sauri momy tace eh jannat tashi ki kaiwa yayanki breakfast, had'a rai tayi dan ba haka taso ba ranta ya b'aci ta mike tai b'angaren d'akinta sulthana ta bita da kallo tana murmushin k'eta

a kunyace jannat ta shi ta d'auka tai b'angarensa sallama tai masa ya amsa hannunshi rik'e da laptop yana amfani da ita tana shigowa ta b'ata rai ta turo baki ita a dole fishi take dashi,

yaji dadin ganinta bata ran datayi yasashi murmushi ya xuba mata ido kusa dashi ta ajjiye flst din ta gaishe shi ya amsa yana murmushi ta cire hijab dinta ta xuba masa tea a cup ta mik'a masa ya amsa ta hada masa komai ta mike xata ta fi
" ina xaki tafi ?
bata waiwayo ba tace zan koma cikin gida ajjiye cup dinshi yayi ya janyo hannunta ya xaunar da ita,tana ta fusge fusge dariya ta bashi ya tallo bo fuskarta, fushin me kikeyi ?

ta juya ido ni ba fushi nakeyi ba,
haka kawai yaji yana son tsokanarta dan kawai tai masa yarinta any'a kuwa wannan jannat ce ? ya k'ura mata ido cikin wasa kodai sulthana ce ?
jannat din dana sani bata da tsiwa matsoraciya ce bata iya fada ba,

kallonshi tayi da sauri niba matsoraciya bace ta fada tana murguda baki, yayi murmushi me fidda sauti yana shan tea din ya ce idan jannat ce me ya sameki kwana biyu ?

ta kalli cup din hannunshi ta kara hada rai ni babu abinda ya sameni
hada ranshi yayi ya kalleta , ki fadamin meya ke damunki ?
kwana biyun nan narasa gane damuwarki, tun ranar da nai miki mgn akan ki fadi abinda kikeso ki huta da boye boye shine kike fushi,

ranta ya baci bata son wannan magnr ko kadan,

xuba mata ido yayi yana kallonta, ta dago kai ta kalleshi, kana son jin wanda nakeso ?
ajjiye cup din daya ke shan tea yayi yana gyada kai akufule tace,wanda nakeso ba shi na aura ba

kallonta yayi da mmk ta marairaice, ban aure shi ba kuma ina sonshi sosai,
kishi mai xafin gsk ya taso masa ya fincikota agabana kike fadamin kina son wani ?

xaro ido tayi tana kokarin kwace kanta,

tambayata kayi na baka amsa plx ka cikani sakin ta yayi, yana jin ba dadi aransa ta mike xata fice ya kuma fincikota, ya xare mata ido,kikace kina sonshi sosai ? kai ta daga masa atsorace matseta yayi da jikinshi har sai da tayi kara ? dolene ki cireshi aranki baxaiyiyu ina aurenki kina son wani ba, ya saketa ta fice da sauri,
sai bayan ta fita yake jin haushin abinda yai mata kamar wani karamin yaro yake mata fadan ta cire wani aranta, tsaki yai shi sam bai son yayi hakan ba sbd kishin daya ta so masa, anya kuwa da gaske take masa ? idan kuwa har haka dinne xai san matakin da xau dauka dan yana matukar sonta yna kishinta

tana fita daga dakinshi ta waiwayo tana kallon kofar murmushi tayi ya khaleel kenan abinda kakeson ji baxaka ka taba jinshi ba idan har bakai kafara fada ba ta wuce tana jin dadin yanda lokaci daya tai nasarar cire masa wancen tunanin ta hau sama tai alwala tayi sallar walaha ta dade tana addu'a akan Allah ya kawo musu mafita na halin da suke ciki

************

da daddre momy ta fito daga dakinta xataje dakin dady giftawar mutun ta hango a k'asa taji tsoro ta dake da kyar ta lek'a abinda ta gani ya bata mmk ta kalli agogo 11:38pm da sauri ta shiga dakin dady tace ya xo yaga wani abu ya biyo bayanta suka sauko kasa da mmk yake kallon umman jidda magani ne a hannunta tana barbade falon dashi tsawa ya kwatsa mata ranshi ab'ace hadiza !! menene haka kikeyi ??

by
*Ummee Garkuwa*
[2/28, 6:43 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

67&68

a raxane ta dago kai ta kalleshi yana sauka daga stairs momy na biye da bayansa, menene haka hadiza ?
cikin yadda da abinda xata ce masa ta kalleshi ta marairaice yaya bashir akwai matsala,daxu naje wajan malamina yake fadamin yaran nan ba banxa suka barka ba sun maka asiri sosai kuma yayi tasiri ajikinka,ya fadamin ma xamansu cikin gidan nan babu alkairi ka koresu wannan maganin danake barbadawa shine makarin asirin da suka maka dan yace gidan nan xagaye yake da layun da sukai maka binne, kallon takaici yake mata kamar ya rufeta da duka yace, meyake damunki hadiza ? meyasa kika bata kanki da wannan banxar rayuwar ? wannan wacce gurbatacciyar rayuwa ce kika dora kanki akai ? wanne irin asiri kuma ? yaran nan nina janyo su jikina basu suka kawomin kansu ba, ki dinka abu da tunanin me jibi xata haifar, kina da yaya

xaki samu jikoki idan suka fada irin wannan rayuwar xakiso su hadu da hannu nagari shi alheri dankone mai shi yake bibiya,
da mmk take kallonsa, yaya bashir ka yadda da abinda nake fada maka kasan baxan cutar da kaiba ba xanso wani ya cuceka ba, tsawa ya kwatsa mata haushinta ya kamashi cike da kuluwa yake girgixa kai dan mmkinta yagama kureshi, bansan a inda kika samu wannan tarbiyyar ba dan iyayenmu ba irinta suka dora ki akaiba, wannan yaxama shine last kada kikuma shigomin da irin wannan karerakin ni ba mutumin banxa bane nasan me nakeyi kije ki tubarwa Allah muddin kina son xaman lafiya ki kiyaye, bana son karajin wayannan xantukan na karyar banxa da wofi, ya kalli momy ki fdawa yaran nan su wanke wajan nan gaba daya, ya hau sama momy ta tsaya kan stairs din tana neman nimbers din ma'aikatan gidan, ran umma abace tacewa momy idan kin hanashi karya tsubbinki anan baki isa ki hana wanda xanyi a bayan idonki ba ta gallawa momy harara tai bangarenta momy takira yaran cikin daren suka wanke falon

***********

washegari da safe momy xama tayi a kitcean tana kallon jidda da ummanta suna ta xirga xirga taki barin kitcean din har sai su suwaiba suka gama hada musu breakfast aka jeresu a dining suka hadu nan kowa ya karya banda khaleel dan tun xuwansu jidda bai fiya xama aci abinci da shi ba, bayan sungama tacewa jannat ta dauki nashi ta kai mishi tana kallon irin kallon takaicin da umma da jidda suke yiwa jannat a kunyace ta ratsa ta gabansu ta dauka tai bangarensa sallama tai masa ya amsa ya fito daga wanka jikinshi daure da farin towel dan karamin a hannunsa yana goge ruwan kanshi dashi, kallo daya tai masa ta kauda kanta ta ajjiye kayan ya karaso kusa da ita ya xauna ta gaishe shi ba tare da ta kalli inda yake ba ya amsa yana kallonta ta mike xata fita ya dakatar da ita,
"ina xaki tafi baki xuba min ba,
ta kalleshi kunya ta kamata sbd ba riga jikinshi ta sunkuyar da kai naga baka shirya ba, dawo ki xauna xanje na shirya tunda naga kina jin kunyar kallona, ya tashi ya shiga bed room dinshi tayi ajiyar xuciya ta cire hijab din ta xuba masa tea a cup da soyayyan dankali ta hada masa da plantains ya shigo falon nasa ya saka wando 3 quarter da riga me gajeran hannu ya xauna ta miko masa cup din ya amsa dayan hannun nashi rike da remote xai kunna tv shiru sukayi dukansu suna sauraron labaran bbc a hankali ta mike xata fita ya riko hannunta ta fixge hannun ya kalleta yaga ta hada rai,
"fushin me kikeyi ?
ni ba fushi nakeba,
kallonta ya cigaba dayi ta juya ta fice daga dakin ya jinginar da kansa jikin kujera yana jin kansa wani iri,

falo ta koma ta tarar da sulthana kwance kan kujera umma da jidda na gefe dukansu harar junansu suke tana shiga suka bita da mugun kallo,
ganin yadda sukeyi yasa tace, sulthana tashi mu tafi daki akwai aikin da xaki tayani ta mike tayi tsaki muje anty jannat mubar marasa aikinyi,
suna shiga daki jannat ta rufeta da fada,

sulthana meyake damunki ? kiyi hkr ki sharesu mana anty jannat nifa idan baxasu dainaba nimafa baxan fasa ba ki kyalesu zanyi magaminsu kima daina wahalar da kanki dan baxan daina ba tagumi jannat tayi tana kallon sulthanan dan da gaske takeyi,hmm Allah ya kyauta, murguda baki sulthana tayi hade da cewa amin

***********

da rana ma momy tattaro su jannat tayi da sulthana suka shiga kitcean suna aiki tare da ma'aikatan momy tana xaune a kitcean din ana ko mai akan idonta jidda tashigo ganinsu duka yasa tayi sororo jikinta asanyaye tace momy kina nan na duba cikin gidan ban ganki ba murmushi momy tayi tace eh jidda muna nan ana aikin tare damu, gyada kai jiddan tayi hnklinta atashe ta juya tabar kitcean din murmushi momy ta kumayi dan tasan akwai abinda ya kawo ta ganin su yasa jikinta yin sanyi, kiran sallar da akayine yasa momy ta dakatar da su akan suje suyi sallah jannat kawai suka bari sbd tana fashin sallah kafin momy ta tafi sai da tace kada ta kuskura tabar kitcean d'in,suna fita ta hau tattara kayan ta suka b'ata xata gyara wajan rungumo bayanta taji anyi a tsorace ta waiwayo tana kokarin yin ihu rufe mata baki yayi yana murmushi, fusge jikinta tayi ya k'ara janyota jikinshi ya rungumeta k'am a hankali ya furta I extremely love u jannat i love u too ina sonki ina sonki sosai, tun ranar dana fara ganinki nasan kece uwar yayana tundaga lokacin nake dawainiya da soyayyarki, ina son na rayu dake,

mmk tayi dan jin xancen nashi tayi kamar saukar aradu ta lumshe ido tana jin dad'in mgnr daya mata xamota yayi daga jikinsa ya kura mata ido cikin matuk'ar jin kunya ta sunkuyar da kanta ya sa hannunshi biyu ya tallabo fuskar ta runtse idonta, cikin wata iriyar murya taji yace,

plx jannat bude idonki kiga soyayyarki cikin kwayar idona, ki kalleni ki tabbar da baxan iya rayuwa babu ke ba plx jannat, maganganunshi sun kashe mata jiki ta bude idonta da kyar ta kalleshi ta xame jikinta ta juya xata bar kitcean din ya riko hannunta a rikice,

ta waiwayo a hnkl tace masa ngd da soyayyarka ta xare hannunta ta fice,

xaro ido yayi yana mmkin amsar ta baiyi tunanin irinta xata bashi ba ya runtse ido yanajin wani iri aransa oh ya rabbi ! jannat me kike nufi da kin gode da soyayyat kina nufin bakya sona ?? kada kiyi min haka meyasa kika xama ta musamman awajena hangota yayi nesa da kitcean d'in atsaye ita da suwaiba da sa'a suna hira tana murmushi alamun ba abinda ke damunta dafe kai yayi yarasa gane inda yarinyar nan ta dosa ya wuce dakinsa yana shiga sageer ya shigo hannu ya bashi suka gaisa cikin farin ciki sageer yana dariya yace ya dai khaleel naganka arikice gashi fad'a naxo muyi kallon sageer ya yi, sageer din shima kallonsa yake jidda ta kawo min kararka,

had'e rai khaleel yayi yaja tsaki ya kwantar da kanshi jikin kujera, cikin fad'a yace meya ke damun jidda ne ?

sageer yace dole ta damu tunda kasan tana sonka bai kamata dan kayi aure ka juya mata baya ba, akufule khaleel yace,

me take so na mata ? tana so na wulakanta matata sbd ita ? na fuskanci abinda take so kai ka sani sageer ni ba sakaran namiji bane, idan xata iya hkr tayi idan baxata iya ba babu dole ta kyaleni na huta nagaji da korafi ya k'arashe maganar da tsaki,

dariya sageer yayi ka dai kara yin tunani jidda yar'uwarka ce bai kamata.....ya isa sageer bana son wannan maganr,

da xoyala sageer yace kafi son mgnr jannat ko ? kallon sageer d'in yayi bai tanka masa ba,

na manta fa kai angone yayi dariya sosai tun kafin aje ko ina sun fara rikita,
ka na ganka so cool me ya faru ??
kamar baxaiyi mgn ba sai kuma ya girgixa kai sageer jannat daban take,
ban gane ba khaleel,
yarinya ce amma tasan kanta tana ja min aji sosai,
murmushi sageer yayi da tsokana yace amma dai ta fad'a maka tana sonka ko ?
zaro ido yayi na fda maka jannat daban take, yanxu kam darajar ta ta karo a idona soyayyar ta kullum karuwa take sbd halayenta tana da aji da biyayya,
yayi shiru bai k'arasa ba,
tashi sageer yayi ya bud'e frige ya dauko coke ya bude yana sha,
na fad'a maka yaran yanxu bana wasa bane, na jinjinawa jannat da ta haukatar min da aminina ya shek'e da dariya, ka cigaba da lallabata, kasan mata yan rarrashine,
kallonshi yayi yai murmushi  ya canza musu wata hirar

**********

misalin k'arfe hudu ya shigo falon ya tadda su gaba d'aya ya xauna kusa da momy ya gaishe ta idon shi akan jannat data k'urawa tv ido,
jannat ! ya kira sunanta gaba d'aya suka kalleshi,
" kije ki shirya xaki rakani unguwa,
ya mike ina jiranki in kin gama, ya fice daga falon kunya ce ta kamata ta nok'e tak'i tashi sai da momy taga da gaske takeyi ta kalleta cikin kulawa,
jannat tashi kishirya mana, da kyar ta iya mik'ewa cike da jin kunya ta hau sama k'arar test taji tana dubawa taga sakonshi........ ki shirya ina jiranki kisaka hijab da nik'af...... ya mutsa fuska tayi kayan daxan sa ma sai an xab'amin ta shirya less tasaka  green collour da kwanliyar amy ajikinsa tasa hijab amy ta kalmi amy ta d'auki hand bag dinta green ta d'ora nkaf ta fito dukansu suna falo a kunyace taiwa momy sallama muryar sulthana taji tana cewa asiyo mana alewa me tsinke, dukansu sukai dariya har da momy da sauri ta fita itama tana dariyar ta hangoshi jingine jikin motor dinshi yasa shadda  milk hular kalan xaren da aka yiwa shaddan aiki tayi masa kyau sosai ta k'araso ya bude mata kofa ta shiga ya xagayo ya shiga mota ya tada ita danjuma ya bud'e musu get ya fice daga gidan

*************

tun da suka tafi babu wanda yai magana wa'axi ya kunna na sheik ja'afar akan ma'aurata shiru sukayi suna jin wa'axin jikinta yai sanyi ta lumshe ido tana jin dad'in sauraran waaxin wata unguwa suka shiga babu mutane a unguwar dai dai k'ofar wani babban gida yai hon me gadi ya bud'e ya shiga cikin gidan,
gabanta ya fadi ganin wasu motocin na daban yasa ta sakin jikinta ya fito daga motar ya xagayo ya bude mata ta fito ya shiga gaba tabi bayansa jikinta asanyaye dan btasan inda take ba sallama yayi aka amsa masa ya shiga falon gidan wani farin mutun ya taso da sauri ganinta da shi yasa ya xaro ido lalala ! khaleel kaine da amarya ? yau ka cika alkawari sannunku da xuwa amarya shigo a d'arare ta xauna khaleel din ya xauna kusa da ita ya shiga cikin gidan bai jima ba suka fito shida matarshi  da sauri ta k'araso inda suke oyoyo oyoyo jannat ! yau kam ranar ta muce ankawo mana amarya xama tayi suka gaisa ta mike tace xo mu shiga ciki kawata, ta mike

tabi bayanta suka shiga d'aki ta xauna ta debo mata kayan motsa baki tana mata hira sosai sai bayan ta xauna tace amarya cire nikaf din na ganki sbd in mun hadu gaba na ganeki, ta xame nikaf din suka had'a ido tayi murmushi so young mashaa Allah anata samin rana xa a kawo ki yau dai gashi an kawo min ke, sunana kausar matar abokin mijinki murmushi jannat tayi,
haka kausar tai ta janta da hira, dan tasaki jiki, ta fuskanceta tana da son mutane da kuma kirki mijinta ne ya shigo cikin fara'a yace amarya mijinki yana jira xaku tafi khausar tace kai ! daga xuwansu d'age hannu yayi ba ruwana mijinta ne yace taxo ta mike, tana mitar kamata yayi a barta sai dare, tace wa mijin nata yatafi yanxu xasu fito leda ta dauko jannat ta mike tabi khausar ta riko hannunta suka fito falon cikin wasa tace, khaleel gaskiya wannan xuwan ba a dad'e ba ka kawomin ita ta yini,
murmushi yayi ya mik'e sukai sallama tabawa khaleel ledar tace ya bata yai gdy suka fice ya bud'e mata kofar motor ta shiga shima ya shiga ya tada ita suka fice daga gidan
kai tsaye store ya kaita yace ta fito ta taxab'i abinda take so,
ta fito daga moto ta bi bayansa suka shige store din ya kaita b'angaren kayan kwalliya kasa tab'a komai tai, ganin xata b'ata musu lokaci yasa ya d'auki box yana loda kayan da duk yaci karo da su, bayan yagama lodan kayan masu yawa ya yaje wajan biyan kudin akai masa total ya biya suka fito daga store din da kayan lodi lodi a hannunsa ya bud'e mata mota ta shiga shima ya shiga suka fice sunxo dai dai danja aka tsayar dasu sbd jiniyar da masu bada hannu sukaji suka bawa bangaren hanno suka danno kai farko motar sojojine bayansu yan sanda sai wasu dank'ara dank'aren motoci jannat tabi motar da kallo ta tsakiya tana tafiya a hnkl ita kadaice glass dinta ba tintac ba, had'a ido sukayi da ta cikin motar gabanta yai mummunan fad'uwa ta tsirawa matar ido ji tayi kamar ta santa kuma tai mata kama da wata amma batasan wacece ba tsurawa matar ido tayi babbar macece, karaf matar ta waiwayo suka tsurawa junansu ido idanuwan jannat kadai ta kalla sbd nikaf din data sa, amma taga kamar matar ta rikice da ganinta wani abu jannat taji yana mata yawo ajikinta motar matar ta wuce, dukansu suna waiwayon juna, abinda jannat bata tab'a jiba taji yana tsirga mata jikinta lokaci d'aya taji tana son matar sosai jikinta na bata wani abu akan matar amma takasa tantancewa runtse ido tayi tana jin wani chock na musamman ajikinta hawaye ya sauko mata dai dai time din da motocin suka gama wucewa aka ba hanyar hannu ya khaleel ya tada moto din suka wuce da sauri basu dad'e ba suka shigo layinsu sai da suka shiga gida ya waiwayo yaga tana xubar da hawaye da sauri ya riko ta yana tmbyr ta shiru tayi dan tarasa me xata ce masa rungumota jikinsa yayi yana rarrashinta tayi lamo cikin kuka tace masa, iyayena ! runtse idonsa yayi cike da jin tausayinta, kamar ya xubar da hawaye shima yace, kiyi hkr babyna in shaa Allah xaki sansu ki cigaba da addu'a ta xamo daga jikinshi still hawayen bai bar xuba ba dan ita kad'ai tasan mai taji dataga matar gaba daya son ganin iyayenta take, shiga cikin gidan tayi yabi bayanta cikin tausayawa tana shiga falon ta tadda su, ganin hawaye na xubar mata yasa momy da dady suke rige rigen tmbyr ta fadawa jikin momy tayi had'e da sakin kuka mai tsuma xuciya khaleel ya biyo bayanta ya xauna yana kallon kukanta mai k'ona masa rai sai da ta gama kukan sannan ta basu Ibrin matar da ta gani,

tundaga ganin matar tajita cikin sabon yanayi da sauri hindu ta matso kusa da jannat, tasa kuka ta rungumeta tana kukan tace watakil mahaifiyar mu ce jin haka yasa sulthana fashewa da kuka itama ta xamo daga kujerar data ke tana kuka sosai

By
*Ummee Garkuwa*
[2/28, 6:43 PM] Nana Zee: ✍✍✍JENNIFER✍✍✍

69&70

Kuka sosai sukeyi cikin wani axababben yanayi da suka dai sukasan yadda sukejin shi, shiru kowa yayi sbd mutuwar da jikinsu yayi dakuma tausayin su daya kamasu, share hawayen ta jannat tayi muryar ta na rawa take mgn tamkar xata kara fashewa da kuka, baxan iya fasalta me nakeji ba amma ta yaya mutun xai rayu da farin ciki ko annushuwa bai San kansa ba ? Bai San suwaye suka kawo shi duniya ba bai San wanne laifi yayi aka watsashi cikin duniya aka jefar dashi tun yana kwana arba'in? Kuka ya kufcemata takasa k'arasa mgnr,
